Granny cikin jin dad'i da murnan ibtisam ta yarda zatai aure tace karki damu, gobe ni dake zamu habuja din inga audullahi muyi magana.

Koda ummi ta dawo ta kira ibtisam, Bayan ibtisam tazo, ummi tace Waye yazo nemanki?

Ibtisam tace ummi shine wanda ya rage mana hanya shekaran jiya, nan taba ummi labarin

yanda suka had'u.

Ummi tace naga kaman ya baki, Leda, ban San amshe amshen kayan samari, Indai kin San ba auranshi zakiyi ba gwara ki sallameshi, ban son fitina

A hankali tace toh ummi, tare da tashi ta fita

Washe gari da safe ibtisam ta shirya ita da granny Wanda Abba bai San da tafiyar Granny ba, sai ganinta yayi da safe ita da ibtisam, yace mama zaki rakata garage ne?

Tace miye kuma wani garan?

Yace ina nufin tasha.

Tace wani rakiya? Tare da ita zamu, muje ka sauke mu tasha sai mu shiga mota

Yace mama tare kuma zaku?

Tace eh ko saina tambayi izini ne, Kafin a barni inje inda nake so?

Yace a'ah kiyi hakuri mama ba haka nake nufi ba, naga tun jiya baki ce zaki jeba sai yanzu.

D'aure fuska tayi tare da fad'in Ummaru zaka kaimu tasha ko mu tafi da kammu?

Yace a'ah muje in saukeku, ummi ta basu kayan miya sukai ma mum tare dasu gurasa da sauransu, sannan ta musu Allah kiyaye hanya suka fita.

Saida Abba ya biya ATM ya cira kud'i sannan sukai hanyar garage, inda ya d'aukan musu shatan mota su biyu, nan ya biya kud'in motan, sannan ya bama Granny kud'i itama ibtisam ya bata, saida suka wuce sannan ya shiga tashi motar ya wuce kasuwa.

Sai wajan 3 da wani abu suka isa Abuja, dai dai kofar gidan alh Abdullahi aka saukesu, inda suka nufi gate din gidan suka fara nocking, wani soja ne ya le'ko yana fad'in 'who is that? Ibtisam tace mune cikin harshen turanci take bashi amsa.

Granny tace Mai yace? Ibtisam tace tambaya yake su Waye?  Granny tace oh yanzu har sai an tambaya, kai dan ubanka zoka bud'e Uwar Mai gidan ce,

Dai dai lokacin sojan ya bud'e karamin kofar gate din, inda mutum zai shiga Inba da mota bane.

Kallonsu yayi sannan yace wa kuke nema?

Ibtisam ta bashi amsa da fad'in Munzo wajan matar gidan ne?

Yace tasan da zuwanku?

Ibtisam na k'okarin bashi amsa, Granny tace wai Mai yake cewa ne?

Nan ibtisam ta fad'a mata, Granny ta kalleshi cikin jin haushin tambayar da yake musu, tace Kai Dallah bamu waje mu shige tare da k'okarin tusa kanta cikin gidan.

Sojan yayi sauri ya tareta tare da magana cikin gurbattaciyar hausan shi yace mama inane zaka? Ka kira ajiya sai in Barka ka ciga, lokaci d'aya kuma ya kalli ibtisam yace ki kira madam a waya in tace in barku saiku shiga.

Granny kam in banda faman surfa bala'i tare da fad'in audullahi yasa Anci min zarafi yanzu in banda iskanci In za'a zo gidansa sai an kirasu a waya, har dani uwarsa.

Ibtisam dake k'okarin kiran mum tace Granny dan Allah kiyi shuru, shifa wannan bai San ke maman uncle bace, inda ya sani Aida ya Bari kin shiga, kuma daka gani sabon zuwa ne, dan duk zuwan da nake ban taba ganinshi ba.

Granny ta galla mata harara tare da fad'in Dallah ni kirata Ina jin fitsari kaman marata zata fashe

Kiran mum tayi, bayan mum ta d'auka tace ibtisam Kun zone, Ashe da Granny kuka tawo, yanzu na gama waya da abbanki.

Ibtisam tace Munzo muna Gate, ance mu kiraki.

Mi'ka ma Sojan wayarta tayi Mai tocilan, ya amsa tare da sakawa a kunne, naji yana fad'in ok ma, ok ma, lokaci d'aya kuma ya fara sorry ma, tare da kashe wayan ya mi'ka ma ibtisam, ya fara basu hakuri, cikin harshen turanci tare da cewa ibtisam taba granny hakuri bai San Maman oga bace.

Nan ibtisam ta fad'a ma Granny abunda yace, Granny ta kalleshi tare da fad'in Dallah bani waje, munafuki, da sauri ya matsa suka shiga, tun Kafin su k'arasa wata yarinya Doguwa chocolate colour kyakyawa ta rugo da gudu ta rungume ibtisam tare da fad'in oyoyo, lokaci d'aya kuma ta saki ibtisam ta rungume granny

Granny tace Dallah sakeni karki Karya ni, saida kika gama rungume y'ar uwarki sannan zaki zo kaina.

Ibtisam tace zarah Kinga kyaleta zomu shige

Granny tace zanyi maganinku Wlh, yara duk sun girma Sun Fara tsufa amma babu aure, ji yanda zarah ta k'ara fashewa, nidai Amina wani laifi na muku babu maganan aure a tsarinku,

kwafa tayi sannan ta shige ciki ta barsu nan tsaye suna murnan ganin juna, sun dad'e a nan Kafin suka shiga ciki inda suka tarar da mum a falo ita d'aya.

Ibtisam gaida mum tayi,  mum ta amsa cikin sakin fuska tare da fad'in ya hanya?

Ibtisam tace Alhmdlh, sai dai rigiman Granny, duk ta isheni dariya suka saka, mum kana kallonta Kaga balarabiya sak ita NAJEEB ya d'auko sai dai wasu sukan ce farinta ya d'auko yafi kama da dad d'inshi wasu suce da ita yake Kama, mum in kaji hausarta saika d'auka ba Hausa takeyi ba dan in tanayi kaman tana larabci

Granny ce ta fito cikin tan'kamemen falon Tana gyara zani tare da fad'in ku komai naku daban dana mutane, Kun tashi kun ajiye mara mutunci a bakin gate.

Zarah tace Kai granny maiya miki kuma?

Tace ban sani ba, in banda wulakanci in za'a shigo gidan sai ace sai an kira a waya, in mutum baida Kati fah, ko in bashi da wayan gaba d'aya fah?

Zarah tace saiya koma, Granny ko a addinance anaso in mutum zaizo wajanka ya Sanar dakai, bawai yazo kai tsaye ba K....

Granny tsaki taja tare da fad'in tunda bakwa son mutane ba, ai dole ki Kawo maganan addini..

Dariya suka saka, mum tace mama muje kuci abinci ku huta

Granny tashi tayi aka nufi k'aton dinning table, harta zauna, lokaci d'aya kuma ta tashi tare da fad'in nifa wannan abubuwan ban cika sonshi ba, in mutum zaici abinci saiya wani zauna a kujera kaman Maye, ni kusa min in zauna a k'asa Inci

Zarah da ibtisam babu abunda suke sai dariya

Granny tace uwarku kuke ma dariya, akan Mai yasa za'a ce cin abinci sai an hau saman kujera maima kuke kiran kujeran Denis ne ko Mai ohon muku

Zarah saboda dariya har dayin k'asa tace miye kuma Denis dan Allah granny kar kisa cikina ya fashe saboda dariya. Tsaki Granny taja tare da zama ta mi'ke k'afa a k'asa tana fad'in nidai ban hawa Denis din nan wlh

Mum da itama take ta dariya k'asa k'asa ta Fara zuba ma Granny abinci, Bayan ta gama ta ajiye mata a k'asa inda ta zauna, Granny Fara cin abinci akayi ana mamula baki.

Bayan sun kammala, Granny tace audullahi bai dawo bane har yanzu?

Mum tace tun dazu yace Sun sauka, Nasan yana gab da gida yanzu

Tashi Granny tayi, tace ni bari in shiga in huta kafafuwana duk sunyi tsami, d'aki ta nufa

Ibtisam taba mum tsaraban da Ummi ta bata, mum taji dad'i Sosai tana ta godiya, inda zarah taja ibtisam sukai d'akinta, wanda d'akin yayi mugun had'uwa, komai dake d'akin pink ne, sai rasi rasin blue kad'an, zama sukai akan gadon d'akin Mai shape din mota, zarah tace kin Fara shirin zuwan mu skul kuwa?

Ibtisam tace na Fara mana, sai dai Granny ta sani gaba da maganan aure, kai wannan tsohuwar akwai jaraba

Zarah tace Niko Tana sani dariya wlh, dama ta mana wata biyu a nan

Ibtisam tace Aiko ko sati tayi a nan sai kince ta isheki, ko sanda take zuwa kina skul in kin dawo kin gaji, yanzu da kike zaman Gida ai wlh saita isheki, dariya zarah tasa inda suka fara tsara yanda za suyi a skul, wayan zarah dake wajan wardrobe d'inta ne ya fara K'ara, tashi tayi da sauri ta d'auka, ganin Mai kiran yasa tayi saurin d'auka tare da fad'in bros

Yace yakike?  Cikin harshen turanci

Tace am fine my bros, sai dai nayi missing dinka

Murmushi yayi tare da fad'in gobe Zanzo Nigeria, make sure kisa a gyaramin part d'ina

Tace an gama bros, Granny tazo ma

Tsaki yaja tare da fad'in har yanzu bata mutu ba?

Zarah tace what?  Sai kuma ta fashe da dariya tare da fad'in Bari Dad ya jika, kana ma mum d'inshi fatan mutuwa.

Kashe wayan yayi ba tare daya kuma ce mata komai ba.

Kallon ibtisam tayi tare da fad'in bros gobe zai zo,, rabonshi da gida wajan wata hud'u kenan

Tabe baki ibtisam tayi tare da fad'in wannan ba damuwa ta bace.

Zarah dariya tayi tare da fad'in oh na manta Ashe enemy d'inki ne, sai kuma ta saki dariya tare da fad'in nima a waya yake sake min, inya dawo sai yayi ta d'aurewa kaman dodo, na rasa irin halinshi Wlh, zanso inga matarshi inya ya zai dinga mata.

Itbtisam tace lallai Aiko duk wacce ta auri wannan ta shiga uku, sunanta sorry, lokaci d'aya

kuma ta tuna da abunda ya kawo Granny, cikin ranta tace Allah ya tabbatar inga yanda zaiyi.

Zarah tace dama Ayi auran zumunci ke dashi, tunda naga halinku d'aya K....

Da sauri tace aniyarki ta biki, da in auri wannan yayan naki gwara in mutu Banyi aure ba, wannan wani banzan tunani nema kikayi haka, tsaki ta saki cikin bacin rai.

Zarah tace Allah ya huci zuciyarki, wasa nake miki,  ai nasan in aka had'aku wata rana k'ona gidan zakuyi

Itbtisam dake huci tace wannan Aiba wasa bane, in mala'iku suka amsa fah? Haba dan Allah, wlh gwara in mutu yau da ace na auri NAJEEB, dan Allah karki k'aramin wannan Wasan plz, wlh kinsa raina yayi mugun baci Sosai

Zarah tace ikon Allah, haka tsanan NAJEEB yayi girma cikin zuciyarki? Adai dinga hakuri d'an uwanki ne dai

Tsaki Itbtisam taja tare da tashi tana fad'in naga baki da wata firan arziki saina wannan yayan naki Kinga Bari inje wajan Granny n....

Da sauri zarah ta janyota Tana fad'in na daina miki firanshi, amma kudaina wannan abun babu kyau Wlh, duk da Nasan laifin bros NAJEEB ne, yana da shegen miskilanci da raini wlh, kodan ya girma mutane ne oho, wlh koni hakuri nake dashi, ga Dad komai yace saiya biye mishi tsaki taja

Itbtisam tace Kema kenan, balle ni ki....  Karan wayarta ne yasa bata k'arasa abunda tayi niya ba, d'auka tayi taga kabir ne wanda a jiya tayi saving number d'inshi, sawa tayi a kunne tare da fad'in hello

Ta gefenshi yace ibti Barka da yamma, sorry ban kiraki ba, aiki yamin yawa, yanzu nace gaskiya sai naji muryanki, ya kano?

Tace uhm lafiya kalau, nima bana Kano Ina Abuja

Da sauri yace yaushe kika zo Abuja?

Tace d'azu nazo nida Granny gidan uncle d'ina

Kabir yace shine baki fad'amin jiya ba, muzo tare

Tace naga hakan bai kamata ba, bai dace in bika ba har zuwa wani gari, hakan ba dai dai bane

Murmushi yayi tare da fad'in hakane, my ibti, tare da fad'in na gode ma Allah daya had'ani dake,

ina Mai farin ciki, Allah ya tabbatar yasa ki zama mallaki na

Murmushi kawai tayi ba tare da tace komai ba.

Yace anjima zan kiraki, ina fatan zaki bani dama inzo in ganki a nan?

Tace babu damuwa tare da fad'in sai anjima, ta kashe wayan.

Zarah dake zaune kusa da ita, tace ke dawa haka? Daka ji saurayinki ne yanda kike wani kashe murya

Ibtisam takai Mata duka tare da fad'in ta ina na kashe murya?kina da sharri Wlh

Zarah tace fad'amim Waye inji tare da d'aga mata gira

Nan ibtisam ta bata Labarin inda suka had'u

Zarah saida tayi dariya Sosai tare da fad'in Wlh Granny tana da matsala, Tab gaskiya ki daina fita da ita.

Uhm kawai ibtisam tace

zarah tace Amma inda nice ke Wlh zan yarda in aureshi, tunda muda zamu karatu kaduna, shi kuma yana Abuja, Kinga zaki samu daman karatu, yanzu fah maza tsada suke sai kiga mata da yawa babu mijin aure, wlh ibtisam inka samu dama Kar kayi wasa dashi, kyace ya jiraki shekara hud'u ai yayi yawa wlh, kina da tabbacin zai iya jiranki har shekara hud'u, haba ibtisam Wlh nima da badan Dad ba da yake son inyi karatu ba Aida aure zanyi Wlh, nifa aure nake so, Amma Dad ya'ki fahimta inaga saina fito na fad'a musu

Dukanta da wasa ibtisam tayi tare da fad'in amma dai da kin cika mara kunya number d'aya, Tabdi Niko Wlh karatu ne a gaba na, Kinga mazan yanzu basu da tabbas, wlh gwara koda zanyi auran saina gama karatu in samu aiki sannan inyi, dan ban son ina bin namiji Ina bani yana min wulakanci, gwara in tsaya da kafafuna, Suma yanzu mazan basu cika auran zauna gari banza ba, dan basa son wahala

Zarah tace uhm, ni Wlh aure nake so, ke nifa wannan karatun kaman dole ne, amma Wlh Ina bala'in son inyi aure, Kinga in Nayi sai inyi karatun a d'aki na, hankali kwance, amma hakan bazai yihu ba, Allah yaban iyaye duka y'an boko, ko wanne zai ka'ida, ba mum ba, ba Dad ba, yanzu koda wasa ban isa ince Ina son aure ba, wai dana shiga uku, ko bros NAJEEB baiyi ba shida yake aiki sai ni, Hmmm ta sauke ajiyan zuciya

Ibtisam tace zarah kin San muhimmancin ilimin mace kuwa? Inda za'a tambayeni tsakanin mace dana miji waya kamata a fi bama ilimi? Zance mace ya kamata, kin San mai yasa? Mace

itace tushen gida Mace itace take zama a gida ita da yara ta basu tarbiya tare da duk wata kulawa, in mace bata da ilimi taya za tayi hakan? Da yawa yaran da zaki gani suna rashin ji Toh uwarsu bata da ilimi, sannan yana dakyau mata a dinga basu ilimi domin ko ina a dinga damawa damu, ki kalla aikin soja akwai mata Kinga wannan abun alfahari ne, ki duba fannin Siyasa akwai mata wanda da ana ma mace y'ar Siyasa kallon y'ar iska, amma yanzu an fara fahimta, inda babu Mata a Siyasa da baza'a dinga bamu hakkin mu ba, bazan musan miye Siyasa ba, sannan mune dai mukaci jefa ruwan kuri'a, sannan yana dakyau mata su dinga karatu kodan su zama likitoci, yanzu Idan mace tazo haiyuwa namiji zai amshi haiyuwar tayu ba musulmi bane, Kinga inda mata suna karatu Sosai da an huta, komai mu ana tauye mu, daka munyi aure shikenan, in namiji yace ba zamuyi ba shikenan ta zauna, bayan ilimi shine ginshikin rayuwa, wlh zarah in Kinga yanda in naga mace take burgeni in naga tana karatu ko aiki sai Kinji mamaki, zan iya bama mace tallafin komai nake dashi dan tayi karatu domin Nasan al'umma zasu amfana da ita, yana dakyau komai a dinga saka mata, ana bamu y'ancin mu, Idan kika duba yanzu zamani ya canza duniya ta canza, ilimi both na addini dana zamani is like kaman ya zama dole mace tayi, indai Tana son ganin ci gaba da taimakon Al'umma.

Zarah tace bank'i taki ba,  shima auren yana da muhimmanci, sannan aure baya hana karatu, nidai Ina baki shawara a matsayina na y'ar uwarki, indai kabir dagaske yake kice Ya fito Wlh, Kinga kyaci gaba da karatun a d'akin ki, amma baki da wani hujja kice saboda karatu k'iki yin aure, Abba Nasan shi zai miki aure amma nikam Dad Nasan Wlh koda wasa saina gama wannan karatun zaimin aure, har shekara hud'u ta k'arasa maganan cikin tausayin kanta.

Muryan Granny sukaji Tana fad'in kuna inane haka?

Zarah tace Granny gamu a nan, Granny shigowa tayi ta saki baki Tana fad'in yanzu wannan kaman mota, motar nan taya akayi ta shigo wannan d'akin, naga dai kofar karama ce, ni ban taba ganin irin wannan motar ba Wlh, mota harda katifa, ya ake tukata?

Dariya suka saki su duka sannan zarah tace Granny gado nefa

Sakan baki tayi tana mamaki tare da fad'in yanzu bakya tsoran wannan abun, salan kina bacci ya fara tu'ka kanshi? Ina gadonki Nada?

Zarah tace Kai granny wannan fah ba mota bane, gado ne mai shape din mota, gadona Nada anbama Mai aiki takai gidanta da aka canza min wannan.

Sakan baki tayi tana mamaki tare da fad'in naji kince gado ne mai chape din mota, miye chape?

Dariya suka saki, itbisam tace haba Granny Tana nufin gado ne mai fasalin mota, yanzu kin gane?

Tace Hmmm wanna ai iskanci ne, in banda asaran dukiya, ace gado za'a saka a d'aki Mai fasalin mota da haka a siya motar mana a ajiye, yanzu wannan gadon nawa aka siya?

Zarah tace million biyu da rabi

Salati Granny ta saki tare da fad'in audullahi yana tunanin mutuwa kuwa? Yanzu gadon da zaki kwanta ki tashi shine har million biyu da rabi, oh ni Aminatu, wannan asaran dukiya haka Kai audullahi zai gamu dani, dama aure yayi miki keda wancan dan banzan, koda yake Bari in Gama da munafukin yayanki da wannan ta nuna ibtisam, sannan in dawo kanki, bari audullahi ya fito naji ance ya dawo yana hutawa

Zarah cikin jin dad'in maganan Granny tace Granny gobe ma zai zo gida NAJEEB din

Granny tace yauwa Alhmdlh Nima zani yola, dan Wlh wannan karan da Mata zai koma dan banza, sai na mishi iya shege, tunda bashi da niyan aure, inma aljana ce ta aureshi zata rabu dashi in na saka aka d'aura mai aure, zan zabo mata guda uku cikin dangi in tawo dasu ya zaba d'aya, inma duka yake so ya auresu dan banza kawai....... Muje zuwa muga had'uwan Granny da miskili, sannan muga ya zata kaya in aka zabo ma NAJEEB mata har uku kaman yanda Granny tace hhhhhh.

~MARYAM OBAM~

*NAJEEB*

*BY*
*MARYAM ALHASSAN DAN'IYA*
*(maryam obam)*

*https://www.facebook.com/Maryam-Obam-Novels-441847396162695/*

*http://WWW.Maryamobamnovels.com*

*Wattpad@ Maryam-obam*

*Instagram@maryam_obam*

*DEDICATED TO.....*

*MY BESTY OF LYF HABIBA BUZY🥰🥰 LOVE U WUJIGA WUJIGA💘💘*

*PAGE 6*

*wai Mai yasa wasu mutane basa tsoran Allah ne? Sai dai a baki kawai, nifa Maryam bacewa Nayi bana son kud'i ba, Yooo ni wacece da Zan'ki son kud'i ai kud'i Abun sone, but in mutum zai naima kud'i saiya nema ta guminsa, akan wani dalili zan zauna in bata lokaci na inyi typing in rubuta Basira na, bata wani ko wata ba, in siya data da kud'ina ba tare da nace wani ko wata ya siya min ba, sai na gama rubuta y'ar basiran da Allah yayi min sai wani ya d'auka ya dinga neman kud'i dashi, toh Wlh Wlh daka yanzu bazan k'ara d'auka ba, abun ya zama raini dacin fuska, da farko an d'auki novel d'ina har guda uku ansa a okada ba tare da neman izini naba, ansa BA'KIN ALJANI in zaka karanta saika biya 500, ansa FATIMA ZARAH, shi kuma in zaka karanta saika biya 200, ansa DUKIYAR MARAYA,  wanda barawon ya canza mishi suna izuwa dukiyar marayu, in Zaka karanta saika biya 300, akan wani dalili, ni Ina rubuta littafi a kyauta sannan wani yaje ya kaimun okada yana amsan kud'i da Littafina Wanda Nina rubuta bashi ba, nima fah ina son kud'in bawai banso ba, amma nayi a kyauta, akan wani dalili Kai ko ke zaku dinga siyar da novel din mutane without our permission, sannan Bayan haka wasu suna bud'e group akan in zasu tura maka novel complete saika biya kud'i, kuma Abun haushin basu suka rubuta novel d'inba, novel dinmu da muka rubuta suke saidawa, wasu ma saisu cire sunanmu akan novel din su saka nasu, Toh Wlh duk wani wanda ya k'aramin haka Wlh bazan d'auka ba, ba cika baki ba ko fariya Wlh akan hakkina Zan iya Shari'a da mutum, Abu d'aya shine in samu number d'in mutum, shikenan an wuce wajan,na fad'a zan k'ara fad'a maryam novel d'ina kyauta ne kar ku yarda ku biya kud'i domin a tura muku novel d'ina, ga sunan littafai na Zan fad'a, *FATIMA ZARAH*
*DUKIYAR MARAYA*
*BA'KIN ALJANI*
*BANDA ZABI*
*AMINIYA TACE*
*KISSA KO MAKIRCI*

 *SUHAILAT*
*TAMBARIN TALAKA*
*JAWAHEER*
*SAINA AURESHI*
*MIYE ILLAR Y'AY'A MATA*
*BARIKI NA FITO*
*SAI YANZU WANDA NAKE RUBUTAWA NAJEEB*
*Gaba d'aya kyauta ne karku yarda wani yace saikun biya kud'i ya tura muku, kuma inna k'ara Kama wani yana saida min da novel saina d'auki mataki*

Zarah tace Kai granny mata har uku? Sai kuma ta fashe da dariya tare da fad'in sunyi mishi yawa ai.

Granny tace rabu da dan banza, koya zabi d'aya koya auresu duka, dan wannan karan bazan mishi wasa ba, inda a kauye ne da yanzu an fara maganan zai aurar da y'a, amma wai sai yanzu zaiyi aure, wannan lalacewan har ina, wlh ni rayuwar Bariki batai min ba.

Ibtisam tace uhm toh saiki koma kauyen ai ki zauna, Muma sai mu huta

Granny taja tsaki tare da fad'in basai ki Mai dani ba, mutuniyar banza, fita tayi dan taji muryan d'an Nata yana waya, alaman ya fito

Alh Abdullahi yana ganin Granny ya kashe wayar yana gaidata cikin girmamawa tare dayi mata ya hanya.

Tace Alhmdlh Ai Kai zance ma ya hanya kaida ka dawo daka k'asa Mai tsarki.

Zama yayi suka fara fira da Uwar tashi, suna cikin firan mum tazo itama anayi da ita,  Alh Abdullahi yace Ina mamana ibtisam?

Mum tace suna ciki ita da zarah, bari in kirasu, tashi tayi ta nufi d'akin sai gasu tare sun dawo, ibtisam gaida uncle din Nata tayi cikin girmamawa, ya amsa tare da sakin fuska yace kin Kawo takardun naki koh, y'an makaranta.

Granny tayi caraf tace dakata ni dan Allah, wai ku Mai yasa bakwa maganan aure saina karatu? Kallesu yara duk sun girma suna shirin tsufa a gida, kwata kwata bakwa maganan aure, saina karatun banza da hofi, toh Wlh na gaji, bazaku sa a dingayi dani ba, ina tafiya ana nunani ba, nazo ne muyi magana akan yaran nan dan Wlh wannan karan rai zai baci in akak'i bin abunda nazo dashi, nazo ne akan maganan auran wannan dan banzan najibu naga ku kaman Abun bai dameku ba....

Dad yace mama Nima Ina bukatan NAJEEB yayi aure Sosai, amma har yanzu ya'ki magana, ko ince ya'ki fito da Mata .

Granny ta tsuke baki tare da fad'in sai ka tsaya jira saiya fito da Mata ai, naga alama Kai ke d'aure Mai gindi yake iskanci Wlh, amma zanyi maganin ka Wlh, gobe zani yola da safe zanje in tawo da  yara cikin dangi ya zaba wacce yake so, dan Wlh wannan karan dole yayi aure sai kuma ta fashe da kuka tana fad'in koso suke saina mutu banga y'ay'ansu ba, Nina tsufa yanzu banda wani buri face inga yaransu Kafin in mutu, amma naga kuke d'aure musu gindi, kuka take wi wi wi tana share majina da riganta

Alh Abdullahi cikin Tashin hankali yake bata hakuri tare da fad'in mama duk yanda kika ce hakan za'ayi ki zabo mishi wacce tayi miki sai a d'aura mishi insun fahimci juna

Suko su zarah da ibtisam dariya suke k'asa k'asa, suna kallon wannan jaraban ta Granny, tsohuwa sai iya jaraba

Granny tace a'ah Zan Kawo su da yawa, inya zaba sai in maida su, daka nan sai a d'aura aure, inda so samu ne da tare dashi zamu ma,amma Nasan bazai jeba, kuma ina son kona tafi kar wanda ya mishi maganan auran saina dawo.

Dad yace duk yanda kika ce mama hakan za muyi.

Tashi tayi tana fad'in nidai na fad'a maka, gobe karfe 6 Zan tafi saika tashi da wuri dan asan abun yi, bari inje in kwanta

Bayan Granny ta wuce suma su zarah suka wuce suna dariya, tare da fad'in Wlh Granny zata ballo ma NAJEEB aiki harda kuka, ita kam ibtisam dad'i take ji, don ta tsani NAJEEB gwara a mishi aure da y'ar kauye din zata fi kowa murna

Mum kam itama tana son dan nata yayi aure, sai dai bada irin matan da Granny tace zata bashi ba, tafi son a barshi ya kawo da kanshi akan a zaba mishi, tunda taga shi zai zauna dasu, amma zata zauna ta saka ido ta gani

Alh Abdullahi Bayan Tashin granny Kai ya girgiza,  domin yadan Indai yana son ganin farin cikinta da albarka a rayuwa dole yayi abunda tace, kuma yasan koda ta kawo matan Indai NAJEEB ne gata gashi, shima Dad d'in yana son dan nasa yayi aure.

Washe gari kaman yanda Granny tace karfe shida dai dai aka sakata a mota ciki harda su zarah da ibtisam da sukace zasu bita, granny tace babu inda zasu, in suka bita a Ina zata saka y'an matan, dole suka hakura mum ta bata su dambun nama, cin cin, cake da sauransu, nan driver yaja suka tafi, cikin mota Mai k'iran Prado, duk da Dad yaso su bar tafiyan zuwa gobe suje a jirgi, granny tace yau zata tafi basai gobe ba, dole Dad ya hakura.

Su zarah gida suka koma, har zata kwana ta tashi tana kallon ibtisam tace Bari in duba d'akin bros in gani, tun jiya yace insa a gyara, kullum sai angyara amma in yazo in ba'ayi wasa ba sai yayi complain yace an bata mishi wani abu, ai gwara Granny ta mishi auren yaje can ya k'arata, tabe baki ibtisam tayi tare da juya baya ta kwanta abunta.

Ibtisam ba ita ta Farka ba sai wajan 11, koda ta tashi Zarah bata d'akin, d'aukan wayarta tayi taga lokaci, tace Kai nasha bacci Sosai, tashi tayi ta shiga toilet tayi wanka sannan ta fito tasa wata jallabiya ba'ka sannan ta d'aura gyalen jallabiyan, zama kiran kabir ne ya shigo wayanta, inda ta d'auka suna ta fira daka karshe yace zaizo ya ganta anjima da yamma.

Tace Allah ya kaimu, yace ta bashi address Sunan Layin ta fad'a mishi da no din gidan, yace OK saiya kirata

Koda suka gama waya, shuru tayi tana d'an tunani, ta rasa mai yasa take d'an jin kabir cikin ranta kwata kwata ko sati d'aya basuyi da had'uwa ba, jiya da yace zai kirata, bai kira ba duk ta damu, toh mai hakan ke nufi? Lokaci d'aya tayi murmushi tare da fad'in dan shine namijin dana Fara kulawa, kuma yana da hankali gashi ya iya magana Mai dad'i dasa nutsuwa.

Jin muryan Zarah tayi tana fad'in Ashe kin dad'e da tashi tunda har kinyi wanka, ina can ina taya mum aiki, wai yau ita da kanta zatai abinci d'anta zai zo.

Ibtisam da bata son maganan NAJEEB tace uhm, Zarah tace muje muyi breakfast tun d'azu nake jira ki tashi muyi tare, yunwa nakeji, yanzu na shigo in tasheki Ashe kin tashi.

Tashi Itbtisam tayi suka fita a dinning suka zauna suka fara cin abinci, bayan sun gama ibtisam tayi kitchen ta gaida mum, tare da fara tayata aiki, suna aiki suna fira, rabin firan duk na NAJEEB ne, shi yasa Itbtisam tayi shuru, sai dai takan yi magana jefi jefi, a haka har suka gama, aka jera komai akan dinning, wayar mum ce tayi k'ara dauka tayi cikin harshen turanci tace son har kazo kenan? Driver yana nan tafe Nasan yama kusa zuwa?

Yace mum nama ganshi saina k'araso, tace ok my only son tare da kashe wayan.

Mum ta kalli su Zarah tace harya k'araso, tunda ibtisam taji haka ta tashi ta wuce d'aki, domin bata son ganinshi balle ya k'ara raina mata wayau, ita rabonta dashi ma zaiyi shekara ko fiye ma

Tana d'aki tana jiyo magananansu harda na NAJEEB daya dawo, ciki harda Dad Sun dad'e suna fira sannan ya tashi ya nufi part d'inshi danya samu ya wuta.

Ibtisam tana nan kwance Zarah ta shigo tace baki fito kun gaisa da Bros ba.

Tsaki ibtisam tayi tare da fad'in dan Allah ki kyaleni inhuta.

Ibtisam dariya tayi tare da fad'in, Allah ya kyauta, itama zama tayi akan gadon d'akin Tana buga game a wayarta.

Kaman yanda Kabir yace wajan 7:30 sai gashi ya kira ibti yace mata yana waje,.

Kallon Zarah tayi tace kabir yazo, yana waje taya zan fita?

Zarah tace muje in rakaki sai in jiraki a bukka inkun Gama saimu shigo tare, ko kuma kice ya shigo mana.

Ido ibtisam ta zare tare da fad'in Rufamin asiri, so kike uncle ya ganni yace ban son karatu, Kome? Salan kisa yace aure nake so, nidai muje saiki jirani a bukka din in fita in sameshi, hakan zaifi

Zarah tace toh muje.

Har waje Zarah ta rakata suka gaisa da Kabir, har suna yar wasa da dariya kaman Sun san juna, komawa tayi ibtisam ta shiga gaban motar kabir.

Kallonta yayi Wanda ta canza kaya Kafin ta fito, wata doguwar rigan atamfa ne, saita yane kanta da wani karamin Gyale, ba karamin kyau tayi ba, duk da fuskanta babu make up, dama ita ba ma'abociyar yin kwalliya bace, yace ibti Anya zan iya jira shekara hud'u kuwa? Karfa wani yamin kwace

Murmushi tayi tare da fad'in ai kaman yanzu ne, shekara hud'un tayi, sannan kamin kyakyawan zato

Yace hakane, kaman yanzu ne, so ya Abuja din? Ashe kina da y'an uwa a nan?

Tace lafiya kalau Alhmdlh, eh uncle d'ina ne

Yace toh nidai na fad'ama ibti koni wanene amma ita ta'ki fad'amin

Murmushi tayi tare da fad'in mai kake son sani a tare dani?

Yace komai, inason sanin komai akan matata dazan aura insha Allah

Murmushi tayi cikin jin kunya, sannan ta Fara fad'a mishi ko ita wacece, tace toh kaji komai yanzu

Yace eh naji komai, ina Ahmad din bros dinmu?

Tace sai Friday yake dawowa gida, boarding school yake, duk da skul din akwai day, yace yafi son boarding din, so duk Friday yake dawowa, saiya koma Sunday, in anyi hutu kuma sai yazo Kano

Kabir yace Allah ya taimaka, ta amsa da Ameen.

Kiran sallah isha'i da akeyi yasa Kabir fad'in Bari in shiga masallaci, da yake akwai masallaci a jikin gidan wanda Dad yasa ayi, itama tace ok bari in shiga gida nima inyi sallah.

Fita tayi tana k'okarin yin nocking aka bud'e gate din, ido biyu sukayi dashi, gabanta taji ya fad'i, shiko kawar da kanshi yayi tare da wucewa masallaci, bayan yaja kofar ta datse kuma yasan ciki zata shiga, tsaki taja tare da fad'in dan rainin wayau, nocking tayi aka bud'e Mata kofar sannan ta shiga, a bukka ta samu zarah Tana sallah, itama alwala tayi a famfo din dake gefe ta cikin ciyayi, bayan zarah ta idar ta amshi hijab din Zarah tayi sallah, Bayan ta idar Zarah tace ya tafi ne?

Ibtisam tace a'ah yana masallaci, yan..... K'aran wayanta yasa bata k'arasa maganan da take son yi ba ta d'auka ganin kabir ne, sawa a kunne tayi ban San mai yace mata ba, naji tace ganinan

Tace ma zarah bari inje in ganshi yace In fito yanzu zai wuce ma

Koda ta fita a tsaye ta ganshi a jikin motarshi, hannunshi ri'ke da Leda, murmushi ya sakar mata tare da fad'in ibti Mai yasa koda yaushe inna kalleki sai inga kin k'ara kyau ne, miye sirrin

Murmushi tayi tare da fad'in babu wani sirri, kawai idonka ne yake ganin maka haka

Yace Kai Anya kuwa? Ni Inda idonane da nafi kowa murna, dan ban son kowa yaga min kyanki saini d'aya, mi'ka mata ledan hannunshi yayi tare da fad'in zan gudu ana son ganina, sai munyi waya.

Tace gskya wannan kyautar da kayi hakuri ka barshi, inaga kaman yayi yawa.

Yace karki manta shaidan shike maida hannun kyauta baya, kuma in banyi ma matar da zan aura abuba wa zamma? Very soon Indai na turo komai ni zan dinga miki dan bazan bari Abba yaci gaba ba.

Uhm kawai tace tare da fad'in ngd, yace ko kefa, sai munyi magana, koda yake muje in rakaki, har kofar gidan suka jera dai dai lokacin NAJEEB yazo shiga gida, ganin yanda suke ma juna dariya abun ya bashi haushi yaja tsaki tare da shigewa gida tunda an bud'e kofar, itama shiga tayi tana fad'in sai anjima.

NAJEEB kam haushi Kabir ya bashi, ya rasa wanda zaiso sai wannan karamar yarinyar mara kunya da bata gaida mutane, hhhhh kunji najeeb fah, wai bata gaida mutane, ya tsaya yana mata dariya, y'ar 15yr ko 12 zance ma, tsaki ya kuma ja, tare da fad'in wasu mazan basu da tunani mutum ya tsaya yana soyayya yana bata ma kanshi lokaci dama Kananan yara ba babban mace ba, yaushe har tayi girman data iya magana da maza, lokaci d'aya ya d'aga kafada tare da fad'in miye nawa a ciki ma

Ibtisam bukka ta nufa inda taga zarah na zaune tana game a wayarta, Zarah ganin leda a hannun ibtisam yasa ta amsa tare da fad'in Bari muga maiya Kawo, tare da bud'e ledan, chocolate ne sai kwalin waya Samsung, Zarah tace inye kin fito gari za'a fara chatting

Ibtisam tace uhm, ai baki Sani ba Abba ne baya son in ri'ke babban waya, yanzu wannan ma ban San yanda zanyi dashi ba Wlh, ko in maida Mai kawai

Zarah tace Kai yanzu saiki maida Mai? Lallai dako kin cika mara wayau, ki boye kawai, balle yanzu nasan dole Abba zai yarda ki ri'ke babban waya, saboda makaranta su browsing da sauransu.

Tashi sukayi suka shiga ciki, inda suka tarar da NAJEEB a falo da Mum yana kallon ball, mum tace daka ina kuma haka?

Zarah tace Mum mun fita siyo abune, ibtisam tace sannu da hutawa Mum, tare da shigewa ciki, NAJEEB kam ko kallo basu isheshi ba, idonshi nakan tv, itama zarah ciki ta shige inda tace ma ibtisam tasa wayar a caji, suje suci abinci, ibtisam tace plz ki kawo mana nan, ki zuba mana, ban son fita na gaji, Zarah tace ok bari in Kawo mana.

Yau kwanan Granny uku da tafiya yola, kuma a yau tace zata dawo, tunda ta tafi sukan yi waya jefi jefi, domin inda Granny take babu network Sosai.

Ibtisam tunda ta had'u da NAJEEB sau d'aya basu k'ara had'uwa ba, ta fito sanye da hijab ya tsaya mata dai dai Giwa, ana ganin dogon wandon da tasa, NAJEEB na kwance akan kujeran falon yana danna waya daka duka alamu yana chatting ne, jin motsin mutum yasa yace a bashi ruwa ba tare daya d'ago ba, banza dashi tayi tare dayin gaba abunta, jin ba'a kulashi ba yasa ya d'ago ya ganta dai dai lokacin tana fita, ranshi yaji ya baci tare da fad'in I will teach her a lesson

Ibtisam samun Kabir tayi a waje, inda ta shiga cikin motarshi, sun dad'e suna fira yayin da NAJEEB yake ta kallonsu ta CCTV, ganin ta fito a motar yasa ya dawo falon ya zauna, koda

ibtisam ta bud'e kofar falon a tsaye ta ganshi a gabanta, d'aga hannu yayi ya tsinka Mata Mari tare da fad'in karki k'ara a rayuwa, ke wacece da ina magana zaki wuce ba tare da kinyi abunda nace ba?

Hannunta dake kan fuskanta ta saitin wajan daya mareta, alaman taji zafin Marin, ta cire tana k'okarin marinshi shima.. Da sauri ya ri'ke hannun tare da murde mata shi ya juyo da ita ta baya, duka suka kalli gaba, yace baki da hankali koh? Ni zaki mara?

Wani irin nishi takeyi na wuya, tare da kokarin ta samu ta kwaci kanta dan murde mata hannun da yayi tana jin zafi Sosai, amma ta kasa Kwacen kanta domin karfin ba d'aya ba.

Yace how dare you, ni sa'anki ne? Ni zaki mara? Jin nishin da takeyi na wahala harda kwalla daya Fara zuban Mata duk da ta baya take yasan tana hawaye dan yaji alama yanda take nishi tare da shessheka ,yace inaso ki bani hakuri tare da alkawarin bazaki k'ara raina wani ba in ur lyf Kafin in sakeki

Ibtisam duk da tana jin zafin murde hannun da yayi mata, bata tunanin zata bashi hakuri domin bata ga abunda tayi mishi ba, dahar zai mareta, sannan yace ta bashi hakuri kuma, jin tayi shuru yasa ya k'ara murde hannun da karfi lokaci d'aya hannun yayi y'ar k'ara 'Kas ta saki wani irin k'ara Mai sauti.......

~MARYAM OBAM~

*NAJEEB*

*BY*
*MARYAM ALHASSAN DAN'IYA*
*(maryam obam)*

*https://www.facebook.com/Maryam-Obam-Novels-441847396162695/*

*http://WWW.Maryamobamnovels.com*

*Wattpad@ Maryam-obam*

*Instagram@maryam_obam*

*DEDICATED TO.....*

*SA'ADATU ALKALI TSAFE🥰🥰💘 MY LOVELY DAUGHTER WANNAN PAGE D'IN NAKI NE SABODA KE NAYI SHI, KIYI YANDA KIKA GA DAMA DASHI🥰*

*PAGE 7*

Ganin haka yasa ya turata ta buge da jikin bango, tare da fita yabar falon.

Mum ta fito da sauri tana fad'in ibtisam fad'i kikayi Subhanallah, tare da nufanta tana k'okarin d'agota, hannun daya murde mata mum ta kamo da sauri ibtisam ta saki k'ara domin wani irin azaba taji da Mum ta ri'ke mata hannun  ganin haka yasa mum tace badai kin buge a hannun ba?..

Ibtisam hawaye ke zuba a idonta Sosai, ga hannunta dake mata zafi, ga bacin rai lokaci d'aya taji kanta na Mata ciwo, tare da tsanan zaman gidan, ji tayi gaba d'aya Tana son komawa Kano gidan Abbanta, mum jikinta ta kama da d'agota, tare da fad'in sannu maiya samu hannun?

A hankali tace babu komai, na fad'i ne, Tana fad'in haka ta wuce ciki inda ta samu Zarah na kwance tana bacci, itama kwanciyan tayi hannunta yana zugi, gaba d'aya ji tayi kaman k'ashin hannunta ya fita dan taji ba yanda ta saba jin hannun ba, wani irin tsanan NAJEEB taji ta kar'ayi ninkin banin kin wanda take Mai, lallai a duniya bata da makiyi yanzu kaman shi, inda za'a tambayeta wata tsana a duniya? Toh lallai NAJEEB zata ce,  kwanciya tayi tana hawaye da haka bacci barawo ya saceta

Sai wajan 6 ibtisam ta farka gaba d'aya ta kasa d'aga hannun da Najeeb ya murde mata, ga wani irin rad'adi da zafi da yake mata sosai, Lokaci d'aya tasa kuka saboda azaba.

Zarah ce ta shigo ta sameta tana kuka, cikin tashin hankali tace lafiya kuwa ibtisam kike kuka?

Ibtisam tace zarah hannu na ciwo yake min Sosai, na kasa d'agashi, zafi yake min

Da sauri Zarah ta nufeta tana fad'in tashi muje hspt maiya samu hannun? Kinji ciwo ne?

Kaita girgiza mata alaman a'ah, tare da tashi tace muje Aban magani zafi yake min Sosai tana shesshekar kuka, fita sukayi inda suka ga Mum a falo.

Ganin ibtisam na kuka Mum ta Fara tambaya lafiya kuwa?

Zarah tace Mum ta buge a Hannu ne.

Mum cikin tashin hankali tace badai faduwan da tayi d'azu bane? Maza kuzo muje asibiti, sannu ibtisam, fita sukayi inda suka shiga mota driver yaja ibtisam na hawaye, har asibiti suka nufa, inda suka nufi reception, receptionist suka fito da file dinsu tunda family card ne, nan suka shiga wajan Dr, inda ya fara fad'in mrs Abdullahi, Sannunku.

Dr kallon ibtisam dake hawaye yayi, yace lafiya kike hawaye? Maiya faru?

Mum tace hannun ke Mata ciwo, ta fad'i ne, nan Dr ya tashi ya ri'ke hannun wani irin k'ara ta saki, ya dad'e yana dan juya hannun sannan yace gocewan 'kashi ne, Bari in kira Dr din kashi yanzu zai zo.

Ba'ayi ko 30mnt ba Dr din yazo bayan anyi gwaje gwaje inda aka fara gyara mata hannun, zo kuga kuka wajan ibtisam zarah kam gaba d'aya tausayin Itbtisam ya kamata harda kwalla, ita kam mum jikinta duk yayi sanyi cike da tausayin ibtisam din, sai take ji kaman a jikinta

Bayan Dr ya gama ya fara ce mata sorry dear, an gama.

Ibtisam kam tasha wuya idonta har yayi ja, dan azaba, an d'aure Mata hannun, wanda ana gamawa ta kwanta akan gadon wajan, babu komai cikin ranta sai tsanar NAJEEB wanda shine silan Jefata cikin wannan halin, ita ta rasa mai tamai ya tsaneta, tun Farko ta gaidashi yayi banza da ita, daka karshe ya zageta, toh miye laifinta danta kama kanta? Sannan miye na shiga sabganta har yace ta kawo mai ruwa bayan baya kulata, baya ganin darajanta, akan wani dalili zai aiketa? Lokaci d'aya ta sauke wani ajiyar zuciya tare da fad'in komai yayi min, danya ganni a gidansu ne, inda a gidanmu ne yaushe zai ganni, Bari Granny ta dawo gobe dole Zan koma Kano I..... Zarah da mum ne suka Katse Mata tunani da fad'in sannu ibtisam.

Ta kasa koda magana sai d'aga musu Kai da tayi.

Dr yace ibtisam dan yaji su mum sun kirata da Sunan, yace yanzu ya daina zafi, tunda Anyi miki alluran cire zafi, za'a baki magani, saiki kiyaye kar kiyi abunda hannun zai kuma gocewa Kinji?

Kaita d'aga mishi alaman toh

Mum ta kalli Dr tace zamu iya tafiya? Koya?..

Dr yace eh zaku iya tafiya, but tayi a hankali, zuwa jibi ku dawo sai muga hannun, kallon fuskan ibtisam yayi tare dayin murmushi yace ibtisam sai ayi tacin nama da yawa, a rage tsalle tsalle.

Ibtisam haushi Dr ya bata, waima a rage tsalle tsalle tunda ya maidata karamar yarinya ai dole yace haka.

Tashi sukayi suka fita inda zarah ta bud'ema ibtisam Mota ta shiga, sannan ta rufe, ita ta shiga gaba, mum baya, Bayan sun shiga driver yaja motar suka wuce

Koda suka isa Gida, Sun tarar da Granny da Mata har guda hud'u, ibtisam da hannu ke ciwo sakan baki tayi tana mamaki, domin kana ganin yaran Kaga y'an kauye futuk, d'aya harda yaro sai dai ibtisam tana tunanin Maman d'aya ce a cikin y'an matan, sai d'aya harda irin kalangun nan na Fulani, sauran biyun su basu da aibu sai dai sunyi yara da yawa, wanda zata ce basu wuce shekara Goma sha d'aya d'aya ba K....  Granny ce ta katse mata tunani tare da fad'in maiya sameki a hannu kuma?

Ibtisam jin haka yasa ta saki kuka, ta nufi Granny tana fad'in Granny faduwa nayi, mu tafi gida gobe

Granny tace garin yaya kika fad'i? Sannu Kinji Kai maiya samu hannun toh? Badai karaya bane?

Ibtisam cikin kuka tace gocewan k'ashi ne Granny

Su mum ko kallon matan da Granny ta Kawo ya hanata magana, tunani take badai suta kawo ma NAJEEB, ba ko waccen su tasha atamfa anyi d'inkin riga da zani, an cabe fuska da kwalli da janbaki, dinkunan yayi musu yawa, ita mai Yaron ma hannun rigan sai Zame mata yakeyi danya Mata yawa Sosai, ga falon gaba d'aya ya d'auki karni duk Kalan kamshin da yakeyi amma zuwan wannan ba'kin na granny yasa kamshin falon ya canza

Granny tace sannu takwarata maza jeki huta Kinji

Ibtisam tace toh Granny amma gobe zamu tafi koh?

Mum tace kina nan, har sai kin warke, sai sannan ibtisam tama tuna Ashe dasu mum take, sai taji kunya tare da fad'in kiyi hakuri mum wasa nake mata, ai nasan jibi zani ganin Dr

Mum tayi murmushi tare da fad'in hakane, kije ki huta Kinji, sannan ta kalli Granny tace sannu da dawowa mama, kunsha hanya.

Granny tace yauwa, hanya bakya, jikina duk yayi tsami, na gaji Sosai, ina wannan Yaron yake ne yazo ga mata nan ya zaba wacce tayi mishi

Zarah bata san sanda ta fashe da dariya ba, tare da fad'in Bari in dubashi, part d'inshi ta nufa amma bata ganshi ba, dan haka ta dawo ta shaida ma Granny da cewa baya nan, mum kam mamaki ne ya isheta, yanzu wa Innan ne NAJEEB zai aura? Lallai kam

Granny ta kalli mum tare da fad'in a basu masauki su huta, Kafin ya dawo.

Mum ta kalli zarah tare da fad'in  kaisu gefen ba'ki, sannan kisa a basu abinci, Zarah tace toh tare da kallonsu tace muje, tashi sukayi suka bita inda takai su gefen ba'ki, sannan ta dawo Taba d'aya daka cikin masu aikin gidan umarni takai musu abinci suci.

Granny mi'ke k'afa tayi akan kujera, Tana zayyano ma mum bayani kaman haka, nasan cikinsu bazai rasa wacce zai zaba ba, ni Inda so samu nema ya auri Mai yaron, mijinta ya rasu ya barta da yaro dan shekara d'aya, gata marainiya, Abun dai gwanin tausayi, kin ganta duk ta tside saboda wuya, in miskili ya aureta Nasan zai ri'ke yaron tunda yana da hali, in kuma duka yake so shikenan saiya aure su, kallon zarah tayi da take ta dariya danta kasa boye dariyan ta.

Tace ku yanzu ba abun kunya bane, gid'a gid'a daku kuna gida babu aure, haba ai wannan abun yayi yawa wlh, yanzu dai Bari a d'aura ma miskili aure, ita takwara ta samu miji, ina fatan Kema kina da saurayi, in baki dashi sai in nemo miki

Zarah dariya ta saki har tanayin k'asa dan dariya, tace Granny Wlh na yafe zan zaba da kaina, dan inna baki zabi sa'an kakana zaki kawo min

Granny ta tamke fuska tare da fad'in, naga dai duk zaban da zakiyi bazai Kai wanda zan miki ba, jiba kyawawan matan dana zabo ma miskili, ku yanzu babu abunda kuka iya sai zaban maza masu shiga irin ta wa incan mutanan, bakwa zabo masu saka manyan kaya, Kema Fulani nake son ki aura yanda zaki dinga jin yaranki, ita ibtisam tana ji, tunda uwarta Fulani ce, Keko uwarki baji take ba Hhhhh Kai granny wannan maganan da takeyi duk a gaban mum takeyi

Zarah tace nikam ban son in iya wannan yaran, Kinga Bari inje in duba ibtisam inga ya take ciki, Granny itama tashi tayi tana fad'in muje Nima inga takwaran tawa, kai wannan Abu baiyi kyauba, Shigowan NAJEEB yasa Granny tsawaya.

Kallonta NAJEEB yayi tare da fad'in sannu Granny cikin gurbatarciyar hausan shi, dabai kware

ba.

Granny tsaki taja tana fad'in shikenan abunda aka iya, sannu daka shi babu wani, ja'iri, ai yanzu na Kawo karshen Abun Wlh.

Najeeb kam ko kallonta bai kar'ayi yi, dan bajinta yake ba, sai dai yana d'an jin wasu kalma kad'an cikin magananta, wanda hakan ya nuna mishi cewa dashi take, dan haka k'okarin barin falon yayi tace Najeebu.... Tsayawa yayi ya tsana Tana kiranshi da wannan Sunan wai najibu, kaman wani d'an kauye, tsaki yaja tare da fad'in what Granny?

Tace kama uwarka tsaki gata a tsaye, mara kunya, kallon zarah tayi tace miye yake nufi da zat Hhhhh wai what shine zat, na daiji yace grandi, zat grandi Mai hakan ke nufi? Ko zagina yayi? Yanzu Inci uwashi

Zarah tace a'a cewa yayi miye Granny

Granny tace oho yanzu naji Batu, matsawa Granny tayi kusa dashi, wanda ya ri'ke kugu da hannunsa biyu alaman yana son ta fad'i abunda zata fad'a ya wuce, dan baya son takura irin Nata ko kad'an

Granny tace miye ka wani kama kugu? Ko dukana za kayi d'an banza, Toh Bari kaji tana mishi magana tana nuna mishi abunda take fad'a da hannu, tace aure za kayi wlh, ta rungume hannunta tare da nunashi tace Kai sannan ta k'ara rungume hannunta tace aure zakayi, na Kawo maka Mata guda hud'u ta nuna Mai da yatsa alaman, kallonta ya tsayayi sannan yace I think this old woman need to see a doctor, am sure she has mental problem.

Mum tace kana dakai kuwa, cikin harshen turanci

Granny kuka tasa Wai suna zaginta, tare da kamo zarah tana fad'in zoki fad'amin Mai sukace? Fad'amin inji.

Zarah tace Granny ba zaginka sukayi, ba, cewa yayi bai gane mai kike nufi ba, zai wuce, shine mum tace bashi da hankali taya kina mishi magana zaice zai wuce baki Gama ba.

Granny tace oho na gane, tare da cema Zarah jeki kiramin matan da nazo dasu.

Kallon Mum tayi tare da fad'in ki fad'ama wannan miskilin ya zauna, in sun fito ya zaba d'aya

Mum ta kalli NAJEEB tace ka zauna son, Granny zata maka magana.

Tsaki yayi tare da zama, yana fad'in wannan matar ta isheni Wlh.

Zarah ce ta fito da matan sun k'ara shafa ma fuskansu, kwalli da janbaki duk sunyi d'ige d'ige.

Najeeb dake zaune ta setin wajan, da sauri ya tashi yana fad'in wa innan wasu irin kazaman masu aiki kuka Kawo mum? Haba mum taya zaki kawo irin wannan yaran, plz ki sallamesu, Niko Abu suka taba bazan iyaci ba, kallon zarah yayi tare da fad'in plz tell them subar falon nan, sai wari sukeyi

Suko da bajin abunda yake fad'a sukeyi ba, duka sun saki baki suna kallonshi, domin fad'i suke Ashe bature ne, irin mamanshi, sai fari suke mishi da ido

Zarah tace bros wannan matan fah ba y'an aiki bane, Granny ta Kawo ne ka zabi d'aya ka aura.

Yace what? Wani irin kallo ya watsa ma Granny tare da fad'in you better tell them to leave, tun Kafin in illatasu tare da sakin tsaki yabar gidan ma gaba d'aya cikin bacin rai, Granny kam fadi take Ina zaka, ke Zarah kira mun dan banza.

Zarah tace Granny shifa yace ki fad'a musu su wuce tun Kafin ya illatasu

Granny tace au haka yace, zanyi maganinshi Wlh Bari audullahi yazo, wlh duka za'a d'aura mishi su zanyi maganin rashin kunya miskili mara mutunci. Kuyi manage plz na gaji sai gobe ko jibi kuma

~MARYAM OBAM~

*NAJEEB*

*BY*
*MARYAM ALHASSAN DAN'IYA*
*(maryam obam)*

*https://www.facebook.com/Maryam-Obam-Novels-441847396162695/*

*http://WWW.Maryamobamnovels.com*

*Wattpad@ Maryam-obam*

*Instagram@maryam_obam*

*DEDICATED TO.....*

*MY LOVELY MUM*

*PAGE 8*

Granny barin falon tayi,bayan tace ma y'an matan su koma, ta nufi d'akin zarah inda ta iske ibtisam kwance tana baccin wahala,  cikin tausayin ibtisam tace sannu Allah sarki dole kiyi bacci, gocewan k'ashi akwai azaba, targad'e mutum yayi yasha azaba, balle ace k'ashi ya goce

Zarah ta shigo d'akin Tana fad'in Granny bacci take amma kina damunta da surutu.

Granny tace Hmmm, wlh tausayi taban, gocewan k'ashi akwai azaba, Allah sarki takwara, Allah ya baki lafiya, k'aran wayan ibtisam yasa Granny tace wayar Waye haka? Duba ki gani karya tasheta k'aran,  zarah d'auka tayi taga kabir, tace Granny kabir ne.

Granny tace Kabiru dan arziki d'auka kiban, dannawa Zarah tayi tare da mi'ka ma Granny, Granny tasa a kunne dai dai lokacin Kabir yana fad'in my ibti,  da sauri Granny ta cire wayar a kunne tana son fad'in abunda yace mi ibt, lokaci d'aya kuma ta maida wayar a kunnenta tare da fad'in Kai Kabiru grandi ce.

Gaidata yayi tare da fad'in ya Abuja?

Granny tace habuja lafiya, kasan takwaran tawa ta samu gocewan k'ashi koh? Yanzu haka bacci takeyi

Yace Subhanallah, wlh ban sani ba, yaushe hakan ya faru? Dazu nazo na ganta fah?

Granny tace Kabiru a Ina ka ganta ita da take habuja, yace Granny Nima ai nazo Abuja din

Granny tace ah lallai soyayya, toh sai kazo ka dubata inta farka, yanzu dai tana bacci, yace insha Allah Zanzo inganta tare da kashe wayan, yana tunani, wani abokinshi dake kusa Mai suna Tahir yace kabir lafiya kuwa?

Yace Wlh ibti nace ta samu gocewan k'ashi, kuma dazu mun had'u, kai Wlh banji dad'i ba, ko kad'an ban son in ganta cikin damuwa, ina sonta da yawa

Tahir yayi murmushi tare da fad'in ina matsayin amininka, komai naka kana fad'amin amma shine baka fad'amin wannan ba, Allah ya bata lafiya

Kabir ya amsa da Ameen, tare da fad'in sorry Tahir naso sai Abu ya kankama Kafin in fad'a maka, domin kasan dagaske nake

Tahir yace Toh wannan wace yarinya ce haka da Abokina ya mutu a kanta? Gaskiya ko wacece tayi sa'a, toh amma irin halin da kake son mace dashi ita tana dashi?

Kabir yace Sosai kuwa, wannan shine dalilin da yasa na K'ara Sonta, sai dai abunda yake damuna, tana da burin tayi karatu, toh ni banda matsala, infact ma Ina son iyalina suyi karatu Mai zurfi, but matsalan shine ita ta'ki yarda muyi aure wai saita kammala karatu nan da shekara hud'u, ni kuma gashi an matsa min akan ya kamata in ajiye iyali, gashi wacce nake so tace sai nan da shekara hud'u, so ni Abun ma duk ya jagula min lissafi, gashi nace mata na amince data gama karatun, kuma gaskiya ban tunanin family d'ina zasu yarda Wlh.

Tahir dariya yayi sannan yace mutumi na an fad'a love, Niko in zaka dubiya tare zamu inje inga wannan yarinyar data tafi da Abokina, Toh amma Indai har Tana Sonka zata yarda kuyi auran, ai wannan ba hujja bace mace tace saita kammala karatu Kafin tayi aure, hakan bai kamata ba, aure ai baya hana karatu, sannan tace ka jirata shekara hud'u ai yayi yawa, sai kayi ta zama haka? Ni gashi inada yaro d'aya gana cikin na biyu amma kai har yanzu kuma Nima iyalin nawa na karatu, ya kamata ka mata bayani Sosai in Tana Sonka zata yarda.

Kabir yace sai dai in wakiltaka, dariya Tahir ya saki tare da fad'in ikon Allah, wato Kai bazaka iyaba, inko hakane zaka rasata Wlh, ko ince zata shigo Ata biyu, dan Nasan Wlh baza'a Bari ka K'ara shekara biyu babu iyali ba, balle har shekara hud'u haba is too much mutumina, kabir yace kai Abokina nifa bani da ra'ayin ajiye mace fiye da d'aya, ibti ta isheni kawai, nidai na wakilta ka, kayi Mata bayani kawai yanda zata fahimta.

Tahir dariya yayi sannan yace babu damuwa, yaushe zaka dubiya, sai muje danta sanni, inta warke daka baya mayi mata maganan, koya kace?..

Kabir yace hakan yayi, sai mu shiga zuwa anjima Bayan sallah isha'i. Tahir yace Toh Allah ya kaimu

Koda NAJEEB ya fita, wani store yaje yasai giyanshi, tare da tafiya dashi, yaje ya kama d'aki a hotel, domin ya sha abunsa, tunda yake bai taba shan giya a Nigeria ba sai yau, saboda duk abunshi yana taka tsan tsan, dan baya so ya batama iyayenshi rai, koya zubar musu da Kima, uhm Najeeb kenan, baka tunanin Allah, Allah yasa mu dace,.

Koda ya shiga bud'e kwalban yayi ya fara sha, domin granny tayi matukar bata mishi rai, wai kaman shi, Najeeb za'a ce ya zaba cikin wannan kazaman matan, ido ya lumshe yaci gaba da Kwan kwadar alcohol d'inshi, lokaci d'aya ya fara surutu ni NAJEEB ni that old woman zata ma haka, ta rasa wanda zata kawo min sai wa innan dako takalmi na bazan iya basu su goge min ba, zanyi maganin wannan tsohuwar Wlh, tunda nace mata ina son aure ai dole ta Kawo min wa innan tarkacen, koda nace ina son auren ni banda ido ne K... Shuru yayi lokaci d'aya kuma ya saki tsaki tare da fad'in Wlh ta raina ni that old woman, ci gaba yayi dashan alcohol d'inshi har saida ya shanye duka kwalban sannan yayi jiba dashi gaba d'aya wani bacin ran da yakeji saiya nemeshi ya rasa, baya iya tuna komai, toh taya Zaima tuna tunda a buge yake, k'okarin tashi yayi lokaci d'aya ya fad'i akan gadon bacci ya D'aukeshi

Zarah kallon Granny tayi wacce take ta cema ibtisam sannu, tace Granny Wai yanzu wa Innan matan Najeeb zai aura? Ibtisam dake zaune hannu na Mata azaba domin alluran da aka mata na cire zafi ya gama aiki, ta d'anja tsaki mara sauti domin jin an kira sunan Najeeb din.

Granny tace kwarai kuwa, duka zansa a aura Mai su, tunda shi Dan banza ne, inko kikaga bai auresu duka ba toh a ciki ya zaba d'aya ne, ni Wlh mai Yaron nake so ya aura, yaron tausayi yake ban, duk ya fige, Kinga ya murmure Idan miskili ya auri uwarsa, zasu tafi inane ma yake aiki k'asar masu jajayen fatan nan?

Zarah ta kwashe da dariya tare da fad'in America.

Granny tace yauwa Ameka.

Ba zarah ba harda ibtisam da hannu ke Mata zugi sai da tayi dariya

Zarah tace Kai granny America ba Ameka ba, kawai kice Turai in baki iya fad'a ba

Tsaki Granny taja tare da fad'in kince Ameka, maina fad'a ba dai dai ba Ameka

Ibtisam ganin irin kallon da yayi mata yasa itama ta galla mishi harara tare da tashi tabar wajan ma, "Najeeb ji yayi kaman ya janyota ya mareta but Koba yanzu ba I will teach her a lesson, saina cire mata hannunta da taji ciwo idiot.

Dad yace maganan tafiyanka gobe Ina son ka d'aga, saboda tare zamu yola dakai.

Yace Dad mai zanyi a yola kuma?

Dad yace maganan daurin aurenka

Murmushi yayi tare da ciro wata takarda yace wannan takardan na rubuta saki uku, so idan kun d'aura auren saiku duba ku gani, "Dad Wlh bazan aureta ba in kuma kuka aura min ita Wlh nan take zanyi abunda za'ayi da'an sani, yana fad'in haka yabar wajan Fuuuuu

Granny tace ikon Allah miye haka kaman iska, Mai yake fad'a ne?

Dad shuru yayi cikin bacin rai, lallai Najeeb yana son yayi Fito na fito dashi, ya kamata ya koya mai hankali

Mum bata ce komai ba, sai Zarah data tashi ta nufi Granny tana fad'a mata abunda Najeeb yace, tare da fad'in Wlh Granny tunda baya so inaga Ayi hakuri kawai kar Ayi abunda za'a zo ana dana sani.

Granny shuru tayi tana nazari.

Hanne ce ta fito ita da d'anta a hannu, Tace Sannunku?

Granny tace Hanne lafiya kuwa?

Tace nidai gaskiya bana son wannan auren, dan Allah ku maidani gida, wlh bana son wannan auren, ni nasan yafi karfina, kawai ku maidani gida

Granny tace ikon Allah, mai kike fad'a Hanne?

Tace eh ni bana son auren

Granny tace ikon Allah, keda nake tausayawa saboda d'anki shine kike fad'in haka?

Hanne tace Idan saboda d'ana ne, kawai a taimaka min yafi, bana bukatar inyi auren da ba'a sona, ni nasan yafi karfina nesa ba kusa

Granny ta tashi ta nufeta cikin sigar rarrashi Tana fad'in haka Hannatu kodai yayi miki wani abu ne? Karki damu Ina nan babu abunda zai faru ki kwantar  da hankalinki Kinji Hanne na?...... Toh Bari muji yanda zata kaya

Plz need ur prayers Wlh banda lafiya

Read and leave it, dnt share to anyone

*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Hanne tace kiyi hakuri Baba, bazan iya auren shiba gaskiya,

Granny salati ta saki, tare da fad'in oh ni aminatu, waike Hanne kanki d'aya kuwa? Maiya sameki haka?

Hanne kuka ta saki tana fad'in ita bata san wannan auren, kawai a Mai data yola.

Mum ganin haka yasa tace kiyi shuru, Kinga kina son saka d'anki kuka.

Zarah kam murmushi takeyi, domin ita d'aya tasan abunda ta k'ulla,"Wanda ko Najeeb bai sani ba.

Granny tace Hanne ko anyi miki wani abu ne? Janta tayi sukai d'akin da sauran matan suke, "suna ganin Granny suka fara gaidata,  tare da k'okarin boye kud'in hannunsu Wanda Granny ta shigo taga suna kirgawa.

Granny kallonsu ta tsayayi tare da fad'in "wannan kud'in fah? Daka ina suka fito?

Nan su duka suka fara kame kame tare da sunkuyar dakai, "Granny tace bada ku nake ba? Cikin tsawa.

Nan Hanne ta Fara bata Labarin abunda ya faru, tare da fad'in koda kanwarshi ta kawo kud'in ta fad'a mana gwara mu amsa ince bana son auren "dama ni ko batace haka ba, wlh baso nake ba, dan Nasan bamu dace ba, "kuka Hanne tasa tana ro'kan Granny akan tayi hakuri ita Kar Ayi wannan auren dan zata cutu  tunda baya Sonta.

Granny shuru tayi,lokaci d'aya ta Fara magana "tare da fad'in ya isa haka, ku kwanta zuwa gobe, insha Allah zamu yola kunji? "suka amsa da Toh ,"Granny fita tayi daka d'akin.

Granny iske Dad tayi a falo shida Mum, daka gani suna jiranta ne, "zama Granny tayi tare da

d'aura hannunta akan fuskanta tana d'an bubbuga k'afa alaman ranta a bace yake.

Dad yace mama lafiya kuwa?

Tace audullahi d'anka baida mutunci, "tsorata y'ay'an mutane yaje yayi tare da basu kud'i, akan karsu yarda da auran.

Dad yace mama ban gane ba.

Nan Granny tace dama yaushe zaka gane?

Yanzu dai abunda za'ayi gobe zanje yola in maida yaran nan, badai auren bane baya so? Sai musa mishi ido ai.

Dad yace a'ah mama kar Ayi haka, kaman yanda aka tsara hakan za'ayi, goben zamu a d'aura aure, insha Allah, "kaman yanda muka shirya

Granny tace ai wannan maganan auren babu shi, tunda ita yarinyar tace bata so, " ya tsorata

Dad yace Wlh mama sai an d'aura wannan auren ko baya so, koda kuwa zai mutu,.

Granny dai shuru tayi tana nazari, can ta tashi Tana fad'in Allah ya kaimu raida lafiya tare dayin cikin d'aki ta kwanta.

Washe gari da safe tunda sukai sallah asuba suka Kama hanya su duka," amma banda Najeeb damin bai tashi daka bacci ba, sai dai Mum ta mishi message akan sun tafi yola

Sai wajan 10 Najeeb ya tashi Kai tsaye toilet ya nufa yayi wanka, tare dayin alwala, sai a lokacin yayi sallah, Bayan ya gama shiri ya d'auko wayarshi sai a sannan yaga sa'kon Mum, wani irin tsaki yaja tare da fad'in mai suke nufi?

Kenan sunje d'aura aurena kenan?

Kai ya girgiza tare da fad'in no no baza suyi wannan mistake d'inba, am sure.

Kawai sunje maida yaranne suba parent d'insu hakuri akan d'auko su da akayi, wannan tunanin da Najeeb yayi shine ya bashi daman cire komai a ranshi, shima daukar jakarshi yayi, yasa a mota driver yaja sukai hotel din da Gina take, baiko shiga ba ya kirata a waya tare da fad'in "come out, "yana fad'in haka ya kashe wayanshi .

Bata jima ba sai gata ta fito d'auke da k'aramin akwatin ta, kai tsaye motar ta shiga Bayan driver yasa mata akwatinta a booth, wani irin peck kiss tama Najeeb akan goshi tare da rungumo shi, tana fad'in oh baby I miss you so much

Wani irin kallo ya watsa mata Mai kama da kin cika jaraba, yaushe muka rabu,.

Ganin baice mata komai ba yasa ta k'ara manne shi, shidai driver tuki yake yana Allah wadai da irin wannan rayuwar

Kai tsaye airport yakai su, inda suka sauka, driver ya d'auko musu akwatin yana ja musu.

Shiko Najeeb da Gina suna manne da juna, kai tsaye Najeeb ya wuce domin ansan pilot ne, ba'a tsaya wani duba kayanshi ba, suka shige cikin jirgi shida Gina, Bayan an gama shiga 11:20 dai dai jirgin ya d'aga zuwa k'asar America.

Su mum sun isa yola, inda suka sauka a wani babban hotel, Kafin gobe su shiga kauyen su Hanne, "koda Abban ibtisam yazo shima a nan ya samesu, ibtisam tasha ko harda ummi za'azo sai taga bada ita bane

Washe gari da safe suka Kama hanyar kauyen su Hanne, inda sukai tafiyan awa biyu, Kafin suka k'arasa, "kauyen gidana irin na Fulani sai wajajan kiwon su.

Sauke su Granny sukayi a gidan y'an uwanta tare dasu ibtisam, su kuma Su Dad suka nufi wajan sarkin anguwan suka nufa, wanda shine sarkin fulanin gefen wajan, inda aka amshesu cikin mutunci da girmamawa, nan Dad ya fad'ama sarkin abunda ya kawo su,inda yayi na'am ya kuma bu'kaci a kira kawun Hanne.

Hakan ko akayi aka kira kawunta, inda ya tubure akan Wlh bazai amince da wannan aure ba, domin an mata miji cikin dangi akwai wanda yace zai aureta saboda yaronta zai ri'ke mata shi, yace sarki yanzu Kaga ni gwara muba na gida akan muba na waje.

Sarkin Fulani yace wannan hakane, amma ai suma na gida ne, tunda suna jin fulatanci suda yaransu duk da ba'a nan suke da zama ba, Koba haka ba? Tare da kallon Dad

Dad yace eh Toh gaskiya nan d'aya, yaron dai bayaji, sai dai mu muna ji

Nan kawun Hanne yace Toh ku kad'o ne koh?

Dad yace a'a mu Fulani ne mana, nan ya fad'a musu sunan mahaifinsu, kawun Hanne yace na sanshi mana, inda ban sanshi ba ai bazan bada Hanne a tafi da ita ba can bariki ba. Yace kenan baya jin fulatanci? Shuru yayi Kafin yaci gaba da fad'in.

kawun Hanne "yace kenan ku rabi da rabi kad'o da Fillo, toh gaskiya bazan yarda ba inba kad'o auren Hanne ba, "Yaje ya kaita shan Bariki ya ajiye ba.

Sarkin Fulani shima tunda yaji ance yaron baijin fulatanci yaji gaskiya wannan maganan bamai

yihuwa bace, dan basa bama kad'o auren y'arsu cikin wannan kauyen, duk da sun San su Dad ba kad'o bane Amma ance yaron nasu baya jin Yaren fulatanci ,

Abban ibtisam yace Amma Al Ina ganin wannan ba matsala bane dan yaron baijin yare....

Sarkin Fulani yace matsala ne babba, mu muna mutunta yaranmu, ku kun tafi Bariki bakwa damuwa da nuna ma y'ay'anku yaransu, "Gaskiya kuyi hakuri bama Hanne ba kaf kauyen nan babu Mai baku auren y'arsu Indai sun San yaron bayajin yaren fulatanci, domin dashi da kad'o babu maraba.

Babu yanda su Dad basuyi ba, amma suka kafe, tare da fad'in d'ansu kad'o ne, haka suka tashi suka koma inda suka sauke Granny, yaro suka tura akan a fad'a musu sun dawo, "Mum ce ta fito tana fad'in su shigo mana .

Dad yace a'ah basai Sun shiga ba, tace ma Mama ta fito su wuce kawai.

Komawa Mum tayi ta kira Granny inda ta sami yaran nata a waje, tace lafiya badai har an d'aura auren ba?

Abban ibtisam yace a'a mama.

Tace toh maiya faru?

Yace... Sai kuma yayi shuru

Tace me inaji ku fad'amin mana?

Abban ibtisam yace Wai baza suba kad'o auren y'arsu ba.

Granny tace toh su Waye kad'on Toh?

Abban ibtisam yace Wai Najeeb tunda baya jin Yaren fulatanci.

Granny tace amma dai wannan ko yan wulakanci, akan wani dalili zasu kirashi da kad'o? Babu komai zan nema mishi Mata wacce tafi tanan Wlh, bari inyi musu sallama mu Kama hanya, ni naji zaman nan yama isan,"jikan nawa zasu kira da wani kad'o dan wulakanci tsaki taja tare da shiga cikin gidan inda tace su Zarah su taso su wuce tayi musu sallama Bayan ta basu kud'i.

Mum kam taji dad'in haka Koba komai d'anta yanzu bazai auri wacce baya soba, kuma y'ar kauye ta bakin nashi, "yanzu Abu d'aya zata dage shine ya koma karatun addini tunda ba'a girma da neman ilimi, sai dai Anfi so mutum yayi tun yana yaro, domin lokacin kwakwalwanshi yana saurin d'auke Abu, ba kaman Idan mutum ya girma ba.

Ibtisam kam ba'kin ciki kaman ya kasheta, "Wlh taso a d'aura ma Najeeb Hanne taga ta tsiya da miskilanci, da mugun hali tsaki taja.

Granny tace ke dawa kuma wannan tsakin kaman wata tsaka?

Ibtisam tace Kai granny miye na dangantani da tsaka kuma? "tare da sakin wani tsakin

Granny tace aikin banza, naga koda tsaka tayi tsaki Allah tsine Mata yayi balle mutum

Uhm kawai ibtisam tace tare da kawar dakai gefe guda

Granny ta tsuke baki tace ai inaga keda Najeebu zan had'a Idan Kabiru bai turo ba, dan naga abun nashi wasa ne.

Zarah tayi caraf tace Wlh kuwa Granny Nima haka nake Fata, kawai a had'asu, Kinga sun dace Sosai

Ibtisam banza dasu tayi, amma kallo d'aya zaka mata kasan ta cika tayi fam, a kumbure take, domin haushin wannan maganan take har cikin ranta wlh, gashi Mum na cikin motar balle tayi wata magana, dole yasa tayi shuru suke ta fad'a mata magana akan a had'ata da Najeeb

ita kam mum dariya kawai takeyi.

Tafiya suke har suka k'arasa hotel din da suka sauka, duk a gajiya, Zarah da ibtisam d'aki d'aya, Mum da Dad ma haka, sai Granny ita d'aki daya, sai Abban ibtisam shima d'aki d'aya.

Suna shiga ibtisam toilet tayi domin tayi wanka danta matukar gajiya Sosai, bayan ta fito wayarta ta Fara ruri "Zarah ta mi'ka mata wayan dan yana kusa da ita tace Kabiru na kira.

Hararanta ibtisam tayi domin tana jin haushinta ita da Granny.

Amsan wayar tayi tare da dannawa, "Zarah kam dariya tayi tana fad'in ikon Allah.

Ibtisam na waya ita da kabir, aka fara musu nocking, bud'e kofar akayi inda Granny ta Kutso kai Tana fad'in tare daku zan kwana, bazan iya kwana ni d'aya ba a nan

Zarah tace Mai yasa Granny?

Granny tace haka kawai, "ni tsoran wajan nan nakeji "yama kuke cema wajan?

Zarah tace hotel?

Granny tace eh zatol.

Zarah dariya, ibtisam dake waya itama Katsewa tayi ta Fara dariya,wai zatol.

Granny tace miye kuke dariya kaman kun zare? Ko kuma sabbin hauka?..

Ibtisam tace Granny miye wani zatol, hotel fa akace.

Granny ta tsuke baki tana fad'in kunce zatol, Nima haka nace zatol, "Toh miye ba dai dai ba?..

Kiran kabir ne ya k'ara shigowa ibtisam ta d'auka.

Granny aka tabe baki ana fad'in sai waya amma ya'ki fitowa, "lokaci kad'an na baka, koka fito ko in bata wani, bazan iya wannan tsiyar ba, da kashe kasuwa ba, kai bada fitowa ba, ka tarema wasu waje.

Gashi yanzu anje nema ma miskili aure anki bashi dan bayajin fulatanci, kai wannan rayuwa damai tayi Kama?"yau an nuna min iyakata koda yake suna da gaskiya, Sun nuna muku suna daraja harshen su, amma iyayenku Sun watsar dashi, sun koya muku Yaren aro, Yaren masu jajayen Fata, sai kuma Hausa daba yaranku ba, tsaki taja tana fad'in ai yanzu kwasan darajan yaran naku.

ita kam Zarah cikin ranta cewa tayi Allah  yaga abunda ya gani sai yasa Najeeb baya ji, inda yana jin fulatanci dayau an d'aura mishi Hanne, "amma a fili sai tace Granny Suma sai basuyi niyan bashi matar bane inda sunyi niya Aida Sun aura mishi ko baya ji, ina ganin yare bashi bane matsala a aure, yanayin kamalan mutum da kuma addininsa.

Granny taja tsaki tare da fad'in inko kamala za'a duba, babu maiba miskili auren y'arsa, "Yaron da kana fad'a yana fad'a, Allah ya rage ma Aya za'ki dabai iya Hausa ba, inda ya iya Hausa Allah kad'ai yasan irin tsiyar dazai shuka, farin banza da hofi

Dariya Zarah ta saki tana fad'in Kai granny..

Granny tace eh mana "baki ga saboda ba'kin halinsa ba, har Hanne tace bata son auren, duk da harda ke aka had'a baki, amma ita ta nuna bata sonshi dagaske, miskilin banza dana hofi, "ki ganshi a fili kaman mutumin kirki amma inya tafka tsiya Kya rantse bashi bane, munafiki

Zarah tace shine munafukin kuma? Masoyin naki?

Granny tace ai Wlh bai gado mai sunan ba ko kad'an, domin ba haka yake ba, "ke inda Kinga Mai Sunan Aida kince Miskili ba halinsa ya gado ba, domin shi mutum ne mai saukin Kai da sanin darajan d'an Adam, baya raina kowa, "gashi ya iya soyayya kai zamanin mu munsha soyayya Allah yaji qanshi, kai sai kuma ta Fara share kwalla "alaman ta tuna da rayuwarsu tada

Zarah tace wayyo Granny kiyi hakuri Kinji? Allah yaji qanshi yasa ya huta

Granny cikin kuka tace Ameen.

Ibtisam dake waya tace nifa Granny kin isheni gaskiya, ki tashi ki tafi d'akin ki.

Granny ashar ta kunduma mata tare da fad'in kinci gidanku, y'ar banza.

Ibtisam dariya ta Fara, "KABIR yace kina tare da Granny ne?

Tace eh muna tare duk ta ishemu da surutu

Jin haka yasa Granny Jan tsaki tare da fad'in zanyi maganinki, kanki zan dawo yanzu, "tunda miskili dai baida farin jini anki bashi mata, "Dan bai iya fulatanci ba

Ibtisam sallama sukai da kabir suka zauna suna fira da Granny, inda Granny take basu shawara akan suyi aure, domin Sun tsufa a gida

Granny tace Wlh Idan kuka je jami'a kallon y'an iska za'a dinga muku, "kuma a jami'a a nan yara ke lalacewa, baki ga yanda miskili ya koma ba ya fetsare ya koma mara mutunci ba? Ana fad'a yana fad'a, dan banza mara kunya

Zarah tace Granny, shifa university ba haka yake ba, mutane ne suke mishi wani irin kallo, duk da akwai wanda suke lalacewa a can, amma mu Granny kiyi mana kyakyawan zato.

Uhmm Granny tace tare da fad'in nidai Ina baku shawara Wlh ku fito da maza kuyi aure tun Kafin lokaci ya k'ure muku ,"domin matan da sukai karatu basu cika samun mijin aure ba

Ibtisam tace injiwa? Mata nawa sukai aure Bayan sun kammala karatu? Kai Granny waike wake fad'a miki wannan labarin kanzon kurege dinnan ne?..

Granny tace uwaki ke fad'amin, "ke bakya ganin abunda ke faruwa ne a duniya? Ai nasan Kun San komai dake wakana, "yarinya zata tai karatu saita gama babu mijin aure, daka wannan yazo ya dauketa sai wancan yazo, in tayi Sa'a ta samu miji Toh sai kuga tsoho ne komai mata..

Dariya Zarah ta saki tana fad'in Kai granny wannan sharri haka? "Wanda ya fad'a miki wannan maganan ba gaskiya ya fad'a ba..

Ibtisam tace fad'a mata dai.

Tsaki Granny tayi tare da fad'in abunda yake a zahiri, maza yanzu basa son auren y'ar jami'a, domin suna ganin kaman idonta a Waye yake Sosai, kuma haka dinne "yara an turasu wani gari karatu babu Mai kwaba a can Al dole suyi ta tsula tsiya, iya son ransu

Ibtisam tace Granny ko ina akwai y'an banza akwai na Allah, "karki manta karatun y'a mace yana da matukar muhimmanci," Kema da kinyi karatu da yanzu tayu kina da ma'kami a gwamnati.

Dariya Zarah ta saki tace aikuwa, da yanzu hala kina office d'inki zaune, kina sanye da glass kina zuba turanci

Tsaki Granny taja tana fad'in Al gwara da Banyi ba, "Wlh nidai na fad'a muku ku fito da mazajan aure tun lokaci bai k'ure muku ba, "domin indai kuka tafi jami'a babu aure toh samun mazan aure sai kunji jiki, Inba so kuke ku auri tsoho ba sa'ana ko kuma mai mata biyu ko uku

Dariya ibtisam tayi tace ai gwara in zauna banyi aure ba, da in auri tsoho ko Mai mata ba, "Kut nifa ban son kishiya Wlh.

Granny tace in bakya so fito da miji tun kan ki tafi jami'a, inko kikai wannan kuskuren damai mata zaki k'are in kinyi Sa'a kenan, in kuma bakiyi ba ki k'are da tsoho Sa'a na, ko wanda ya girmeni mara hakori

Ibtisam da zarah dariya suke Sosai suna fad'in lallai kam wa yaga mara hakori, "zarah tace Tashin hankali

Granny tace kuna d'auka wasa nake koh? Shikenan ai

Karan wayar zarah yasa ta d'auka tana dariya domin taga Sunan Najeeb ne, tace Bros har ka tafi ne?

Mai yakon ya bata amsa sai yace Maiya kaiku yola?

Tashi tayi ta fita Tana fad'in Wlh munje akan maganan aurenka ne

Yace what?

Tace kwantar da hankalinka bros ba'a d'aura ba.

Yace what happen?

Labari ta Fara bashi yanda akayi

Yace better domin inda an d'aura nan take zan saketa saki uku

Zarah tace uhm

Kashe wayarshi yayi gaba d'aya danya samu ya kwanta ya huta koda ya kwanta kasa bacci yayi domin ya gaji gashi ya kora Gina data mishi massaging, tunani yai tayi Kala Kala

Lallai shida ya k'ara zuwa Nigeria saiya dad'e tunda Idan yazo har Dad na biyema wannan old woman din , wai shi za'a d'aura ma widow kuma Mai yaro yar kauye, "murmushi yayi tare da fad'in god forbid, "bazan iya shiga ramin da wani ya shiga ba, kai never, inda wacce zanyi wani abu da itane da sauk'i, amma aure kam never in auri bazawara, ido Ya lumshe lokaci d'aya yana Mai jin zafin abunda akaso mishi, "taya zai auri bazawara wacce ta tabayin aure?

Murmushi ya saki lokaci d'aya tare da fad'in, I think inna tashi aure bazan fad'a musu ba sai dai suga mata, koda zanyi aure secret marriage zanyi, Danni inna auri mace bazan saketa ba, domin inna rabu da people will say my ex wife, I won't let that happen, ina da kishin abunda nake so, gwara ace ta mutu akan ace na saketa har a kirata da ex wife d'ina, tsaki yaja tare da fad'in ni bama auren bane a gabana, Indai Mata ne gasu nan like Recharge card everywhere you go, murmushi yayi tare da fad'in na them they rush us, so why will I marry? In ajiye abunda zai daman no bazanyi wani aure ba, ban son takura.....

Read and leave it, don't share to anyone

*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Washe gari tunda sukai sallah asuba suka Kama hanya, domin so suke su isa da wuri,"ibtisam taso a tabi Abbanta su koma tare, "amma Dad yace dole tare zasu koma dan zasu wuce Zaria maganan registration d'insu hakan yasa ta bisu Abuja din suka koma tare.

Sai wajan yamma suka k'arasa gaba d'aya a gajiye suka shiga gidan, koda suka isa su ibtisam d'akinsu suka shiga, "kai tsaye toilet ta nufa dan tayi wanka ko zataji dad'i,"Tana fitowa itama Zarah ta nufi toilet din dan tayi wanka.

Bayan sun kimtsa suka nufi falo dan suci abinci, kowa na gamawa ya wuce bedroom dan hutawa, "Granny kam fad'i take Ahmad ya huta dabai bimu ba, "ni ku bani man zafi inje in shafa a kafata wannan wahalan zama haka. "Niko wancan karan da naje yola bansha wuya irin haka ba, haka dai ta tafi tana mita waita gaji kafafunta  na mata ciwo Sosai.

Washe gari da safe wajan 11 su ibtisam suka farka, kai tsaye falo suka nufa, "Mum suka gani tace sai yanzu? Ai tun dazu na shiga d'akinku naga baku farka ba,"gaskiya kunsha bacci ko duk gajiyan ne haka?

Zarah tace Kai mum wlh akwai gajiya, irin wannan tafiya haka.

Gaida mum ibtisam tayi, "Mum amsawa tayi cikin sakin fuska, tare da fad'in ansha hanya, "dariya ibtisam tayi tare da fad'in kai Aini mum ban taba yin tafiyan da nasha wuya irin wannan ba.

Zarah tace ina Granny ne wai?

Mum tace itama tana d'aki tana bacci, bata farka ba, har yanzu.

Kai tsaye d'akin da Granny take ibtisam ta nufa,"ganin Granny tayi tana bacci, yanda take baccin harda munshari wannan shine zai tabbatar ma mutum da cewa lallai Granny a gajiye take Sosai, dariya ibtisam tayi sannan ta fita falo dan tayi breakfast danta Fara jin yunwa.

Granny ba ita ta tashi ba sai wajan karfe d'aya lokacin ana kiran sallah azahar,"Bayan ta farka ta Fara mi'ka tare da fad'in kai yau nasha Bacci, toilet ta shiga tayi wanka, tana jan y'an kafafunta.

Granny falo ta fito inda ta iske su mum dasu ibtisam da Zarah, "tace shine baku tasheni ba? Kuka barni inata sharar bacci haka.

Mum gaida Granny tayi, "Granny amsawa tayi tare da fad'in Sannunku Ya gajiyan hanya?

Mum tace Alhmdlh, hanya babu kyau babu dad'i.

Granny zama tayi tana fad'in ina yaga dad'i, gaba d'aya jikina tsami yakemin Sosai wlh, damma na shafa man zafi, kar kiji yanda kafana ke zugi kaman nayi tafiya a k'asa, lokaci d'aya kuma "taja tsaki tare da fad'in "duk wannan uban wahalan babu biyan bukata, "ni ko shi miskilin ne yaje kauye yace karsu yarda da wannan auren dai?

Zarah ta kwashe da dariya tare da fad'in "kai Granny taya zaije kauye, shida ko hanyar bai sani ba, inma yaje Mai zaice musu yazo yi? Shida baya jin Hausa, "balle fulatanci, taya ma zai san kauyen da kika dibo matan? mutumin da yake America yanzu.

Granny tsaki taja tare da fad'in kibar miskili ni gaba d'aya ban yarda dashi ba yanzu wlh, amma zan gamu dashi nan bada dad'ewa ba, "zan duba mishi wata matar kwanan nan wlh, zanyi maganin shi, dan banza, mara kunya.

Yau Monday kuma granny a yau zata koma Kano, "su kuma su ibtisam a yau zasu wuce kaduna domin registration d'insu.

Granny driver ya kaita har Kano, yayin da driver din daddy shi kuma yakai su ibtisam Zaria, a hotel suka sauka, inda suka fara kuciba kuciban registration, basu wani sha wuya ba, domin dad yama VC magana, VC ya had'asu da wani, cikin kankanin lokaci sukai komai har an fara shiga Aji an fara lecture.

Su Zarah Abuja suka koma,inda Zarah ta had'o kayanta domin Sun zamu d'aki a cikin skul din su hud'u ne a cikin d'akin, kwanan su d'aya,"suka nufi Kano inda itama ibtisam ta had'o Nata kayan Washe gari zasu koma

Ibtisam na zaune a tsakar gida da Granny da Zarah, suna fira, "Granny tace ku yanzu wannan makarantar kun dage sai kunje koh?

Ibtisam tace Kai Wlh Granny kina da mita, ke kullum magana d'aya kar muje karatu kar muje karatu, haba mana, ki barmu dan Allah

Granny tace kinci uwarki, ai dole in fad'a, tunda ke baki San ciwon kanki ba, dole kice haka, wlh Ina guje muku rasa mazajan aure, "Dan naga ke kabiru kaman bada gaske yake ba, domin kuwa inda dagaske yake aiya kamata ya turo, nifa yanzu haushi yake bani, sai shegen kira a waya, daka zuwanki jiya jiya kin hanani bacci da shegen waya, wlh gwara kibar kulashi in bazai turo ba.

Ibtisam tace au yau kabir dinne ke baki haushi?  "Wai Mai yasa ke Granny baki da gwani ne? Daka kice mutum kaza sai kaza, waya had'ani da Kabir din Inba ke ba.

Granny tace eh muka had'u dai a hanya, kuma Aiko da nace ki kulashi Al danya fito ne Ayi

aure, badan yazo ya kashe miki kasuwa ba, shi bai fito ba baiba wasu waje ba, ni wannan ai mugunta ne wlh

Zarah dariya ta kwashe dashi tana fad'in lallai granny.

Itbisam tace rabu da ita, "itama ta dage saina kula Kabir din, harda wani in amsan Mata number, shine yanzu take kushe shi.

Granny tace aikin banza da hofi Aini da nace ki kulashi a tunani na zai fito ayi biki, amma har yanzu naji shuru.

Ibtisam tace koma dai miye nidai ba damuwa ta bace, kabir dai tunda kika had'ani dashi, dole ki barni dashi, aure kuma saina gama karatu za muyi sh.....

Innalillahi'wa inna ilaihirajiun Granny ta zabga salati tare da tafa hannu, tare da fad'in a ina zaki gama karatun? Wlh badai a gidan nan ba, keda kikai min alkawari za kiyi aure in miskili yayi aure.

Ibtisam tace ai cewa nayi in yayi, toh yanzu tunda baiyi ba, nima ban shirya ba, Kinga in yayi sai nima inyi.

Granny tace zanyi maganinku Wlh kuwa, zan baku mamaki, zan shuka muku tsiya wallahi in baku fito da mazaje ba.

Zarah tace Granny inaga sai Kinje masallaci kin bada sadakan su Gamai bukata

Granny tace yauwa shawara Mai kyau h....

Ibtisam takai ma Zarah dukan wasa tare da fad'in kin San wannan tsohuwar zata iya, wlh ki bari.

Granny tace ai zan baki mamaki wlh

Ibtisam tace kullum haka kike fad'a, dama kin daina fad'in haka wlh

Granny ta galla mata harara tare da fad'in zaki gani Ai, wannan karan bada wasa zan miki ba

Ummi ce ta fito hannunta d'auke da tray, tasa plate guda uku, ajiyewa tayi, faten tsaki ne wanda yaji alaiyahu da Naman rago, ta ajiye ma Granny a gabanta sannan tace ma Zarah "gashi ki d'auka zarah kisha da zafinshi Kafin ya huce

Granny tace inada yaji cikin jakata a d'aki, d'auko min.

Ummi tace bari in d'auko miki, "kai tsaye d'akin ummi ta shiga sai gashi ta kwala ma ibtisam

kira.

Da sauri ibtisam ta tashi tare da amsawa.

Koda ibtisam ta shiga d'akin kwalin wayar da kabir ya bata ta gani a hannun ummi.

Ummi tace waya baki wannan wayar?  Na tabbata inda babanki na abuja ya baki zaki fad'amin waya baki?

Ibtisam tace ummi Kabir ya bani.

Ummi tace Waye Kabir?

Ibtisam tace shine wanda ya taba zuwa, granny tace in fita, harya Kawo min su chocolate, kika ce bakya son Ina am....

Ummi ta daka mata tsawa tare da fad'in Yimin shuru mara tunani, ke yanzu har kinyi girman da zaki dinga amsan abu wajan samari, har a baki kyautar waya koh?

Mai Abbanki yace miki akan ri'ke babban waya? Yace baya sonki da babban waya, Shine har kin iya amsan na saurayi koh? Yayi miki kyau, "ummi fita tayi wayar na hannunta ta fita takai ma Granny yajin ta koma d'aki ta ajiye wayar, sannan ta fito

Ibtisam kam cikinta ya dura ruwa, domin tasan yau kashinta ya bushe Idan Abba yaji labari, gaba d'aya kasa fitowa tayi daka d'akin domin jinta tayi zazzabi ya kamata lokaci d'aya.

Granny tace Wai ina takwara tane? tabar abincinta a bud'e saiya huce, "kwala mata kira Granny tayi tare da fad'in ibtisam kina inane?

Fitowa tayi kamar wacce kwai ya fashe mawa a ciki, tace Granny gani.

Granny tace kizo kisha wannan fatan koh saiya huce baki shaba?

Ibtisam tace na koshi bana jin yunwa

Zarah tace Kai Kinji yanda yayi dad'i kuwa? Wlh kisha kiji

Ibtisam bata k'ara cewa komai ba, sannan bata d'auki faten ba, sai zama da tayi tana kallonsu Suna cin abincin suna fira .

Ummi kam ko kallon ibtisam batai ba, Illa faten ta da tayi tasha ,Tana fira da Zarah.

Bayan sun kammala, ana kiran sallah magrib duka suka tashi sukai ciki, domin yin sallah,

ibtisam na ganin ummi ta shiga d'akinta ta bita tana mata magana akan tayi hakuri da....

Ummi ta dakatar da ita tare da fad'in fitar min a d'aki sallah zanyi banda lokacin magana yanzu, ummi na fad'in haka ta shige toilet dan tayi alwala.

Ibtisam ji tayi kaman tayi ihu dan takaici, tare dayin data sanin amsan wayar da kabir ya bata tayi, lallai inda tasan hakan zai faru data maida mishi tun Farko, yanzu Allah kad'ai yasan Mai Abba zai Mata in Ummi ta fad'a mishi, "na shiga uku yau, wani hawaye ne ya zubo mata a ido Mai zafi tare da tunanin wani irin hukunci zata fuskanta yau wajan Abba in yaji wannan batun

Sai wajan 9 Abba ya dawo Gida, "tunda ibtisam taji ya dawo ta kasa zama, gaba d'aya a tsorace take, dan tasan yau ta shiga uku wajan Abba, "wani abun mamaki har wajan 11 Abba bai kirata ba, hakan yasa tace Ummi bata fad'ama Abba ba, ko kuma ta fad'a Mai yace babu komai, wannan tunanin da tayi shine yasa lokaci d'aya taji ta Fara jin yunwa, wanda sai yanzu ta tuna bata ci komai ba, wanda da bata jin yunwa din gaba d'aya, "fita tayi inda taga Abba a falo Wanda batai zaton zata ganshi ba, "yace mamana d'auko mun ruwa.

Tace toh Abba, "ibtisam dad'i ne ya cikata ta tabbata babu abunda ummi ta fad'ama Abba domin tasan inda ta fad'a Mai dasai ya Mata magana, "amma yanda ya Mata yanzu ya nuna mata babu komai hakan ya mata dad'i Sosai

Koda ta kawo ma Abba Ruwa, baice mata komai ba, harta koma kitchen ta d'auko abincinta ta nufi d'aki Abba na nan zaune a falo yana kallo.

Hakan yasa ibtisam yin bacci cikin kwanciyan hankali ba tare da shiga damuwa ba, ko tsoro ba, "Dan tasan Abba bai San komai akan wayar da uummi ta amsa ba

Washe gari da safe , koda ibtisam ta tashi ita ta d'aura abincin safe dan kawai ta faranta ma ummi duk da wani lokacin dama takan d'anyi mata.

Ibtisam doya dakwai tayi da tea ta dafa Lipton dasu citta da Kanin fari, sannan ta juye cikin flask, takai falo ta ajiye akan center table

Koda ummi ta fito ganin ibtisam ta Gama komai, yasa ummi cema ibtisam sannu da aiki?

Ibtisam tace yauwa Ummi Ina kwana?

Ummi tace lafiya kalau

Nan ummi ta koma d'aki Jim kad'an saiga Abba ya fito ya zauna ya faracin abinci, bayan ya kammala yace Ummi ta kira Mai ibtisam.

Ummi tace toh tare da kwala ma ibtisam kira.

Ibtisam amsawa tayi tare da fad'in na'am ummi gani nan, "bayan ibtisam ta fito falon gabanta taji yana fad'i domin irin kallon da taga Abba yana yi mata,.

Gaida mahaifin nata tayi, ya amsa fuska d'aure babu annuri balle wasa a cikinta

Zama tayi a kujeran dake kusa da ummi tace gani Ummi.

Ummi tace babanki ke kira, bani ba.

Abba ya jefo mata tambaya Waye Kabir?

Dam gabanta ya fad'i, tare dayin k'asa dakai, "Abba ya daka mata tsawa tare da fad'in ba dake nake magana ba? Waye Kabir nace?

Cikin in Ina tace mun had'u dashi ne, nida Granny ranan zamu kasuwa.

Abba yace shine ya baki waya kika amsa koh?

Kanta na k'asa tana hawaye

Abba yace Ina son kice Ina son ganinsa, aure dai kike so za kiyi ki kirashi kice Ina son ganinshi, tunda har kin iya had'uwa dashi ba tare da ya nemi izinin iyayenki ba.

Granny ce ta fito tana fad'in fad'a mata dai, gwara yazo asan abunyi, danni nafi son tayi auren akan wannan karatun, da bashi da wani amfani ko kad'an, in banda lalata wasu yaran da yakeyi, banga abunda yake tsinana musu ba wlh

Ibtisam ji tayi kaman tasa ihu dan takaici, yanzu shikenan na shiga uku, burina zai rushe, Innalillahi'wa inna ilaihirajiun "yanzu karatun da nayi buri shikenan zai tafi?

Abba yace mama Nima ban amince taje karatun ba, sai a d'akinta, domin taban mamaki, ba haka nayi zato ba daka gareta ba.

Granny tace Atoh dama tun tuni abunda nake k'okarin nunawa kenan, auran shine mafita, gwara Ayi tunda lokaci, kar nan gaba azo ana dana sani duk da bama Fata.

Abba kallon ibtisam yayi da kanta ke katsa dan takaicin yanda Granny ke k'ara zuga Abba din, "shi kuma yayi na'am da maganar ta d'ari bisa d'ari

Yace tashi kiban waje ki tabbata kin fad'a mishi ina son ganinshi, "mara tunani kawai

Tashi tayi simi simi kamar wacce kwai ya fashe mawa a ciki tayi cikin d'akinta, tana shiga ta

fad'a gado ta fashe da kuka gwanin tausayi.

Zarah rarrashinta ta farayi, domin duk Tana jin abunda ke faruwa.

Ibtisam kam kaman zugata akeyi, ba komai take tunani ba, sai yanda abba yace badai a gidansa zatai karatun ba, kenan aure zai Mata dagaske? Gaba d'aya ta shiga cikin damuwa tare da tashin hankali mara misaltuwa, domin Idan aka hanata wannan karatun an gama da ita Sosai, bata tunanin zata iya jura, kaman yanda bazata iya had'a karatu da aure ba

Zarah sai bata baki takeyi akan tayi hakuri insha Allah komai zaizo da sauk'i.

Ibtisam cikin kuka tace wani sauki Zarah, kina ji Abba yace in fad'ama kabir yana nemanshi

Zarah tace toh dan yace yana nemanshi shine wani abu? Kika san mai zaice ne? Ko an fad'a miki daka yaga Abba sai ace an bashi ke d'aure aure? Ko me?

Ibtisam dan tsagaitawa tayi da kukan da takeyi, tana nazari lallai maganan Zarah gaskiya ne, idan Kabir yazo yaga Abba koda ma yace ya fito nasan zai iya cewa ba yanzu ba, koda ya turo iyayenshi zai ce abba ya barni inna Gama karatu"wannan tunanin da tayi shiya bata karfin giwa tare dajin dad'i Tana Allah Allah gari ya k'ara haskawa ta kira kabir ta fad'a mishi Abbanta yana nemanshi...... Muje zuwa muga yanda zata kaya....

Read and leave it, dnt share to anyone

*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN

MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Wajan karfe 10 da wani abu saiga kiran kabir ya shigo cikin wayar ibtisam, da sauri ta d'auki wayan ganin kiran kabir ne yasata sakin murmushi tare da fad'in kaman yasan Ina son magana dashi, "tashi tayi da sauri tabar d'akin dan suyi magana.

D'aukan wayan tayi tare da sakawa a kunne tana fad'in hello.

Kabir yace Barka da Safiya, ina fatan kin tashi cikin koshin lafiya tare da kwanciyan hankali.

Tace uhm lafiya kalau, kaifa?..

Yace Nima haka Alhmdlh,

I just call to hear your voice my ibti, I really miss your face  and dat your smile

Murmushi tayi tare da fad'in yaushe na dawo? Harka Fara missing dina?

Yace Sosai kuwa, "nifa Inba gani Nayi ance yau an mallakamin ke a matsayin mata ba, toh bazan daina fargaba ba ko tsoro, wlh ibti a kullum Ina kwana da tashi tare da fargaba, da kuma tsoro cikin raina, kar ace wani ya kwace min ke "inko hakan ta faru ban San wani irin hali zan shiga ba,"Ina miki son da baki bazai iya fad'a ba, tunda nake ban taba son wata mace ba saike, "plz ibti karki yaudareni koki Bari wani ya canza miki ra'ayi akaina I really love you so much my ibti

Sonda nake miki shine yasa zanyi hakuri in jiraki ki gama karatu, badan komai ba sai dai hakan shine zaisa kiyi farin ciki, kuma hakan shine zai nuna miki cewa Ina sonki dagaske bada wasa ba.

Tace uhm nagode Sosai, sannan insha Allah bazan taba yaudaranka ba, duk rintsi duk wuya bazan taba juya maka baya ba, sai dai ban sani ba kasan kana naka Allah Na nashi,kuma na Allah shine dai dai.

Kabir yace wannan haka yake, tabbas kana naka Allah Na nashi

Ibtisam tace Abba yana son ganinka.

Yace ni? Ina fatan dai lafiya koh? Ba laifi nayi ba.

Ibtisam tace lafiya tare da fad'in Abba yaga wayan daka bani ranshi ya baci Sosai, ya kuma nuna cewa Ina son aure, wanda yace bazani karatun ba sai Nayi aure ku.... Sai kuma ta fashe mishi da kuka

Cikin tashin hankali ya fara rarrashinta tare da bata hakuri akan tabar kukan suyi magana.

Dakyar ta tsagaita dayin kukan tana shessheka

Yace my ibti plz tell me Mai yake faruwa?

Bata kulashi ba, sai sauke ajiyar zuciya da takeyi alaman har yanzu tana kukan

Yace my ibti cikin damuwa plz fad'amin inji komai ke faruwa plz plz

Tace Abba yace yana son ganinka, yace bana son karatu aure nake so, labarin abunda ya faru ta bashi

Kabir yace kiyi hakuri ibti Zanzo inga Abba sannan zan tabbatar dagaske nake son auranki, "Nasan bakya son kiyi aure yanzu sai kin kammala karatu ina sonki zanyi duk abunda kika ce "sai dai ina son ki sani ko ince zan ro'ki alfarma akan dan Allah Karki bari wani ya canza miki ra'ayi a kaina plz "ibti sonda nake miki yayi yawa idan na rasaki ban tunanin zan iya jura, "plz ki ri'ke min alkawari

Magana ta Fara cikin dashewan murya irin na wacce tayi kuka tace bazan taba yaudaranka ba, "domin Nima Ina Sonka.

Kabir jin tace Tana sonshi abunda bai tabaji ta fad'a mishi ba, "ido ya lumshe cikin jin dad'i.

Taci gaba da fad'in Nasan bakowa bane zai iya hakuri da abunda nace ba, nasai na Gama karatu inyi aure ba, na tabbata kana sona Sosai tunda har zaka iyamin wannan uzurin kum..... Sai kuma tayi shuru

Kabir yace inaji kuma me??

Tace ina jin tsoro Kar Abba yace bai yarda ba.

Murmushi yayi tare da fad'in karki damu, "amma ibti Indai kina sona dagaske inaga komai Abba ya yanke zakiyi na'am dashi, koda kuwa yace wannan satin zamuyi aure "bai kamata inga damuwa a tare dake ba, "karki manta Ina sonki kuma na fad'a miki tun Farko aure baya hana karatu.

Tace hakane aure baya hana karatu, "amma ni bana son in had'a Abu biyu aure da karatu nafi son in kammala karatun sai inyi auren

Ajiyan zuciya ya sauke tare da fad'in babu damuwa, ina sonki zanyi hakuri da duk abunda kika ce,"Zanzo jibi insha Allah inga Abba

Tace Allah ya kaimu

Ya amsa da Ameen tare dayi mata sallama, akan sai sunyi magana anjima

NAJEEB ne zaune akan gadon dake bedroom d'inshi, daka shi sai boxer babu riga a jikinsa, hannunshi ri'ke da kwalban alcohol yana sha, "turo kofar d'akin akayi wata yarinya ce ta shigo kallo d'aya mutum zai Mata ya gane balarabiya ce domin irin dressing din dake jikinta, jallabiya ne brown a jikinta sai k'aramin gyalen jallabiya din.

Nufan Najeeb tayi ta rungumeshi tana fad'in inata kira bakai picking ba.

Dan janyota yayi, Ido ya kura mata lokaci d'aya kuma ya sakar mata murmushin da yake k'ara mishi kyau, tare daja mata hanci "da sauri ta lumshe ido, "ganin haka Najeeb ya hura mata iska a fuska

Da sauri ta bud'e ido tare da sakar mishi murmushi tana fad'in I miss you Najeeb rabona dakai tun a Dubai wajan wata 10 fa kenan. "yanzu an kusa shekara

A hankali yace miye Abun mita ko korafi? Bayan kina tare dani yanzu?

Tace ina fad'a maka ne saboda na dade ban ganka ba, kuma Nayi kewarka Sosai da Sosai

Janyota yayi jikinshi tare da matseta Sosai, lokaci d'aya ya fara taba nononta da suke a mi'ke kuma a cike manya manya,"matsa mata su yake tare da murzawa babu abunda take sai lumshe ido tana sauke nishi sama sama, tare da kashe ido tana k'ara matse shi jikinta

Shiko Najeeb Sosai yake taba mata nonon domin yana matukar sonshi fiye da komai, musamman ya samu irin wanda yake so, manya gasu a tsaye, shi bako yaushe yake son yin sex ba, Indai zai samu nono ya taba yana wasa dashi, toh burinshi ya cika, wani zubin yakan biyema matan da yake hulda dasu ne dan yasan ya taso musu da sha'awa sai kawai ya biya musu bukata.

Dan sakinta yayi domin yaji k'aran wayarta dake ajiye akan gadon d'akin, kallon wayar yayi yaga an rubuta my love

Wani irin tureta yayi tare da tashi tsaye cikin bacin rai yace tashi kibar min gida

Tace Najeeb maiya faru?

Yace nace kibar min gida, and karki k'ara nuna kin sanni a rayuwarki, I hate cheaters.

Shuru tayi tana kallonshi cikin mamaki lokaci d'aya ta tuna da kodan Sunan da yaga ana kiranta da shine yasa yake ce mata cheater? Yes tabbas saboda shine "wani irin murmushi ta saki tare da fad'in Najeeb karka manta "am not your wife or your girlfriend am hare just to have fun me and you, "so miye Abun damuwa a ciki? Kodai kana sona ne? Tare da nufanshi Tana k'okarin tabashi.

Wani irin tsawa ya daka mata Wanda yasa gaba d'aya ta rud'e tare dayin baya da sauri danta tsorata Sosai dashi

Yace bana auranki, kuma bana sonki, so just leave from here tun Kafin in fitar dake dakai na

Cikin tsoro da yana yin daya sauya lokaci d'aya tace Najeeb "plz am so sorry plz, I don't mean to hurt you, wlh Najeeb ina Sonka da yawa nasan ba lallai bane dama kaika soni ba, sannan wannan kiran daka ga anyi min is my Mum let call her kaji.

Danna wayar tayi tare dayin dialing number din sai gashi mace ta d'auka

Kallon Najeeb tayi alaman kaji koh? Bana miji bane.

Najeeb sauke ajiyan zuciya yayi, domin a duniya ya tsana yaudara baya son yaga abunda yake Nema yana tare da wata, shi koda baya son Abun Indai nashi ne Toh baya son wani ya taba sai dai inya Bari

Bayan ta gama wayan ta nufeshi tana fad'in am sorry Najeeb, ina Sonka Sosai

Dan janyeta yayi jikinshi tare da bar mata bedroom din alaman har yanzu yana fushi da ita

Ido ta bishi dashi tana murmushi,lallai Ina son Najeeb, inda zai aureni da nafi kowa Sa'a, ji yanda ya nuna kishi a kaina, ido ta lumshe cikin jin dad'i.

Kabir yazo garin Kano, kuma a yau yace zaiga Abba domin suyi magana

Abba da kanshi yakai Zarah kaduna, domin an fara lecture, amma ita ibtisam ya hanata zuwa, taci kuka harta gode Allah

Yace aure take so kuma shi zatayi, "har mum saida ta kirashi amma yace tayi hakuri, domin ibtisam ta bashi mamaki, bai taba sanin tana kula wani ba saida ummi ta nuna mishi wayar daya bata ,"duk da Mama ta sani shima ya kamata ace ya Sani, "in saurayi zai dinga yima yarinya hidima haka ba tare da yaga iyayenta ba, ko ince ya turo magabatanshi ba, ya dinga

bata Abu Tana ansa ai dole iyaye suji tsoro, "kuma a haka Tana gabanmu Idan taje jami'a saiya kuma?

Mum dai taita bashi hakuri akan yabarta ta wuce skul domin lecture yana wuceta

Abba yace sai yaga yaron da take tare dashi, daka nan sai ya yanke hukunci akan abunda ya dace

Granny kam Murna takeyi sai faman zuga Abba take akan Ayi ma ibtisam aure yafi,.

Saboda takaici ibtisam ko kula Granny batayi.

Yau da daddare wajan karfe 8:30 saiga kabir shida wani Kanin mahaifinshi Sun hallara a gidansu ibtisam

An saukesu a falon ba'ki, inda Abba da wani Abokin shi suka tarbesu, domin ganin irin shigarsu Kabir din ya nuna ma Abba y'an gidan mutunci ne "wani abunda ya k'ara burge Abba da kabir din gaba d'aya ya'ki zama akan kujera a k'asa ya zauna, Abba yace tashi kahau kujera mana

KABIR yace a'ah Abba nan ya isa

Kawun Kabir addu'a ya fara sannan ya fara fad'in nine k'anin mahaifin Kabir, kwanaki ya Sanar dani Akwai yarinyar daya gani yana so, kuma yana son muje muga iyayenta.

Toh a lokacin nace mishi zanyi tafiya Amma inna dawo zanje insha Allah, bayan na dawo ban zauna ba, sai shekaran jiya nace ya kamata dai inzo, sai ga kiranshi akan ance in turo

Abokin Abba yace Allah sarki, dama abunda yasa muka bu'kaci ya turo saboda mu tabbatar dagaske yake ko wasa, domin mudai yarinya ta isa aure kuma auren za muyi mata

Kawun Kabir yace madallah, Abu yayi dai dai kenan ,domin muma abunda muke fama kenan, domin mutuncin mutum saida iyali

Abokin Abba yace hakane, kam gaskiya

Nan dai sukai magana, inda Abba Shima yayi magana akan aure Zaima y'arsa.

Inda kawun Kabir yayi magana akan su a shirye suke

Abba yace Toh Alhmdlh, nan dai suka k'ara gabatar da junansu.

Kabir yace Abba Ina neman alfarma.

Abba yace name?

Yace Abba Ina neman alfarma abar ibtisam ta tafi makaranta

Abba yayi shuru can yace kabiru zata makaranta amma a d'akinta domin nidai ba'a gabana ba

Jin haka yasa kabir yin shuru domin yasan tunda yace haka, bai kamata ya k'ara cewa komai ba, domin ba Abokin musunshi bane, ko kuma yana fad'a shima yana fad'a ba, "amma yaso abar ibtisam ta tafi makaranta

Nan dai suka tattauna inda sukai sallama akan zasu dawo bada dad'ewa ba

Koda kabir suka tafi, yana zuwa Gida ya kira ibtisam d'inshi

Bayan ta d'auka yace ibti yanzu na dawo gida daka wajan Abba.

Tace Sannunku da dawowa

Ya amsa da yauwa, sannan yayi shuru na wani lokaci, "Kafin ya fara magana ibti Abba ya'ki yarda akan maganan makarantar ki, yace sai dai kiyi a d'akin ki.

Itbisam hawaye ta farayi domin tasan tunda Abba yace haka, ko zata mutu bazai canza magana ba, shikenan yanzu zatai aure tare da karatu abunda batai taba tunani ba, gashi zai faru da ita yanzu.

Kabir yace ibti kiyi hakuri, sannan Ina son ki sani koda anyi auran ba gari d'aya zamu zauna ba, saboda karatun ki karki damu insha Allah auran bazai kawo miki matsala ba a cikin karatun naki ba

Ibtisam tasan bata da wani mafita yanzu Illa ta amince da auran kaman yanda Abbanta yace, yama zaman mata dole tunda ko taso ko bata soba, dole auren Abba zai Mata tunda ya furta bata da wani option

Kabir ya katse mata tunani da fad'in ibti just trust me, komai zai tafi normal, bazaki samu wata matsala a karatun kiba I promise insha Allah

Tace Allah yasa hakan shine alkhairi cikin muryan kuka

Kabir ya amsa da Ameen cikin jin dad'i, dan yasan tunda tace haka ta amince kenan" dan haka dole cikin satin nan ya turo a Gama magana, domin yana son inya turo a barta ta Fara skul Kafin Ayi auren duk da ba wani lokaci Mai tsawo yake son akai bikin ba, abunda zai kawo tsaiko danma bai k'arasa ginin da yakeyi ba, amma yanzu dole yaba Abun muhimmanci Ayi a gama ginin domin yasa ibtisam a ciki

Yace ibti yanzu sai in turo ayi komai saboda in nemi izinin ki koma makaranta koh?

Tace eh da sauri

Kabir murmushi yayi domin ya Lura da yanda take mutuwar son tayi karatu Sosai.

Kabir ya turo an kawo kud'in gaisuwa dana sadaki, duk da Abba baiso amsan kud'in sadakin ba saboda yace shi yafi son a bada ranan daurin aure, "da yake harda Dad cikin masu amsan kud'in shine ya amsa dubu d'ari na sadaki, inda aka tsaida wata biyar na auran ibti da kabir

Inda iyayen Kabir suka nemi alfarma a barta ta tafi makaranta.

Dad yace babu damuwa, ai tunda an amshi sadaki, shaidu Kawai muke jira yanzu.

Abba dai baice komai ba, Bayan iyayen Kabir Sun tafi Dad yace dama ba tafi skul ba?

Abba yace eh

Dad yace akan wani dalili? Kuma Zarah bata fad'amin ba

Nan Abba ya bashi Labarin abunda ya faru.

Dad yace Allah ya kyauta, yanzu dai saita tafi gobe, "koda yake dakai na zan kaita goben sai in wuce Nima

Tashi Dad yayi yana fad'in Bari inyi musu sallama Kafin in tafi inje in huta.....

Read and leave it, dnt share to anyone

*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Dad shiga yayi inda ya samu su ummi da Granny a falo suna fira

Dad yace Sannunku da hira?

Ummi tace yauwa, "tare da tashi tana fad'in bari in d'auko abinci

Dad yace A'ah ki barshi saida naci abinci Kafin nazo nan

Ummi tace kai waina ne, kasan abun marmari ne.

Dad yace a'ah Alhmdlh a koshe nake, gobe dai Zanzo da safe inyi breakfast a nan.

Ummi tace Allah ya kaimu ya nuna mana goben raida lafiya

Duka suka amsa da Ameen

Dad kallon Granny yayi tare da fad'in mama mun yanke lokacin bikin wata biyar

Granny gud'a ta saki tare da fad'in Alhmdlh, kai Allah na godema, "amma sai naga kaman an jashi da nisa Ina laifin wata d'aya ko biyu

Dad yace kabir din bai kammala ginin shiba, so yake ya kammala sai yasa aka kaishi har wata biyar din, "amma ai kaman yau ne

Granny tace hakane kam, Allah dai ya kaimu rai da lafiya

Abba yace ina ibtisam din?

Ummi tashi tayi ta kira ibtisam

Ibtisam fitowa tayi sanye da hijab a jikinta, "gaida Dad tayi tare da zama a k'asa kusa da ummi

Dad yace mamana Ashe baki tafi makaranta ba?

Bata bashi amsa ba, sai k'asa da tayi da kanta hawaye na son zubar mata

Dad yaci gaba da fad'in gobe ki shirya kayanki Zanzo wajan karfe goma sai in kaiki makarantar Kinji

Wani irin dad'i ibtisam taji har cikin ranta,zata skul gobe.

Dad ya k'ara kiran sunanta da ibtisam

D'ago kai tayi tare da fad'in na'am

Dad yace yau mun amsa kud'in sadakin ki gasu Naira dubu d'ari, "bazan baki ba yanzu sai ranan da aka d'aura aure zan mi'ka miki a hannunki domin naki ne

So abunda yana dakyau koda Kinje skul kisan an bada ke, shaidu kawai ake jira su shaida, dan haka saiki kame kanki banda rawan kai, kin San haramun ne neman aure akan aure, sannan mun tsaida lokacin bikin ki nan da wata biyar "Ina fatan kin gane?

Tace eh

Dad yace Allah yayi miki albarka, "saiki shirya gobe mu tafi da wuri "tashi kije ki Fara shiri.

Tashi tayi jiki a sanyaye tayi d'aki, koda ta shiga zama tayi akan gadon d'akin ta rasa mai takeji, dad'i ne ko ba'kin ciki.

Na farko Tana murna zata skul gobe na biyu kuma maganan aurenta Wanda ta rasa gane mai takeji, murna ne ko haushi, ita dai tasan danso Tana ma kabir, kuma shine zabinta ko tace shine burinta, dan tana mishi son so, wanda bazata iya misalta irinshi ba, "Lokaci d'aya tayi murmushi wanda tasan dole tayi hakuri ta saki jiki Koba komai auran kabir dinne zai bata daman ci gaba da karatu.

Bayan tafiyar ibtisam d'aki Abba ya kalli Dad "yace Aini banso ka amsa musu zata Fara zuwa makaranta naso sai an d'aura auren ta Fara a d'akinta, amma ba'a gidana ba.

Dad yace a'ah ba'a haka, akan wani dalili zaka hanata yin karatu Bayan yana da muhimmanci? Aini tun Farko ban San ka hanata ba, Aida nazo da kaina na kaita makarantar, ilimin mace yana da matukar muhimmanci a wannan lokacin K...

Granny tace nifa wannan karatun ba sonshi nake ba, amma tunda zatai aure ai hankali kwance,ni dama burina tayi auren tabar gidan, yarinya duk tabi ta tsufe a gida

Dad yace mama kwata kwata kwaya nawa suke yaran?

Granny tace ai dole kace haka, tunda kai dan boko ne.

Tashi Dad yayi yana fad'in Bari inje in huta sai gobe inna shigo, "tare da mi'ka ma Abba kud'in sadaki dana gaisuwa.

Abba yace a'a ka ri'ke a wajanka kawai

Dad yace OK tare dayi masu ummi da Granny saida safe, ya fita shida Abba domin ya rakashi

Ibtisam na kwance saiga granny ta shigo yana fad'in Amarya wajan kabiru bakya laifi

Tsaki ibtisam tayi domin haushin Granny takeji yanzu sai take ganin itace ta zuga Dad ya hanata zuwa skul, domin sanda yace bazata k'ara zuwa ba, taita zugashi akan tayi aure, "gashi dad ya biye mata

Granny tace kinma uwarki tsaki bani ba, y'ar banza

Shikam Najeen koda ya fita, zama yayi a reception tare da d'aura hannunsa akansa gaba d'aya ya rasa maike damunshi, tunda ibtisam ta shigo rayuwarshi Tana k'okarin ta canza mishi lissafi da tunani..

Gaba d'aya tasa yana abunda bayayi, Tana k'okarin kawo mishi damuwa cikin rayuwarshi, shi bai San miye tunani ba ko damuwa amma gashi yanzu ibtisam tasa ya fara wanda kwata kwata bayayi, kanshi yaji yana mishi ciwo, ciwon kai din Sosai dole tashi yayi ya koma ciki domin ya bukatar ya kwanta harya kusa zuwa kofar d'akin ya tuna da ya barta tana kuka sanda zai fita, tsaki yayi ya juya tare da kiran driver akan yazo su fita Dan baya son jin kukan nata ko kad'an

Ibtisam kam, bacci ta samu ya d'auketa

Najeeb bai dawo ba sai wajan 3 shima tunawa da yayi ya rufeta yasa ya dawo cikin sauri Bayan yayi mata siyayan abunda zata iya ci

Koda ya dawo ya ganta a kwance alaman tana bacci, sai yaji ta bashi tausayi a karo na farko, tare da fad'in yasan baccin wahala ne

Nufan gadon yayi Bayan ya ajiye Mata ledojin, zama yayi a kusa da ita tare da kallon fuskanta

ya kura mata ido sai yaga kaman tana kyarma..

Taba jikinta yayi da sauri yaji zafi Sosai, yace fever, a hankali ya kira sunanta da ibtisam

Tace uhm, sai a sannan ya gane ba bacci take ba,

Yace baki da lafiya ne??

Bata bashi amsa ba

Ganin haka yasa ya d'agota tare da kamota yana son sauketa akan gadon, yace muje hspt a dubaki

Ibtisam tace plz ka barni  I need only paracetamol, and food

Jin haka sai yaji ya k'ara jin tausayinta Sosai, ya tabbata tana jin yunwa Sosai

Yace OK ga waina nan na samo miki, zauna kici Bari inje in d'auko miki paracetamol a cikin mota

Zaunar da ita yayi tare da kawo mata ledar da aka saka take away, din waina din a ciki ya bud'e mata ledan kamshin wainar da taji yasa ta k'osa ta faraci ga kuma kamshin turaren najeeb din wanda take mutuwar so

ibtisam tun kafun yace taci ta faraci kaman mayya ci take Sosai,

Najeeb daya k'ura mata ido sai yaji ta bashi tausayi Sosai, lokaci d'aya ya nufi fridge ya d'auko mata Ruwa tare da fita danya d'auko mata paracetamol din tasha

Koda ya dawo gani yayi harta cinye kuma wainar Nada yawa, Abun mamaki ya bashi, nufanta yayi tare da bud'e mata maganin gudu biyu ya bata tasha, zata kwanta ya hanata tare da fad'in no tsaya kiyi kaman 10mnt saiki kwanta ba'a shan magani a kwanta

Ibtisam zama tayi lokaci d'aya kuma ta tashi, da ido ya bita ganin ta shiga toilet yasa ya kauda idonshi daka kanta, kwashe kayan da taci abinci tayi tare da sakawa a wata Leda ya fitar dashi waje

Koda NAJEEB ya dawo d'akin yaga Tana sallah, da alama sallah azahar take, tana cikin yi aka kira la'asar shima ji yayi yana son yaje masallaci yayi sallah a jam'i

Toilet din ya fad'a yayi alwala tare da fita Bayan ya rufe kofar

Ibtisam Bayan ta idar kwanciya tayi a wajan, yanzu taji dan dama dama zazzabin Ya fara sauka,

ba k'aramin dad'i taji ba da taci wainar daya kawo mata ba, taji dad'in wainar Sosai.

Najeeb ne ya shigo d'akin, ganinta a k'asa yasa shi fad'in lafiya?

D'ago dakai tayi ta kalleshi Wanda suka had'a ido su duka, itace ta Fara kawar da idonta gefe tare da sauke wani irin ajiyan zuciya

Najeeb ido ya lumshe tare da fad'in ya zaki kwanta a k'asa? Keda kanki kike janyo ma kanki ciwo, kina fever and you sleep on d floor

Ibtisam bata kulashi ba sannan bata tashi ba

Ganin haka yasa ya dauketa cak yayi gado da ita

Shima kwanciya yayi a bayanta, tare da janyota ya rungumota da hannunshi

Ido ya lumshe yana wani irin sauke ajiyan zuciya, gaba d'aya ya rasa maike damunshi....

Ita kam ibtisam batai kokarin matsawa ba, domin tana shakar kamshin turarenshi Wanda take cewa ya boye ne, tunda duk ta fesa turaren nashi amma bata ji kamshin ba, sai dai a jikinsa take ji, kuma daka ya shigo d'akin take ji ko inya matso kusa da ita

Gashi wani abun takaicin duk yanda taso ta mishi Abu, saita kasa indai taji kamshin turaren nashi ita da kanta tana mamakin irin sauyin ta, amma tabi bama kanta macijin ciki ke damunta shine yake sata take irin wannan mugun cin, wanda ya wuce misali

Lokaci d'aya ta kira sunan Najeeb

Yace plz allow me to slp

Tace magana zanyi and you must listen to me

Najeeb tashi yayi ya zauna tare da fad'in mai yasa bazaki banni in huta ba, and kinsha magani Kema plz slp Quickly and allow me to slp too

ibtisam tace uhm nifa inada lecture 4 gashi time harya wuce

Najeeb yace tunda Kema kin San time ya wuce so just keep quiet

Ibtisam tace toh yanzu mai kake nufi dani? Ko a nan zanyi ta zama?..

Najeeb murmushi yayi tare da fad'in exactly that is what am thinking

Ibtisam tace Hmmm, nidai Dan Allah ka barni in tafi

Najeeb yace ashe kin iya ro'kan mutum

Ibtisam tace uhm I can apologize Indai zaka barni, inma kana son I should go on my kneel and apologize I can do it, indai zaka barni in tafi I will do what ever you ask

Kallonta yayi tare da fad'in saboda kije ki dinga hulda da maza right????

Da sauri ta kalleshi tare da nanata Kalman hulda da maza as how??

Najeeb tashi yayi tare da fad'in I tell you I will never allow you to go to that skul har sai naga kinyi ciki.....

Ido ta zaro waje tare da fad'in ciki? Gabanta taji ya fad'i gaba d'aya hankalinta ya tashi ita sai yanzu tama tuna da sex din da yayi da ita zata iya samun ciki.... Innalillahi'wa inna ilaihirajiun kodai cikin ma gareni?? Ina yawan Kwadayi tare da cin abinci anyhow gashi 2month kenan banga period d'ina ba.....

Dira tayi akan gadon tare da fad'in dan Allah NAJEEB Ina son inje hospital ayi min test

Kallonta yake cikin mamaki, lokaci d'aya yace test??? Wani irin test??

Tace plz najeeb bani da lokacin bayani I need to see a doctor plz najeeb Ina son ganin dr dan Allah sai kuma tasa mishi kuka tare da nufanshi ta ri'ke mishi hannu Tana fad'in NAJEEB ka taimaka ka kaini hospital na shiga uku, Allah ba Ameen ba, wayyo Allah na..

Najeeb yace ibtisam maike damunki? Cikin damuwa yake mata maganan

Tace najeeb ina cikin wani hali bazan iyayi maka bayani ba, idan abunda yake tunani ya tabbata Wlh bazan yarda domin kabir.....

Wani irin tureta yayi daka jikinta tare da sha'ko mata wuya yace how dare you.....

Shuru yayi na wani lokaci kafin yace how many times did I warn you not to call his name in front of me???. Tell me how many times did I warn you..... Lokaci d'aya kuma yayi shuru tare da fad'in wait you say you want to go and see doctor for a test and kince bazaki yarda ba Indai abunda kike tunani ya faru what did you mean? And you are calling dat stupid guy name

Ibtisam shuru tayi tana kuka

Najeeb jijjigata yayi tare da fad'in mai kika aikata keda shi?????

Jin tayi shuru yasa ya sakar mata wani Mari cikin tsana tare da fad'in tell me...... Shuru yayi lokaci d'aya yana kallonta hannunshi yasa a kai tare da fad'in no wander but koma miye we should go and see doctor right now for a test....... Janyota yayi yana k'okarin bud'e kofa ya tsaya lokaci d'aya ya waigo ya kalleta, ganin kayan jikinta yasa ya sakar mata hannu tare da komawa ciki ya d'auko mata d'aya daka cikin jallabiyoyinta ya jefa mata a fuska alaman tasa

Ibtisam jiki a sanyaye ta d'auki jallabiyan taja shiga toilet tasa tare da wanke fuskanta wanda ya kumbura musamman ta wajan daya mareta

Koda ta fito ganinshi tayi yana kaiwa da komowa a d'akin, ganin ta fito yasa yaja hannunta sukai waje

Kai tsaye Mota suka shiga inda driver yaja su, yace ma driver kaimu asibiti dake kusa and plz drive fast.......

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Ibtisam hawaye kawai takeyi, Ita ba komai bane yake damunta sai dai kar ace tana dauke da ciki, cikin kuma na NAJEEB, wani irin kuka mai sauti ta Saki Wanda bata san tanayi ba

Najeeb wani irin kallon tsana ya mata tare da juyar da kanshi gefe, yana fatan kar Allah yasa abunda yake zargi ya tabbata

Kallon driver yayi cikin zafin rai tare da fad'in I said you should drive fast, kana tafiya a hankali

Driver k'ara ma motar gudu yayi na fitan hankali, gashi yana gudu amma shi ogan nashi baya ganin saurinshi Wanda shi driver din a tunanin shi ibtisam ce bata jin dad'i, shi yasa yake son suje asibitin da sauri musamman daya jita tana kuka

Koda suka k'arasa wani asibiti private hospital ne wanda Kai tsaye Najeeb na fita ya fito tare da jan hannunta sukai ciki, kai tsaye reception suka nufa inda suka bud'e Kati a receptionist, Kai tsaye aka sadasu da Dr

Koda suka shiga najeeb yace ma dr din yana son Ayi mata test....

ibtisam tayi sauri ta Katseshi tare da fad'in Dr plz kamun da sauri ina bukatar sanin Mai yake damuna cikin kuka take maganan

Dr yace maike damunki?

Najeeb yace Dr pregnancy test zaka mata right now, infact ma kawai ka mata scanning

Dr yace OK tare da fad'in ibtisam ta tashi bayan ya kira nurse yace ta rakata wajan scan Bayan yayi rubutu a wata paper ya bata

Najeeb na nan zaune ibtisam suka fita, jim kad'an sai gasu sun dawo, tashi NAJEEB yayi yana fad'in mai result ya nuna???

Nurse tace sai kun jira, bada dad'ewa za'a baku ba

Dr Ya cabe da fad'in wannan ne first samun cikin madam right?

Najeeb shuru yayi itama ibtisam shuru kawai tayi tare da fargaban Kar Allah yasa ciki gareta, domin idan shine lallai ta cutu, shikenan NAJEEB yayi Nasara akanta, shikenan karatu na, burina ya tafi kenan a Banza

Bud'e kofar akayi aka shigo inda nurse dince cikin Fara'a ta mi'ka ma Dr result din..

Amsa Dr yayi inda ya fara dubawa, lokaci d'aya yace congratulations matarka Nada cikin sati tara.....

Zumbur NAJEEB ya tashi tare da fad'in what 9week how many months kenan??

Dr yace wata biyu da sati d'aya, an Tana bukatar hutu, infact ma kar kayi sex da ita na sati b.....

Najeeb yace ya isa plz dr

Ibtisam kam sumar zaune tayi tana nanata Kalman cikin zuciyarta, congratulations matarka tana da cikin sati 9..... Lokaci d'aya ta saki ihu tare da fashewa da kuka tana fad'in Dr plz a zubar min da wannan cikin plz Wlh ban shirya haiyuwa ba yanzu....

Najeeb wani irin kallon tsana ya mata wanda idonshi ya kad'e yayi ja, gaba d'aya baya gane komai, wani irin abune ya tokare mishi a kirji Jan hannunta yayi ya figeta suka fita, direct Mota ya shigar da ita inda ya kalli driver yace muje hotel

Koda suka k'arasa hotel din bama driver din key din d'akin yayi tare da fad'in Jeka kwaso komai nawa dake d'akin kazo mu wuce kano

ibtisam da sauri ta kalleshi tare da fad'in ka barni in tafi wlh zubar da cikin nan zanyi domin Wlh bazan bari in ha......

Wani irin gigitaccen Mari ya sakar mata wanda saida yasa taga stars tare da fad'in you better keep quiet, wannan cikin da kika kwaso dole sai kin haifeshi, wlh koda zaki mutu sai kin haifeshi

Ibtisam da tasha Mari ga ciwon kai na yunwa dake damunta, shiru tayi tana ganin jiri jiri

Driver ne ya dawo tare da masu aikin hotel din da suka tayashi kwaso kaya ciki harda wayan ibtisam da suka bashi ya watsa mata wayar

Hanya suka kama inda NAJEEB yama Dad d'inshi message akan su kamo hanyar kano urgent plz shida Mum, yana tura mishi message din ya kashe wayar gaba d'aya domin a halin da yake baya jin zai iya d'aukar wayar kowa yanzu

Driver hanya ya Kama, inda yake ta sharara gudu, ibtisam bata komai sai kuka, ita burinta Wannan cikin ya zube shine burinta

Sun isa kano inda suka tarar su Dad na nan cikin tashin hankali, domin tunda Dad yaga message din NAJEEB gabanshi ya fad'i Wanda hakan yasa suka biya jirgi wannan shine yasa suka rigasu zuwa gidan

Dad cikin damuwa yace NAJEEB maiya f....

Ganin ibtisam na kuka fuska a kumbure Dad yace Mamana maiya sameki??..

Ibtisam batai magana ba sai kuka granny tace ke maiya faru ne haka??

Najeeb yace Dad ciki gareta and kuma ba nawa bane

Gaba d'aya salati suka saki cikin tashin hankali

Granny tace Kai Mai ya faru ne Wai??

Mum ta kalli Granny ta fad'a mata abunda yace

Granny tace na uban Waye inba naka ba? Shege a Kai ma yarinya budurwa amma kace tana da ciki ba naka ba??

Najeeb wani irin kallo yake watsa ma Granny domin yana jinta sai dai ba komai yake ganewa ba, and bazai iya maida Mata ba

Dad yace Toh NAJEEB inba naka bane na Waye??

Yace Dad na saurayinta KABIR

Ibtisam da sauri ta kalli NAJEEB cikin mamaki tare da nanata Kalman daya fad'a

Abba shuru yayi amma ranshi gaba d'aya a bace yake da ibtisam kenan irin abunda ta aikata kenan, duk irin tarbiyan daya bata shine ta bama kabir kanta Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, lallai ibtisam ta cuceshi, yanzu abunda ta aikata kenan??

Dad yace mamana Kinji abunda mijinki ya fad'a cikin harshen turanci yake maganan domin kowa yaji, ciki Granny ce kawai bata ji.

Ibtisam cikin kuka tace Wlh Dad nashi ne b.....

Abba cikin zafin rai ya tashi yakai Mata Mari tare da fad'in k'arya za'a miki da kike fad'in cewa nashi ne? K'arya zai miki? Mutuniyar banza irin abun kunyar da zaki d'auko mun kenan?? Abba sarkewa yayi wanda ya fara tari da sauri ummi taje ta Kawo mishi Ruwa yasha yana sauke numfashi sama sama.

Kowa dake d'akin sannu yake mishi, inda Dad yake fad'in mai yasa Zaka bugeta, komai fah a hankali ake tafiyar dashi

Abba yace Wlh da akwai abunda yafi duka saina Mata, inda badan Kar in bata lahira na ba da

wlh saina kasheta..

Granny tace wai miye kuke ta Yaren da bana ganewa?? Gashi naga harda duka, ku fad'amin maike faruwa inji

Mum ta fad'ama Granny abunda ya faru

Salati Granny ta saki tare da fad'in shi kabirun yayi mata ciki?? Sai kuma ta saki kuka

Ibtisam dake kuka domin gaba d'aya ita Abun ya d'aure mata kai, ita bata da laifi kuma ciki na NAJEEB ne bana kabir ba, ita tsakaninta da NAJEEB shine kiss kawai shima sau d'aya.....

Dad ne ya Katseta tare da fad'in mamana Kinji abunda mijinki yace??.....

Ibtisam cikin kuka tace Wlh Dad cikinshi ne, wlh nashi ne bana kabir b....

Najeeb ya Katseta tare da fad'in keep quiet duk abunda zaki fad'a bazan amshi wannan cikin ba, domin bani nayi ba and Wlh bazanyi accepting ba, you must punish for it I.....

Dad yace NAJEEB ka mana shuru banso in k'ara jin maganan ka, har sai na baka izini

Najeeb yace Dad akan wani dalili zanyi shuru? Kana ji tana k'okarin had'ani da d'anta na shege Wanda bani Nayi ba, dad shekaran jiya kawai wani abu ya taba shiga tsakani na da ita tunda mukai aure....

Ibtisam cikin kuka tace Wlh ba sau d'aya bane, yafi.....

Najeeb yace yaushe na taba kulaki?? Oh is all my fault nine naja ma kaina da har na yarda nayi wani abu dake, dole Kimin sharri inda Nasan haka kike da ban had'a jikina da wannan k'azamin jikin naki ba, crap.......

Dad yace kai NAJEEB kana da hankali kuwa?? A gaban mu kake irin wannan maganan???

Najeeb yace Toh dad in Banyi ba, kana ji tana k'okarin turamin d'anta na shege da tayi, wlh Dad duk inda zamu je I will not accept this Bastard unborn child din

Abba wani irin tukukin ba'kin ciki ya tsaya mishi a wuya, domin komai najeeb ya fad'a ibtisam taja, lallai koshi bazai yarda da dan wani ba a gidansa

Ummi kam hawaye take tare da takaicin abunda y'arta ta jawo musu

Dad ya kalli ibtisam yace ibtisam ki fad'amin ya akai kika aikata hakan? Mai yasa kika aikata hakan??..

Ibtisam tace Allah shine shaida na wlh ban taba aikata zina ba tunda nake, Nayi kokari na kame kaina daka fad'awa dattin zina, Dad Wlh na kame kaina har zuwa gidan miji.....

Najeeb yace wani mijin?? Ina fatan badai niba

Dad yace NAJEEB Idan ka k'ara magana wlh saina saba maka

Shuru yayi yana tsaki k'asa k'asa alaman nifa bazanyi shuru a cuceni ba

Dad ya kalli ibtisam tare da fad'in ina ji ibtisam

Tace Dad lokacin da kuka kaini America Bayan kun tafi NAJEEB yayi min wannan Abun...... Kuka yaci karfinta Sosai alaman tana jin nauyin abunda zata fad'a

Dad yace ibtisam muna sauraranki

Ibtisam kuka take Sosai, ta kasa magana.

Abba yace bazaki magana ba? Saina ballaki

Najeeb yace tana tunanin k'aryan da zata had'a ne

Dad yace ibtisam ki fad'a mana abunda ya faru

Ibtisam taci gaba da fad'in Bayan kun tafi wata rana ina kitchen ya shigo mukai cacan baki inda na gudu d'aki tun daka ranan ban k'ara ganinshi ba, saida akai wajan kwana biyu sai gashi shida wata mace inda na bu'kaci ya ...... Kuka ta kuma saki, lokaci d'aya ta basu labarin abunda ya faru....

Gaba d'aya salati suka saki

Najeeb Kam tashi tsaye yayi yana fad'in Karya take mishi baiyi sex da itaba ranan

Abba tashi yayi tsaye cikin zafin rai tare da fad'in najeeb da gaske kana shan alcohol??

Najeeb shuru yayi ba tare daya bama Dad amsa ba, Dad ya daka mishi tsawa tare da fad'in ina maka magana dagaske ne kana shan alcohol

Najeeb Kai ya girgiza tare da fad'in no Dad Nasan wine ta gani ta d'auka alcohol ne..

Ran Dad ya baci Sosai akan cewa da ibtisam tayi NAJEEB yana shan alcohol, kenan sharri tayi mishi

Ibtisam tace wlh Dad dagaske ne y.....

Dad yace ya isa ibtisam, akan wani dalili zaki ce mijinki nashan alcohol??

ibtisam kuka take Sosai tare da d'auko wayarta ta nuna musu hotan giyan

Dad kallon NAJEEB yayi tare da fad'in wannan miye Toh??

Najeeb yace ni ban San inda ta samo shiba, Dad so take ta kulla min sharri akan in amshi dan daba nawa ba, and wlh Dad bazanyi accepting yaron ba koda kuwa Mai zai faru

Dad yace nima bazanyi Supporting ka amshi Yaron da ba naka ba, dan haka dole mahaifin Yaron ne zai amshe shi....

Abba ranshi ya baci akan abunda Dad yake fad'a kenan ya nuna NAJEEB ne Mai gaskiya ibtisam kuma Mai Karya, inbai manta ba sanda ta dawo daka America Al yaga ciwo a goshinta har ummi take fad'a mishi granny tace tayi mishi gardama ne yasa yayi mata da karfi, sannan yanzu bayanin da ibtisam ta bada ya k'ara tunawa da Abun...

Granny ce ta Katse Ma Abba tunani tare da fad'in wai mai yake faruwa ne,??

Dad ne ya mata bayani tare da fad'in mama sai kusa ta, ta fad'i uban Yaron wanda yayi mata cikin??

Abba yace bai kamata ka kama maganan gefe d'aya ba, ya kamata Ayi bincike Kafin a yanke hukunci

Dad yace babu wani bincike domin na yarda da abunda najeeb ya fad'a duba da sharri da ita ibtisam take k'okarin yi mishi, akan yana shan giya, yau inda ibtisam ba y'arka bace dasai Nayi karanta akan tayi mishi kazafi akan yana shan giya....

Granny tace kumin shuru cikin kuka tare da fad'in akan yaranku kuke son ku bata zumuncin ku, Bayan duka baku zurfafa bincike ba wlh ko kaffara bazanyi ba wannan cikin NAJEEB ne, domin na yarda da ibtisam

Dad yace mama Nima na yarda da NAJEEB bai taba min k'arya ba tunda nake dashi....

Mum tace taya zaka fad'i haka, karka manta duka namu nesu NAJEEB da Ibtisam din S....

Dad ya dakatar da mum tare da fad'in enough, ya isa haka, idan ke baki yarda da d'anki ba Toni na yarda dashi dan haka dole ibtisam ta fad'i Wanda yayi mata ciki

Abba wani irin hawaye ne ya zubar mishi a ido cikin kunci da ba'kin cikin abunda Dan uwanshi yake fad'a Wanda bai taba expecting ba, amma babu komai laifin y'arshi ce domin shima bawai ya gama yarda da maganan ibtisam din bane

Najeeb kallon ibtisam yayi tare da fad'in zan fad'ama duniya abunda kika aikata I will make sure you regret abunda kika min cheater, lallai saina hukunta ki yanda bakya zato

Ibtisam tace babu abunda zakamin domin duk inda zamu ciki naka ne, kuma kaine ubansa

Najeeb yace OK zansa kiji kunya, sannan zansa kowa ya yarda ke mazinaciya ce domin kin aikata zina kin shigo gidana da cikin wani

We will move to America tomorrow for DNA test

Ibtisam tace babu inda zan bika domin bana kaunar koda da minti biyu ne In k'ara ganin fuskanka..

Najeeb dariya yayi tare da fad'in same with me, domin even me bazan zauna da mace fasi'ka ba, "Al dole kice ba zaki bini ba Domin gudun abun kunya ba

Ibtisam murmushin takaici tayi tare da fad'in OK zanje but Ina son ni dakai muyi yarjejeni akan Idan muka je akai gwaji Indai cikin ya tabbata naka ne zan zubar dashi.....

Najeeb yace ki zubar mana who care?? Nidai Nasan ba nawa bane and bazai taba zama nawa dinba har abada

Ibtisam ta kalli iyayenta dake kallonsu ko wanne ranshi a jagule tace Abba ka yarda dani wlh cikin nan nashi ne wlh Abba Nayi k'okarin ri'ke mutunci na n.....

Abba yace ya isa haka, koma dai mai nene idan akaje akayi gwajin komai zai bayyana....

Najeeb kallon abba yayi tare da fad'in duka su bashi password d'insu domin tare zasu tafi duka ciki harda Granny

Abba yace a'a basai yaje ba, sannan ummi itama ba zata ba, kawai su suje

Najeeb yace OK tare da kallon Dad yace Dad na tafi hotel sai goben

Dad yace muje tare Muma hotel zamu tafi

Fita sukayi Bayan sunyi musu sallama

Koda suka isa hotel NAJEEB gaba d'aya kasa bacci yayi tare da kosawa subar k'asar domin

suga karshen wannan Abun, ya tabbata cikin ba nashi bane. . Lokaci d'aya kuma yayi shuru yana nazari tare da tunanin abunda ibtisam din tace ranan da abun ya faru.... Lokaci d'aya ya girgiza Kai tare da fad'in no ba haka bane k'arya ta fad'a da Najwa nayi sex ranan gaba d'aya kawar da tunanin ma yayi tare da cire Abun a ranshi, sai dai wani abun mamaki ya kasa bacci sai juyi yake......

Ta gefen ibtisam kam tashi tayi ta shiga daki tana kuka, kiran zarah ne ya shigo cikin wayarta k'in d'auka tayi domin bazata iya magana ba.

Itama wani abun takaicin kasa bacci tayi domin son kamshin turaren najeeb din taji tana sonyi, duk yanda tayi danta sama kanta tsanar son jin kamshin amma ta kasa, jin kanta na ciwo wanda ta tabbata yunwa ne yasa ta tashi dakyar

Granny da itama ta kasa bacci sai juyi takeyi itama, itama Abun duk ya isheta

Granny tace ina zaki??..

Ibtisam tace yunwa nakeji, zani kitchen Inci abinci

Granny tace zoki zauna in dibo miki Kinji

Ibtisam zama tayi akan gadon d'akin

Granny tashi tayi ta fita Jim kad'an sai gata da abinci da Ruwa ta Kawo mata

Ibtisam amsa tayi domin ganin dambu ne na cous cous, ci take Sosai kaman wacce bata taba ganin abinci ba.

Granny kallonta take cikin tausayi domin ita in kowa bai yarda da ibtisam ba, ita ta yarda da ita domin tasan ko wacece ibtisam din, tasan halinta, zata iya cewa ko Ummi data haifi ibtisam bazata kaita sanin halin ibtisam din ba.

Ta tabbata cikin na NAJEEB ne bana wani ba, in kowa zai karyata ita bazata karyata ba, koma dai miye y'ar nune zata nuna Idan aka haifi yaron koda ba'ayi gwaji ba

Ibtisam ajiye plate tayi tare da gyasa alaman ta koshi, ganin kallon da Granny take mata yasa tace Granny Kema baki yarda dani bako??

Granny tace ko d'aya ibtisam ba haka bane, kawai Ina mamakin Abunne, ni nasan cikin NAJEEB ne, domin Nasan koke wacece, sai dai abunda yake bani mamaki da kika ce yana shan giya

Wani hawaye Mai zafi ya fito Mata, tare da fad'in Granny Idan Nayi mishi sharri Riban Mai

zanci???

Granny Wlh abunda na fad'a shine gaskiyan magana, amma koma dai miye za'ayi gwaji a gani Idan akayi DNA test za'a gane ko jinin Waye AI

Granny tace taya za'a gane Bayan yaro bai fito duniya ba???

Ibtisam tace za'a gane, kawai jinina ake bukata, sai nashi su za suyi gwajin su gane jinin na Waye

Granny tace ikon Allah kaga Abu iri iri dai a duniya

Ta gefen Mum kuma koda suka k'arasa ta Fara fad'ama Dad abunda yayi bai dace ba, domin abunda yayi ya nuna yana Bayan NAJEEB ne, kuma hakan bai dace ba, domin Wlh ni nafi yarda da maganan ibtisam din

Dad yace koma dai Mai zaki fad'a ni na yarda da NAJEEB, akan wani dalili zata kirashi da mashayin giya?? Wato ke baki ji komai ba akan an kira d'anki da mashayi ba koh???

Mum tace gaskiya kayi babban kuskure da ka yarda da NAJEEB, Bayan ko daka irin halin shi, ya kamata ka yarda cewa zai iya shan abunda yafi giya Indai akace yanayi, karka manta ko irin yanda najeeb yake......

Dakatar da Mum yayi tare da fad'in ya isa haka plz, I trust my son, so ban son wata magana plz koma dai miye gobe zamu tafi gaskiya zata fito and ina tunanin tunda basa son juna is better a raba auren

Mum salati ta saka tare da fad'in Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, Mai kake fad'a haka?? Kana nufin akan d'anka har zaka iya yarda kayi fad'a da dan uwanka?? Ko kasan wannan abunda kakeyi zai iya Kawo rashin fahimta kaida k'anin ka? Yanzu kai saboda yaran da kuka haifa saiku yarda su raba muku zumunci K....

Dad ya Katseta da fad'in sai me?? Akan mai yasa bazai rabu da ita ba, Bayan tana binshi da sharri akan wani dalili zai zauna da ita??

Mum shuru tayi, lokaci d'aya tace ina guje maka abunda zaisa kazo nan gaba kana dana sani

Yace babu dana sanin da zanyi domin Nasan NAJEEB komai yayi zai fad'a Dan haka kibar wannan maganan ki barni in kwanta In huta

Mum shuru tayi tana mamakin yanda mijin Nata yadau zafi, ita bata ga abun d'aukan zafi ba, ita a yanda take kallon NAJEEB komai akace zaiyi zata yarda, domin su da kansu suka lalata rayuwar d'ansu da kansu, yaro sun D'aukeshi sun kaishi waje karatu ba tare da mai kwaba

mishi ba, ai dole suga ba dai dai ba

Washe gari wajan karfe 9 tayi masu NAJEEB a gidansu ibtisam, koda suka zo ,Ummi ta Kawo musu abinci

Mum ce kadai taci amma shi Dad yaci abinci

Najeeb kam baici komai ba haka kawai yaji baya son cin abincin domin gaba d'aya baya cikin nutsuwa, Ummi kiran ibtisam tayi wacce ta fito cikin jallabiya tare da yafa k'aramin gyalen jallabiya din wanda yayi mata kyau Sosai

Najeeb tunda ta fito ya kura mata ido Lokaci d'aya ya kauda kanshi tare da jan gajeran tsaki

Ibtisam kam wani irin dad'i taji, domin tana shigowa kamshin turaren shi taji wanda ya sata nishad'i

Gaida su Mum tayi cikin girmamawa

Dad ya amsa babu yabo babu fallasa

Mum tace ibtisam sannu ya jikin naki??

Ibtisam tace Alhmdlh

Najeeb yace Dad mu kama hanya 10 jirgin zai tashi

Gaba d'aya tashi sukayi, suka fita cikin masu tafiyan harda Granny yau zata Ameka

Koda suka k'arasa airport suka shiga jirgi granny dai ba wannan bane farkon shigarta jirgi ba, kar kuji batai kauyanci ba Hhhhh

Bayan kowa Ya gama shiga jirgi ya d'aga zuwa America koda suka sauka Kai tsaye mota suka shiga inda NAJEEB yace shifa bai yarda aje Gida ba sai an fara zuwa anyi DNA test din hakan ko akayi

Suna tafiya a mota domin zuwa asibti Granny tace oh ikon Allah kalli yanda suke yawo kaman tsirara Kai dole mutun ya lalace idan yazo wannan k'asar Wlh, jiba wannan Abun kunyar har Ina fisabilillahi

Mum dariya tayi tare da fad'in Granny aisu ba musulmai bane, sannan Idan bakai wannan shigar ba su gani suke baka Waye ba

Granny dake zaune sanye da riga da hijab tace kenan ni sai su koreni daka k'asar kenan

Mum tace a'a sai dai ka zaman musu abun Kallo

Granny tace Allah shiryesu

Mum ta amsa da Ameen

Ita kam ibtisam bama jinsu take ba, ita burinta aje Ayi gwanin ta samu ta zubar da cikin kowa ya huta hankali kwance

Koda suka k'arasa asibitin ba tare da bata lokaci ba akama Dr bayani akan abunda suke bukata, nan aka d'iba jinin ibtisam aka d'iba na NAJEEB tare da fad'in sai nan da kwana biyu result zai fito

Nan sukayi gida Kai tsaye, suna isa Dad yayi kitchen domin Ruwa yake bukatar sha

Mum kam ciki suka shiga inda ibtisam tace d'aki d'aya zasu zauna da Granny hakan ko akayi

Gaba d'aya ibtisam bata fita koda falo ne, abinci sai dai Granny ta Kawo mata daki,balle yanzu da komai taci sai tayi amai bata ma cika ciba sai taji kanta na Mata mugun ciwo shine zata ci Dan dole shima tana gama ci sai amai gaba d'aya ta kosa result ya fito a cire mata cikin ta huta da wannan wahalan

Najeeb kam gaba d'aya baya zama a gidan tunda suka zo, domin aiki yayi mishi yawa sosai

Ibtisam tana d'aki zaune bata son jin komai sai kamshin turaren najeeb, ganin ba samu zatayi ba, yasa tasa kuka Sosai kaman ranta zai fita Dan takaici gashi gobe ne result zai fito, gashi gaba d'aya taga lokaci baya gudu

ibtisam na nan zaune taji kamshin turaren NAJEEB, da sauri ta d'aga Kai suka had'a ido, wani irin murmushi da bata san ya fito ba ta saki tare da sauke wani irin ajiyan zuciya

Najeeb wani irin kallo ya mata tare da fad'in gobe result zai fito you better tell them the truth tun kafin lokaci ya k'ure kiji kunya

Ibtisam tashi tayi tare da kallonshi tace najeeb nasan bazanji kunya ba, domin Nasan ban aikata abunda kake tunani ba am sure kaine zakai dana Sani

Wani irin shu'umin murmushi ya saki tare da fad'in we shall see tomorrow

Wani irin kallo ya watsa mata tare dayin gaba Zai fita har yayi nisa ya kusa fita, da sauri ta kira sunanshi da fad'in najeeb plz wait

Tsayawa yayi cak  ba tare daya waigo ba

Nufanshi tayi tare da zuwa gabanshi tana fad'in dan Allah kaban..... Sai kuma tayi shuru alaman tana jin nauyin fad'an abunda take son cewa

Gira ya d'aga mata tare da fad'in zaki fad'amin Waye kwarton naki ne???

Ibtisam baki ta cije alaman taji zafin abunda ya fad'a amma saita basar tare da fad'in turaren ka nake son ka bani plz wanda kake sawa....

Ido ya kura mata yana kallonta lokaci d'aya kuma ya saki murmushi tare da d'aure fuska yace shi d'an iskan da yayi miki cikin nashi baiyi miki bane???

Ibtisam tace plz ka bani ban son dogon magana plz

Najeeb wani kallo ya k'ara watsa mata tare da fad'in kije uban cikin naki ya baki shi saurayin naki

Cikin bacin rai tace OK zanje ya bani amma ina son ka sakeni sai in koma waj......

D'aga hannunshi yayi zai mareta alaman bacin rai ga idonshi da yayi ja, lokaci d'aya ya sauke hannun tare da cije baki ya fita fuuuu.

Bai dad'e da fita ba, sai gashi ya Kawo mata turare wajan Kala 8, tare da watsa mata akan gadon d'akin

Har zai fita ibtisam tace babu shi a ciki wanda kake sawa shi nake so, dan Allah ka bani ka tausaya min ka bani sai kuma ta saki kuka......

Plz kuyi manage zazzabin mura ya kamani dakyar nayi wannan

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

NAJEEB waigowa yayi tare da kallonta, yanda take kuka, "duk Da yana jin haushinta Sosai yanda take kukan sai yaji ta dan bashi tausayi kad'an

Tashi tayi tazo inda yake tare da fad'in Wanda kasa a jikinka shi nake so, wanda nake jin kamshin shi yanzu tana maganan ne cikin kuka

Ido najeeb ya k'ara kura mata yana mamaki, lokaci d'aya kuma yayi murmushi tare da fad'in heey enough stop making and excuse da zaki dinga zuwa kusa da inda nake, kina wani kina son perfumes d'ina, gashi na baki sai me kuma? Mai kike so kuma???  Tell me what do you want?? Inma kina wannan Abunne danna tabaki you are mad,..... Yeah sai yanzu na fahimta kina manne min Dan inyi sex dake right wani irin dariya ya saki tare da fad'in that is your problem Nigerians girl, kuna da naci, nacin ku yayi yawa, ga jaraba daya muku yawa, small rat like you shine kike son Wai Kimin taku da dabara tare da k'arya Wai kina son turare ne, na baki turaren kinzo kince babu shi a ciki, saboda ba turaren kike bukata ba, ni kike bukata me, just come out and say it ni kike bukata, cije lips d'inshi yayi tare da d'an murmushin ba'kin ciki wanda zuciyarshi bata komai sai tafarfasa da zugi tare dajin takaicin abunda ta aikata, tazo mishi gida da cikin wani....

ibtisam ce ta Katse mishi tunani da fad'in najeeb ban taba tunanin inyi wani abu dakai ba a rayuwa ta, amma sai gashi ka cuceni kayi min abunda har in mutu bazan manta ba, kayi min irin abunda ko.... Sai kuma tasa kuka tare da fad'in ka cuceni.....

NAJEEB yace or nine na cuceki??  You are mad infact you are stupid, let me tell you something, ko sanda Nayi sex dake Nayi regretting duk da shima kena taimaka domin naga kina bukata, and I try to help you cos naga kin Fara fita out of control..... Shuru yayi sannan yace "But....

Shima shurun ya kar'ayi yana kallonta sannan yace 'you cheat me kin Sa Nayi sex dake da dattin wani k'ato a cikin ki, you cheat me and I will never forgive you, I will make sure to make your life miserable, I will make you regret what you did to me... Ibtisam I hate you I so much hate you I never hate person in my life like the way I hate you, kinyi min babban laifi a rayuwa and kin fake da abunda nake aikatawa kina son Yimin sharri, kince nasha alcohol Nayi sex dake..... Shuru yayi tare da lumshe ido Lokaci d'aya kuma ya bud'e idon tare da fad'in why me? Why? Mai yasa kika zaba ki cutar dani? Mai yasa tun Farko baki fad'ama parent d'inki kinyi sex da wani ba, sai yasa kika shiga shock sanda akace saurayinki yana da HIV..... Shuru yayi tare da dafe Kai yace oh my god I have to do HIV test.... Kallon ibtisam yayi tare da fad'in duk da ance bai dashi I will go for HIV test domin ban yarda dashi ba, and Ina jira gobe yayi kowa yaga result at that time zanyi punishing d'inki zanyi miki abunda baki taba expecting ba, just wait and watch, Allah ya kaimu gobe..... Fita yayi Fuuuuu tare da barin gidan wanda su Mum suma basa nan sun fita harda Granny

Ibtisam k'asa tayi tana kuka tare da Alla wadai da wannan auren da aka mata, lallai NAJEEB ba miji bane, lallai an cuceta Wlh, an d'aura mata mashayi Wanda bai San darajan Dan Adam ba, Wanda baya mutunta kowa, gashi yanzu yayi mata ciki yana fad'in ba nashi bane, wlh Idan har result ya fito dole in zubar da wannan cikin, ibtisam wani irin tsanar abunda ke cikin Nata takeji Domin tunawa da cewa jinin najeeb ne a cikinta, lallai zata iya aikata komai a yanda take jin kanta yanzu domin taga wannan cikin ya zube, dan bazata iya yarda ta had'a zuri'a da NAJEEB ba, kuka take sosai tare da tsanan kanta da tun Farko da akai Mata auren Mai yasa bata gudu ba

NAJEEB kam Kai tsaye hospital ya nufa inda ya bu'kaci a mishi HIV test a dubashi ya gani wanda dama yanayi every 6month amma wannan karan lokacin daya kamata yayi bai kaiba, yazo a dubashi dan kawai yayi sex da ibtisam Wanda yake tunanin tana da HIV kabir ya saka mata, shi gaba d'aya bai yarda da kabir d'inba duk da ance mishi baida shi sharri aka mishi, domin najeeb a duniya in aka cire ibtisam babu wanda baya kaunar ya gani kaman KABIR din, wanda tun farkon ganinshi da ibtisam din yaji guy din gaba d'aya baiyi mishi ba, yaji ya tsani kabir, musamman da yake ganin yana zuwa wajan ibtisam Wanda yake ganin kaman ya bada maza, domin yana zuwa wajan karamar yarinya wacce bata kaiba.... Lokaci d'aya najeeb yayi tsaki tare da fad'in ai dole ya nace mata kullum sai yazo munafuki Ashe yasan abunda ya kunsa mata, Bari gobe yayi in tabbatar Wlh sai nasa an d'aureshi

NAJEEB na nan zaune har aka bashi result d'inshi yaga negative alaman bai dashi, ido ya lumshe tare da barin hospital din, koda ya fita gidan ya koma direct inda ya tadda har yanzu su mum basu dawo ba, tsaki yaja tare da nufa d'akinshi ya shige tare da rufe kofar d'akin

Kallo d'aya zaka masa ka gane yana cikin tashin hankali tare da kunan rai, domin gaba d'aya inda mutum zai ganshi daka jiya zuwa yau, zai gane yana cikin tashin hankali har wata y'ar rama yayi na kwana d'aya, gaba d'aya tunanin abunda ibtisam tayi shike mishi yawo a Kai, ji yake kaman ya hadiyi zuciya ya mutu dan ba'kin ciki, wai matar da aka d'aura mai itace tazo da ciki Kai Wlh an cuceni, ganin kanshi yana mishi ciwo saboda tunani yasa ya tashi ya d'auko

kwalban alcohol d'inshi wanda ya boye a wardrobe d'inshi saboda Kar iyayenshi su gani, ya fara sha, najeeb gaba d'aya Wanda ya rage baida yawa domin ranshi a matukar bace yake, idonshi yayi ja gashi yanda yake shan alcohol din duk ya zubar mishi a jiki, tashi yayi yana ganin jiri tafiya ya farayi wanda baya cikin hayyacinshi balle yaga inda yake son dosa, bugewa yayi da wardrobe d'in d'akin Wanda hakan yasa ya fad'i ya fara bacci a nan

Ibtisam kam gaba daya kanta taji yana mata ciwo tare da jiri, wanda tasan ba komai bane yake damunta sai yunwa, ga kuma tunani Wanda ta tabba inda za'a gwada jininta za'a fad'a mata cewa yahau Sosai, lallai yau lokaci baya mata sauri ita yanzu burinta gobe yayi kowa ya gane itace keda gaskiya tasa a zubar da cikin ta koma skul ita wannan shine burinta kawai

Granny ce ta shigo d'akin ta ganta tana rusgan kuka, granny tace ibtisam, "lafiya kike wannan kukan kaman wanda akace wani naki ya rasu??..

Ibtisam rungume Granny tayi tana kuka tare da fad'in Granny Wlh wannan cikin ya isheni, ya takura min gaba d'aya yasa na kasa samun sakat, ga ciwon kai ga son kamshin turaren da bazan samu ba, Wlh Granny Ina cikin wani hali na gaji na gaji...... Kuka ta kuma fashewa dashi wi wi wi wi

Granny shafa mata baya ta farayi alaman tana rarrashinta tayi hakuri, granny Tana jin tausayin ibtisam jin kukan nata take har cikin ranta, domin tana son ibtisam Sosai

Granny tace ibtisam kiyi shuru Kinji fad'amin sunan turaren da kike so, zan saka a si..... Shuru Granny tayi tare da fad'in a'ah ga turare can na gani da yawa, babu wanda kike so a ciki??

Ibtisam tace Granny babu irin wanda nake so, ni wanda nake so baya ciki

Granny tace toh ya sunan wanda kike so??

Tace Granny ni wanda n..... Sai kuma tayi shuru tana kuka

Granny tace zoki zauna Kinji

Zama sukayi sannan granny tace fad'amin inji

Ibtisam tace ki barshi kawai Granny

Granny tace Allah ya kyauta, yanzu dai gashi, Leda taba ibtisam tare da fad'in gashi nan na siyo miki

Amsa ibtisam tayi tare da bud'e ledan Tana kallon abunda ke ciki, kayan fruit ne a ciki, ibtisam tace Granny mai yakon ki kai kitchen.

Tashi ibtisam tayi tare da fad'in Bari inkai kitchen

Granny itama Tashin tayi tace muje, Kai tsaye falon suka nufa inda suka ga Dad a falon, ibtisam gaida dad tayi

Amsawa yayi cikin sakin fuska tare da fad'in ya jikin naki??

Tace da sauk'i Alhmdlh

Kai tsaye kitchen ta nufa inda taga mum na aiki, ibtisam tayi ma mum sannu da aiki

Mum ta amsa tare da fad'in Granny ta baki kayan fruit koh?..

Ibtisam tayi murmushi tare da fad'in eh ta bani gashi nan, ajiye kayan fruit din tayi tare da d'aukan carrot ta Fara kankare ma mum

Mum tace a'ah Kinga barshi kije ki huta

Ibtisam tace a'ah Mum zan iya

Ganin yanda ta dage yasa Mum barinta domin ta tayata din duk da ba wani aiki bane, Sosai

Mum sunayi Tana d'an jan ibtisam da fira, domin ta lura ibtisam din kaman tunani yayi mata yawa, tana son ta cire komai a ranta domin ta sake dan haka Mum tai ta janta da fira, Sosai

Ibtisam tun bata sakewa harta dan saki jikinta da Mum, suna cikin aiki taji Tashin zuciya da gudu tayi waje tare da nufa d'akinta inda tayi toilet ta fara kwarara amai mai d'aci, gaba d'aya idonta ya firfito ga kwalla dake zubar mata a ido, Wanda yasa kanta taji ya k'ara mata wani uban ciwo

Mum ce ta shigo cikin toilet din tana mata sannu tare da taimaka Mata ta wanke jikinta.

Ibtisam ji tayi jijiyar kanta na Mata ciwo Sosai, kaman zai fito yanda yake buga Mata da karfi

Koda suka fito daka toilet din zaunar da ita mum tayi akan kujeran d'akin tare da fadin kwanta ki huta, mai zan Kawo miki domin ki Washe bakinki dashi???

Ibtisam da sauri tace abinci amma ban son wanda aka saka curry ko cinnamon

Mum tace toh Bari inje kitchen din in Kawo miki, amma saina dafa miki wani wanda ba curry din, bari in Fara baki fruit kisha Kafin in Kawo miki abincin Kinji?..

Ibtisam Kai ta d'aga mata alaman toh

Fita Mum tayi saiga granny itama ta shigo Tana mata sannu

Ibtisam amsawa take da yauwa, ibtisam tana kwance tana tunanin lallai duk Wanda bai girmama iyayenshi ba yayi Asara, jiba irin wahalan da take sha, kullum cikin ciwon kai Mai tsanani......

Mum ce ta Katseta data Kawo Mata fruit, tashi tayi ta amsa ta Fara sha kamar mayya yanda take sha kaman wani zai kwace mata yasa Mum murmushi tare da fad'in Bari inje in duba abinci ,fita Mum tayi ta barsu da granny

Ibtisam ta kalli Granny tace wai Granny Mai yasa daka naji yunwa sai kaina ya fara ciwo Sosai, daka naci abinci saiya daina, anjima kad'an kuma sai Kai din ya fara ciwo Sosai inna kuma cin abinci saiya saina, wlh Granny na gaji da irin wannan cin da nakeyi, so nake in daina, koda yake daka gobe ma shikenan

Granny tace shikenan me?? Ai shi dama ciki ko wanne yana zuwa da irin nashi yanayin, ke naki na ciwon kai ne, zai daina nan gaba k'adan, wata fah ita inta samu ciki kullum a kwance zaki ganta bata iya tabuka komai, wata kuma ta Dinga kwanciya a asibti kenan, wata kuma zaki ganta garau, sai dai ciwo jefi jefi da kwadayin masu ciki, ke Kinji dad'i ma kamshin turare kike so, wasu fah warin toilet suke zuwa su shak'a sannan suke samun nutsuwa K.....

Ibtisam tace Allah ya kyauta, warin toilet? Tabdi jam, Aiko Wlh bazan iyaba kam

Granny tace Kedai kar kice haka, domin dan dai ke naki ba irinshi bane, amma sanda zaki je ki shinshina zaki sani ne?? Aiba sani za kiyi ba kawai dai ayi sha'ani

Ibtisam tace uhm, ni gobe Idan aka bada result zan rabu da wannan cikin in huta

Granny tace saboda kina hauka koh??

Ibtisam tace shikenan granny kiyi shuru kawai amma nifa sai Nayi abunda Nayi niya

Granny shuru tayi tana kallonta, tare da fad'in Allah dai ya kyauta

Ibtisam ta amsa da Ameen tare da ajiye fruit din ta kwanta

NAJEEB sai wajan magrib ya tashi inda ya tashi ya shiga toilet gaba d'aya komai dake ranshi yaji ya fita, duk wani damuwa yaji baya tare dashi yanzu, sai dai kanshi da yaji ya mishi nauyi Sosai

Koda ya fito daka wanka, sallah yayi a gurguje eh a gurguje domin yanda yake sallah din zai nuna maka cewa kaman yana sauri ne, Hmmmm Allah dai ya kyauta, duk saurin mutum idan

yana sallah nutsuwa akeso yayi domin yana tare damai badawa ne gaba d'aya wato Allah mahaliccin komai da kowa, Toh saurin Mai mutum zaiyi kuma, Bayan yana gaida Mai badawa da hanawa

Koda ya idar fita yayi direct inda ya nufi falo yaga babu kowa a ciki dan haka waje yayi inda ya shiga motarshi ya figa, wani hotel ya nufa inda ya kira wata number tare da fad'in am in the hotel just come to room 106 tare da kashe wayar yana sakin gajeran tsaki

Ba'a wani dad'e ba akai nocking

Tashi yayi daka shi sai gajeran wando yaje ya bud'e kofa NAjwa ce ta shigo cikin d'akin tare dayin hugging d'inshi tana fad'in my guy I miss you so much

Tureta yayi daka jikinshi tare da fad'in ina jinki, akan mai kike ta kirana haka?? Yana mata maganan ne cikin fad'a

Najwa ganin haka yasa ta saki kuka tare da fad'in haba NAJEEB tun daka Dubai nazo just kawai to see you, amma kalla irin tarban da kamun, haba NAJEEB

Tsaki yaja tare da fad'in did I invite you??.

Shuru tayi tana kallonshi tana hawaye, lokaci d'aya tace no but NAJEEB I...

Yace enough, kin riga kin bani amsa, so you can go..

Jin haka yasa ta tsugunna da sauri tare da kama kafarshi Tana bashi hakuri tana kuka tare da fad'in najeeb nasan kana fushi dani ne, saboda na'ki zuwa hspt akan in duba wannan yarinyar, plz am so sorry Nasan baka sona but ni Ina Sonka kishin ka ya hanani zuwa, and NAJEEB Nasan ba wani abu bane yasa ka damu just kawai because you sleep with her that is the reason da kake son inje in......

NAJEEB Ya Katseta tare da I sleep with her?? Are you mad how dare you say that

Najwa tace eh najeeb you have sex with her, domin ranan da kayi da ita kasha alcohol, Nima nasha and naga sperm ga kuma kayanka a kitchen daka watsar nan ta Fara fad'a mishi irin abubuwan data gani wanda zai gamsar dashi akan yayi sex da ita, ita Najwa tana fad'a mishi ne domin ya yafe Mata sannan yasan cewa dan tayi kishin ibtisam ba laifi

NAJEEB zama yayi a kan gadon d'akin tare da daura hannunshi akai yana tunani, lokaci d'aya ya d'ago ya Kalli Najwa tare da fad'in kina nufin ranan ba da ke Nayi sex ba

Najwa cikin kuka tace eh bada ni kayi ba, da ita kayi sai kuma ta saki kuka dan yaji tausayinta.....

NAJEEB ya daka mata tsawa tare da fad'in keep quiet and tell me everything

Nan Najwa ta Fara fad'in najeeb Wlh da ita kayi bada niba, kaga dole inyi kishi.

Najeeb da sauri ya Fara saka kayanshi tare da d'aukan key din motarshi

Najwa ta rungumoshi Tana fad'in najeeb Ina zaka kuma

Tureta yayi tare da fita yabar d'akin hotel din, inda ya nufi waje Kai tsaye motarshi ya shiga ya tada gudu yake yana tafiya Kai tsaye hospital din da yakai ibtisam ranan da abun ya faru yaje

Koda yaje direct wajan Dr din ya nufa inda ya bu'kaci yasan maiya faru da ita sanda ya Kawo ta

Dr yace bazai iya fad'a mishi ba, domin bai San miye halakan ta dashi ba.

NAJEEB cije lips d'inshi yayi tare da fad'in she is my wife I need to know everything about her and plz Dr tell me ranan tafiya ne ya kamani urgent kasan aiki na dole in tafi..

Dr dakyar ya yarda ya fad'ama NAJEEB abunda ya faru da ita, tare da ce mishi anyi mata fyad'e ne, nan najeeb ya tashi tsaye cikin mamaki tare da fita yabar hospital din gaba d'aya tuk'i yake cikin tashin hankali kenan shine yama ibtisam ciki ranan da yasha alcohol yayi sex da ita and bai mata da wasa ba, kenan yaji Mata ciwo tunda har an gane anyi raping d'inta ne, kai ya dafe wanda ya taka burki da sauri ya tsayar da motar, kanshi ya d'aura akan motar yana fad'in that mean na zargeta akan abunda bata aikata ba? Kenan she is virgin nine nayi dis virgin d'inta ba tare da sanina ba, oh my god what should I do??

Wani iri yaji tare da tausaya ma ibtisam din yanda ya zargeta ba tare data aikata wani laifi ba kaman yanda yake zargi ba, lallai yayi babban kuskure...... Dan shuru yayi lokaci d'aya kuma yace banda laifi coz kowa ye as my position zaiyi zargi, domin Tana yawan kiran that stupid guy, komai na Mata is her fault, lokaci d'aya kuma ya tuna da gobe ne fa za'a amsa DNA test din da akayi, a hankali yace no I won't let that tin to happen jan motar yayi da gudu Kai tsaye gida ya shiga

Ganinsu yayi su duka a falo amma banda ibtisam

Nufan Dad d'inshi yayi Yana fad'in Dad Ina son magana plz is urgent let me go and call ibtisam, gaba yayi ba tare daya jira ansa daka mahaifin nashi ba

Granny ta kalli mum tare da fad'in lafiyanshi kuwa?? Naga yana sauri kaman ance mishi wani nashi ya bata

Mum tayi dariya tare da fad'in Bari muji Mai zai fad'a yace dai zaiyi magana damu

Granny tsuke baki tayi tare da fad'in ja'iri komai zai fad'a oho

Ibtisam na kwance a d'aki, aka budo kofar da sauri ta tashi domin kamshin turaren da taji tasan bana kowa bane saina NAJEEB

Aikam tana Waigawa ta ganshi tsaye, shima ita din yake kallo

Sunanta Ya kira da fad'in ina son magana dake a falo wajan su Mum

Ibtisam bata bashi amsa ba, sannan bata kulashi ba

Ganin haka yasa najeeb K'ara nufanta tare da zuwa gab da ita, yana fad'in am talking to you

Ibtisam har wani lumshe ido take saboda kamshin turaren nashi

Ganin ta'ki kulashi yasa ya kamo mata hannunta tare da janyota jikinshi yana fad'in am try to help you daka jin kunya, so muje falo muyi magana

Ibtisam k'okarin jan jikinta tayi daka nashi amma ya k'ara matsota tare da fad'in don't try to move muje muyi magana a falo..

Ibtisam tace bana bukatar yin wata magana da kowa, bana son jin wata magana, sannan bana son wani taimakon ka, kawai kaje

NAJEEB wani irin murmushi yayi tare da fad'in, you must listen to me, either you like it or not, look young girl stop all this nonsense and fallow me, in baso kike na barki da abun kunya ba

Ibtisam wani irin kallo ta mishi tare da fad'in abun kunya?? Miye abun kunya??

Yace wannan cikin naki da kika shigo gidan auranki dashi..

Ibtisam murmushin takaici tayi tare da fad'in Wlh ko kad'an ba Abun kunya bane, ni nasan wannan cikin baida uba sai Kai gobe.....

Najeeb ya Katseta tare da fad'in sai yasa nake son Nayi accepting cikin tunda kin li'ka min shi, ya zanyi? Dole in rufa miki asiri tunda na aureki, bazan so duniya suyi Alla wadai dake ba, ace matar aure taje da cikin wani gidan miji wannan Abun kunya ne in our society  not even in our society in our religion is a big sin....

Ibtisam wani irin kallon tsana ta watsa mishi tare da fad'in, Abun kunya??? Who care?? I don't care cos Nasan ni Banyi Abun kunya ba, ni yanzu banda lokacin ol this maganan gobe kawai nake jira, domin ka tabbatar da abunda ka aikata cikin Maye and daka gobe wannan cikin tare

da nuna cikinta, zan cireshi ka.....

NAJEEB cikin bacin rai yace don't you ever try to tin of abortion

Ibtisam tace wlh Wlh na rantse da Allah saina zubar da wannan cikin Koba a cikin wannan k'asar ba, Bari kaji koda zai jamin matsala I will do it sai Nayi abortion, domin bazan haifa ba, and kace ba naka bane so ina ruwanka???

NAJEEB yace ibtisam Wlh Idan kikai mistake cikin nan Ya zube..... Shuru yayi tare da lumshe ido sannan ya cije lips d'inshi, lokaci d'aya ya bud'e ido tare da fad'in I will show you how evil I am, akan wannan cikin zan iya miki abunda sai kinyi regretting zuwanki wannan duniyar.

ibtisam tace do your worst, ciki babu wanda ya isa yasa in Haifa tunda bana bukatar hakan

NAJEEB yace ni Ina bukatar hakan and dole ki haifa yazo wannan duniyar ko k'in k'i ko kinso, is better kima daina wannan shirmen, ni Ina son yaron Zan rik'eshi and Treat him or her like my own child

Ibtisam dariya tayi tare da fad'in like your own child?? Funny to dama na Waye inba naka ba

NAJEEB yace whatever inma kince nawa ne koba nawa bane nidai is non of my business, d only tin I know or I should say I Want you to knw shine dole ki haifa wannan cikin kuma mu Raine Shi me and you

Ibtisam tsaki taja tare da zama akan gadon d'akin

Da sauri ya d'agota tsaye tare daja mata baki yana fadin don't try it again I hate it

Ibtisam jan jikinta tayi daka nashi tare da k'okarin zama da sauri ya rukota tare da tsayar da ita ya jata sukai falo inda su Mum suke zaune

Yana ri'ke da ita, yayin da ita kuma take k'okarin jan jikinta daka nashi

Mum tace najeeb ya kake janta haka? Karka manta ba ita d'aya bace

Jin haka yasa ya saketa tare da fad'in mum na Kawo tane saboda taki yarda tazo muyi magana

Ibtisam ita dai shuru tayi tana kallon k'asa tare da fatan Allah ya kaisu gobe zata ba NAJEEB mamaki Wlh, saita nuna mishi Iyakar shi

Da sauri ta tashi tsaye tare daja baya tana fad'in ka tashi ka fita, domin na tsani ganinka a r....

Janyota yayi tare dasa mata hannunshi a bakinta ya toshe mata baki, ya fara fad'in ibtisam you have to listen to me

Ibtisam tirje tirje take domin tana k'okarin ta kwaci kanta daka ri'kon da yayi mata

Ganin yanda takeyi yasa ya saketa domin tunawa da abunda Dr yace akan cikin zai iya fita

Bayan ya saketa hawaye ya Fara zuba a idonta inda ta Fara fad'in najeeb na tsaneka har abada bazan taba Sonka ba, wlh even for a minute ban son ganinka, plz am begging you just stay away from me...

Lokaci d'aya idonshi ya kad'e domin a duniya ya tsani wannan Kalman Nata, yanda take nuna

Mai kiyayya, yace ibtisam am your husband so dole inzo inda kike

Tace you are not my husband, najeeb..... Sai kuma tayi shuru tana kuka...

Kokarin matsawa yayi ya kamota tace don't touch me.....

Ido ya bita dashi tare da kallonta

Ibtisam tace najeeb am not your wife karka manta ka sakeni..... Oh na manta how will you knw that u divorce me?? Tunda kana cikin Maye.....

Ina tayaka murna ka rabu da enemy din'ka and Nima Ina taya kaina...... Kuka yaci karfinta

Shi kam NAJEEB gaba d'aya d'auke wuta yayi data furta Mai Kalman cewa ya saketa Bayan yasha giya, wani irin sarawa yaji kanshi yayi,.... Lokaci d'aya magananta ya fara mishi yawo a Kai wanda take fad'in am not your wife don't touch me...... Kenan alcohol d'in da yasha last a America shine ya furta Kalman ya saketa?? Tunawa yayi a ranan ya ganta kaman bata da lafiya.....

Kallonta yayi tare da kamota ya rungumota yace ibtisam plz don't tell anyone akan cewa na rabu dake bazan iya barin Uwar d'ana ta auri wani ba, plz just for our child keep this as Secret......

Da sauri ta tureshi tare da fad'in ni inada ilimi Nasan abunda nakeyi, sannan nasan abunda Allah ya hana da kuma wanda Allah yayi hani dashi, lallai Kai tarin laifin naka kullum k'aruwa yake Bayan manyan laifin da kake aikatawa shine kake Son k'ara wani? Lallai babu komai a ranka sai duniya baka tuna Allah inda kana tuna Allah Wlh bazaka fad'i haka ba, ni ba irin matan da kake bi bane, ni nasan abunda nakeyi kuma daka yau kar I.....

Yace enough ibtisam komai zai faru am still your husband and keep this on your mind yana fad'in haka ya fita Fuuuuu

Ibtisam kam ganin najeeb ya fita ranta wani irin tafarfasa yake mata, da sauri ta d'auko ledan maganinta Wanda aka bata a hspt ta bud'e su duka maganin suna da yawa ta watsa a bakinta ta shanye su duka, tana murmushi tare da fad'in nasan tunda nasha wannan maganan wannan cikin zai zube and daka ya zube shikenan kowa ya huta.......

Kabir ne zaune a office yana danna system d'inshi wayarshi ce tayi K'ara, alaman kira yana shigowa, d'auka yayi ya duba ganin Sunan hafsat yayi akan wayar

D'auka yayi tare da sawa a kunnenshi yace madam ya akayi??..

Ta gefenta tace lafiya, when zaka dawo??

Yace did you miss me ne??.

Murmushi tayi tare da fad'in alot I really miss you, and I cook your favorite food....

Tun kafin ta k'arasa yace oh I have told you, ki daina shiga kitchen kina bama kanki aiki, but baki ji abunda nace ba, kina son wahalar min da baby

Hafsat tace am sorry, kasan Mai irin Lalura na ana son ta dinga yin aiki yanda inta tashi haiyuwa zaizo mata da sau'ki

Yace but nidai banso, tunda baiyi kwari Sosai ba, and gani nan zuwa right now

Tace OK

Bayan sun kashe wayar kabir murmushi yayi domin duk wannan Abun da yakeyi yana yine domin kar Allah ya kamashi and yasan yanzu ibtisam tayi aure shima dole ya sauke hakkinshi dake kansa akan matarshi, amma so d'aya ne yaba ma ibtisam har yanzu yana Sonta Sosai, sai dai yakan ro'ki Allah akan ya cire Mai Sonta ya amshi tashi kaddaran amma Abun mamaki kullum kaman Sonta K'ara k'aruwa yake a cikin ranshi, har tausayin hafsat yake yanda take nuna Mai kulawa amma shi gaba d'aya zuciyarshi baya wajanta ko kad'an

Har yanzu zuciyarshi bata cire mishi cewan zai samu ibtisam ba, sau da yawa yakan k'okarin ya cire tunanin ta in yanayi amma ya kasa sai yasa yake keeping kanshi busy saboda baya son bata lokaci wajan tunani

Lokaci d'aya ya tashi tare da fita kai tsaye waje yayi inda ya nufi wajan motarshi ya shiga ya tada..... Tuk'i yake yana lafiya wani Mota ne yake ta mishi horn alaman ya tsaya

Kaman bazai tsaya ba, lokaci d'aya ya faka tare da fitowa, inda motar itama ta faka a gaban nashi

Wani mutumi ne ya fito cikin motar kiran golf inda ya nufi kabir din ya bashi hannu suka gaisa

Kabir yace lafiya??

Mutumin yace ai yau wajan kwana biyu inata so in ganka amma Allah baiyi ba, domin ina son fad'a maka wani abu mai muhimmanci tare da k'ara fad'a maka kayi a hankali akan mutanan da kake hulda dasu, and mutane ba Abun yarda bane, wanda bakai expecting ba sai yaci

amanarka, wanda bakai tunani ba shine yaudaranka ya munafunceka....

Kabir ya Katseshi tare da fad'in wai maike faruwa ne plz fad'amin mai nene???

Mutumin yace nine wanda naje ranan daurin aurenka nace kana da HIV......

Kabir ru'ko mutumin yayi idonshi ya canza Kala..... Lokaci d'aya kuma ya saki mutumin tare da fad'in kasan Mai ka aikata kuwa!? Kasan irin laifin daka aikata kuwa?? Ka cuceni ka batamin rayuwa, har yau Ina fama da dakon son ibtisam......

Mutumin yace kayi hakuri KABIR Wlh nima sani akayi, ba komai bane ya kawo ni face in fad'a maka gaskiya domin Nima Wanda ya sani aikin ya yaudareni yaci amanata......

Yace KABIR wannan aikin ba kowa bane ya sani sai abokin ka Tahir

Kabir yace Tahir??

Wani irin kallo yama mutumin tare da fad'in karka kara mishi wannan k'azafin domin har abada Tahir bazai taba min wannan Abun ba.....

Mutumin yace Allah sarki, haka masu kyakyawan zuciya suke dama, kuna da saurin yarda, gashi ana saurin cin amanarku, Wlh Allah d'aya ne koh?? Toh Wlh Tahir yasa ni saboda yana son yarinyar, ya Turani inje ince kana da HIV domin in an fasa auren shi yace tunda hakane zai aureta sai akai rashin Sa'a go slow ya rik'eshi a hanya har aka d'aura auren yarinyar da wani

Wanda haushin wannan Abun yasa ya hanani sauran kud'in aiki na, da naga haka shine nace Zan fad'a maka gaskiya domin mu irin mu bamu da amana indai Mun ri'ke amana Toh ka bamu hakkin mu

Dan haka saika kiyaye dashi, yana fad'in haka mutumin yayi gaba abunsa

Kabir kam gaba d'aya wani irin dum yaji a kansa mamaki yake Tahir taya Tahir zai mishi haka!?? Lallai inko ya tabbata shi dinne yaci amanarshi, domin a yanda ya d'auki Tahir duk yanda yakai da son Abu Indai yace yana so zai bashi amma...... kai hannu ya d'aura a kanshi tare da lumshe ido yana jin wani irin jiri

Dakyar ya samu ya bud'e motarshi ya shiga inda ya figa da gudu Kai tsaye office din Tahir ya nufa koda ya shiga

Tahir yace a'a angon hafsat

Kabir zama yayi tare da kallon Tahir yace Mai yasa kamin haka Tahir??

Tahir yace mai ya faru??

Kabir yace Mai yasa ka zama silan da yasa aka fasa aurena da ibtisam??

Da sauri Tahir ya tashi ya fara in Ina.....

Kabir ganin haka yasa ya tabbatar shi dinne, dan haka yasa yace Tahir kaci amanar amintaka inda ka d'aukeni yanda na d'aukeka bazaka min haka ba, just saboda kana son ibtisam Wlh ni nasan Ina son ibtisam but a yanda nake jin abokantakar mu zan iya hakura, but kaci amanata but babu komai is part of experience

Tahir yace KABIR Dan Allah kayi hakuri Wlh Sharrin shedan ne, daka baya Nayi nadama, musamman da ni ban sameta ba kaima baka sameta ba, Nasan tun sanda na ganta naji Ina sonta Wlh Sharrin zuciya ne kawai tare da shaidan dan Allah kabir kayi hakuri kar wannan Abun yasa ya zama silan abunda zai had'a zumuncin mu....

Kabir yace babu komai haka Allah ya nufa nayi imani da kaddara Allah yasa ba tawa bace yana fad'in haka ya fita yabar office din Tahir

Shi kam Tahir babu komai a ranshi sai tarin nadama tare dayin dana sani da abunda ya aikata wanda bai taba jin kunya a duniya ba irin yau, lallai son zuciya ya kaishi ga halaka lallai ya biye ma zuciyarshi Wanda gashi ta kaishi dayin dana sani Innalillahi'wa inna ilaihirajiun

Shi kam kabir koda ya nufi gida kai tsaye d'akinsa ya fad'a hafsat ganin haka yasa taji wani iri domin tasan indai ya fad'a irin wannan halin to tasan yaji magana akan ibtisam ne, ido ta lumshe gaba d'aya kishin ibtisam  yana cinta wanda take ganin itace tasa mijin Nata ya kasa bata wani kulawa

Kai tsaye ta tashi ta nufi d'akin kabir din amma Abun mamaki yasa ma kofar key ya rufe, alaman baya bukatar a shigo a damesa

Wani hawaye ne ya gangaro mata a ido tare da ba'kin cikin wannan rayuwa, yaushe mijinta zai cire wannan ibtisam din cikin ransa? yaushe zai daina tunaninta? yaushe zai bata cikakkiyar kulawa?

Lokaci d'aya tabar kofar d'akin tana kuka ta nufi d'akinta, lallai tana fama da son maso wani koshin wahala, ita Tana masifar son kabir amma shi ibtisam yake so

Ibtisam bayan tasha maganin duka, lokaci d'aya cikinta ya fara murdawa da ciwo Sosai kaman zata mutu, ihu ta Fara saki wanda bata san tanayi ba, domin irin azaban da takeji gaba d'aya bata san inda kanta yake ba ihu take Tana kuka hannunta nakan cikinta.....

Najeeb a tare da Mum suka zo d'akin da gudu

Koda suka k'araso tayi k'asa hannunta na kan cikinta tana kuka.

Da sauri NAJEEB ya dauketa sukai hspt da ita inda akai emergency da ita sai ihu take Tana kuka

Najeeb gaba d'aya ya kasa samun sukuni domin a furgice yake tare da fargaban mai ya sameta??

Itama Mum ta kasa zama gaba d'aya hankalinta a tashe yake

Dr dai yana ciki gaba d'aya jikin ibtisam yayi weak babu kwari

Dr yayi wajan 40 mnt sannan ya fito inda yake fad'a musu tasha magani over Wanda hakan yasa take wannan ciwon, daka duka alamu tana son zubar da cikin dake jikinta amma yanzu ku gode Allah komai normal but if she try again zata iya samun matsala domin kuwa wannan maganin da tasha yasa mahaifarta tayi weak, is better tayi hakuri harta haifi abunda ke cikin Nata....

Tunda Dr ya fara bayani idon NAJEEB ya kad'a yayi ja, lallai ya tabbatar da irin tsanar da take mishi lallai ya tabbatar tunda har Da gaske zatai yunkurin kashe abunda ke cikinta ya tabbatar zata iya kasheshi Fuuuuu ya fita daka hspt din mum na kiranshi amma ina kota ita bai bi ba Kai tsaye inda ake siyar da alcohol ya nufa inda ya siya wajan kwalba goma ya nufi gida

Koda ya k'arasa key yaba driver tare da fad'in ya koma hspt ya jira mum

D'akinshi ya shiga ranshi a bace har wani duhu duhu yake gani, bud'e bottle din alcohol d'in yayi yana k'okarin sawa a baki ya tuna da maganan ibtisam din I hate you duk wasu manya laifi ka had'a, you are drinker womanizer.... Ido ya lumshe tare da kafa kwalban a baki ya fara sha yana surutai yana fad'in even I, I hate you shan alcohol d'inshi yake kaman hauka yana surutai tare da jefar da bottle din ya fashe a d'akin a kalla yasha wajan bottle hud'u kuma duk ya fashe bottle din a d'akin lokaci d'aya ya fad'a kan bottle din a k'asa.......

Mum a asibti ta kwana ita da ibtisam wacce take a kwance har yanzu bata farka ba

Ibtisam sai wajan asuba ta farka tare da bud'e idonta Wanda yake a kumbure ta Fara kallon d'akin, ganinta a asibti ga Mum na sallah ta gane an kawo ta hospital ne, lokaci d'aya abunda ya faru ya fara dawo mata wani irin Abu taji yazo mata tare da fatan Allah yasa cikin ya zube tunda tasha magani da yawa.....

Jin muryan mum tayi tana fad'in kin tashi ne??

Ibtisam cikin dashewan murya tace eh

Ibtisam tashi tayi amma jikinta babu kwari, Mum tace Bari in taimaka miki kar abun drip din ya goce...    Ko da yake bari in kira su domin naga ya kusa k'arewa ma,  fita Mum tayi ibtisam taba cikinta tayi wanda ya dan Fara tashi saboda yawan cin abincin da takeyi sosai, jin alaman har yanzu yana nan yasa ta saki wani irin kuka tare da fad'in duk wannan wahalan da nasha?? Wannan wani irin jarabban ciki ne haka??  Wlh in bai fita ta sauk'i ba zanje a wanke shi ta yanda zai fita da hujja

Shigowan mum da nurse yasa tayi saurin goge hawayen idonta, nan nurse ta cire mata drip din Bayan mum ta tambaya ko akwai wanda za'a k'ara mata??

Nurse din tace a'a sai dai in dr yazo

Ibtisam toilet ta shiga inda tayi alwala tare dayin sallah, Bayan ta idar ta koma kan gadon ta kwanta wanda Tana tafiyan ne dakyar

Mum Tana zaune har Dr yazo ya duba ibtisam

Dr Ya kalli ibtisam yace ya jikin??

Tace da sau'ki

Yace ibtisam Mai yasa kika sha magani da yawa haka??  Kina son cikin ya zuba NE??

Ibtisam shuru tayi ba tare da tace komai ba, wanda ta tabbata Mum tasan komai wani irin kunya taji Sosai

Dr yace ina son in baki shawara Idan kika k'ara yunkurin yin hakan zaki iya samun matsala domin mahaifarki bata da kwari, so you have to be very careful Indai kina son rayuwarki

Nan Dr yace zata zauna na kwana biyu a nan, inda Mum tace bazasu iya tafiya gida ba

Dr yace zasu iya but tana bukatar hutu sosai, koda Kun koma Karta dinga aikin komai

Nan Mum tace shikenan inda Dr ya sallamesu suka koma Gida, koda suka isa Gida mum saida ta had'ama ibtisam ruwan dumi a cikin bath sannan tace taje tayi wanka

Bayan ibtisam ta shiga toilet mum direct d'akin NAJEEB ta shiga inda ta ganshi a k'asa ga jini dake zuba a jikinshi wani irin ihu ta saki mai firgitarwa da sauri ta nufeshi ta juyo dashi domin ta kife ya fad'i cikin mayen giyar da yasha inda ya fad'a akan kwalba Wanda ya sokeshi a cikin sa, Bayan ta juyo dashi ta Fara kuka ganin kwalba da sauri ta d'auki wayarta tana kuka lokaci d'aya ta kira Dr inda ta fad'a mishi yazo da kayan aiki kwalba ya sokar mata da a ciki

Ciki ta koma inda sai a sannan ta lura dako numfashi bayayi..... Wani irin ihu ta kurma mai ban tsoro wanda yasa ibtisam dake d'aki itama ta fito da sauri ta nufi gefen da taji ihun da yake a bud'e mum tabar kofar ibtisam itama shigowa tayi ganin halin da yake ciki yasa itama ta tsorata ganin jini a daskare Wanda da duka alama ya dad'e shine ya fara bushewa, Wanda ga wani shima yana zuba lokaci d'aya taji tana jin jiri ita dafa bangon d'akin tayi ta sulale tayi k'asa itama........

Read and leave it, dnt share to anyone......*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Mum ganin haka yasa ta kuma rud'ewa tare da salati, cikin tashin hankali ta nufeta, Shigowan dad ne yasa ya tsaya yana kallon ikon Allah, gaba d'aya kasa magana yayi sai kallo da yake binsu dashi ga NAJEEB kwance jini na zuba ga ibtisam itama kwance, lokaci d'aya yayi karfin halin ciro wayarshi ya fara kiran Dr.....

Jin sallama a falon yasa Dad fita, Dr ne yazo inda Dad ya mishi Iso har cikin d'akin najeeb din, inda Dr yaga kwalban daya sokeshi da kuma irin ciwon da yaji, nan take dr yace dole sai anje hspt, Mum fita tayi ta kira masu aikinta inda aka Kama ibtisam su Dad kuma suka Kama najeeb Wanda gaba d'aya basu San a wani hali yake ba

Kai tsaye hspt aka nufa dasu, inda duka aikai emergency dasu, Dr har uku suka shiga tare da nurse domin ceto rayuwarsu

Dad da Mum kam gaba d'aya sunyi zugum, musamman Dad yau da yaga abunda ya firgita shi, Domin kwalban giyan daya gani a dakin najeeb din, wanda bai shaba da kuma wanda ya fasa yaji mai wannan raunin, yau kawai for the first time yaji ya aikata babban kuskure na tura d'ansa waje karatu, ba tare da mai kula dashi ba, yau ne rana ta farko da Dad yaji ibtisam bata dace da d'ansa ba, yau ne rana ta farko yayi dana sani...... Wani irin fargaba yakeyi tare da tsoran yanzu idan dan nasa ya mutu Mai zaice ma Allah wanda ya tabbata giya yasha har yayi yawa yasa ya fad'a cikin wannan halin, Innalillahi'wa inna ilaihirajiun. Lallai ya cuci kansa tare da d'ansa gaba d'aya bai bashi ilimin addini ba, baima taba Ankara da kula da irin yanda yake gudanar da abunda addini yace ba, shidai d'ansa kawai yayi karatun boko, domin shine yake ganin hanyar data dace bana addini ba......

Mum ce ta katse ma Dad tunani cikin kuka tare da fad'in yanzu ka gani koh?? Ka tabbatar ma kanka koh??? Ka gani da idonka abunda d'anka yake aikatawa, wanda son d'anka da kuma rashin yarda da abun da wani ya fad'a maka saina wanda d'anka ya fad'a gashi yanzu ka gani da idonka, yanzu idan ya mutu Mai zaice ma Allah?? Kwata kwata babu ruwanka da irin rayuwar da d'anka yakeyi Kai komai ya fad'a a wajanka shine dai dai, wlh ka cuceni yanzu inya mutu shikenan ya tafi wanda giya ta zama ajalinsa tunda ita yasha ya bugu ya kasa gane mai ke gabansa Wlh...... Sai kuma tayi shuru can tace ba Kai d'aya bane Mai laifi harda ni Nima uwa ce, ya kamata in kula da irin tarbiyarsa duk da ka nuna akan NAJEEB kai keda power sosai......

Dad jin yanda take magana ga mutane na kallonsu yasa ya janyota tare da fad'in dan Allah kiyi shuru muna asibti ne.....

Mum kuka take Sosai amma gaba d'aya tasan an gama da najeeb, which tasan sune da laifi, wanda dad d'inshi yake ganin kaman gata yake mishi bai San cutanshi yake ba, tunda bai barshi yasan addini ba, gashi yanzu ya girma Wanda d'aukan karatu zai mishi wuya bama lallai yayi ba, domin sun riga Sun bata Abu tun Farko gyaruwanshi zaiyi wuya inma ya gyarun

Koda aka shigar da najeeb da ibtisam nan dr daya yayi kan ibtisam wacce take a sume domin

jinin data gani yasa ta jiri tare da tsoro wanda ya sata ta sume, ga jini daya Fara zubar mata a kasanta.......

Shi kam NAJEEB aiki za'ayi mishi domin kwalban Bayan ya huda shi akwai wanda ya karye ya shigan mai ciki, wanda yasa dole sai anyi mishi aiki domin a ciro thank god baima taba mishi hanji ba.....

Dr ne ya fita inda su Dad suka tashi suna tambaya akan ya ake ciki??

Dr yace dole sai anyi mishi aiki, domin kwalban ya shigar Mai ciki, nan yaba Dad takarda yayi signing

Inda Dr ya koma domin Ayi MA NAJEEB din aiki

Gaba d'aya su Mum sun shiga cikin tashin hankali tare da damuwa Sosai, wayar Dad NE yayi k'ara d'auka yayi yaga Abba ne

Bayan yasa a kunne Abba yace gamu Munzo ance wai kuna asibiti

Dad yace eh, kusa driver ya kawo ku, kace mi.... Bari in kira driver din ka shiga ka ajiye motarka a ciki saiya d'auko ku ata gida

Su Abba basu dad'e ba sai gasu sun zo shida Granny cikin tashin hankali

Granny ta Fara magana maiya faru Waye baida lafiya??

Dad yace najeeb da Ibtisam

Granny salati ta saki tare da fad'in ciwo lokaci d'aya haka?? Maiya samesu ni aminatu

Jin ihun ibtisam yasa sukai shuru cikin tsoran maike faruwa da ita.....

Gaba d'aya sunyi jigum..

Ibtisam farkawa tayi tana jin wani irin mugun ciwon ciki wanda ba komai bane ya sata hakan sai miscarriage din da tayi wanda domin abunda zata haifa gashi ya fito a dunkule kaman kwado amma bashi da girma Sosai, wanda hakan ya nuna alaman cikin mace gareta gashi ya zube, sauran jinin dake cikinta shine yasa ta murdawan ciki Sosai take wannan ihun, wanda yasa dole za suyi Mata wankin ciki

Granny dake waje bata san abunda ke faruwa ba, babu abunda take sai kuka domin a duniya bata son abunda zai taba lafiyar ibtisam ita da NAJEEB, domin Tana matukar sonsu, gashi yanzu tana jin ihun ibtisam din Wanda gaba d'aya yasa ta shiga cikin rud'ani

Jin ibtisam din tayi shuru yasa Granny K'ara tsora

Dr ne ya fito inda yace suje office d'inshi kai tsaye dukansu suka bishi

Inda Dr yace anyi nasara anyi ma najeeb aiki, an cire mishi kwalban, sai dai ina Mai baku shawara akan ku tabbata ya daina shan alcohol domin zai iya taba mishi kidney, dan yana sha da yawa wanda hakan yasa har ya fara taba Mai amma ba Sosai ba, idan yaci gaba dasha am sorry to say Indai harya taba Mai Toh mutuwa ne..... Sannan ya zubar da jini da yawa mun K'ara Mai

Salati Granny tasa tana kuka

Dr yaci gaba da fad'in ita kuma macen razanan da tayi yasa cikinta ya fita......

Granny kuka take Sosai, cikin data kwallafa rai dashi shine ya zube?? Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, yanzu jikan nata da take burin yazo duniya shine ya tafi?? Kuka take Sosai tare da fad'in Allah yasa hakan shine alkhairi

Dr yace ita macen yanzu babu wani matsala Domin anyi Mata wankin ciki, shine dai dai bai Farfad'o ba har yanzu

But karku damu any moment from now zai iya tashi

Nan su Dad suka fita koda suka fita inda su ibtisam d'in suke suka nufa wanda take kwance tana hutawa

Najeeb kuma na kwance har yanzu bai farka ba

Ibtisam gaba d'aya hawaye takeyi domin tsintar kanta tayi da ba'kin cikin zubewar cikinta, kuka take Sosai Wanda yasa NAJEEB farkawa tare da bud'e ido a hankali ya ganshi a kwance a asibiti da sauri yayi yunkurin tashi amma saiya kasa tare da ri'ke cikinshi, lokaci d'aya ya koma gaba d'aya Abun daya faru ya fara dawo Mai..... Da sauri ya tashi tare da tsige drip din dake hannunshi Wanda dai dai lokacin su Mum suka shigo

Jini ke zuba a hannunsa da sauri Mum tace najeeb......

Najeeb kam k'okarin tashi yake....

Ibtisam itama tashi tayi ganin jini yana zuba a hannunshi yasa ta nufeshi da gudu tare da cire hulan dake kanta tana k'okarin tasa Mai a hannu ya tureta tare da fad'in don't you dare touch me.......

Tsayawa tayi sororo tana kallonsa

Najeeb kam fita yake son yi amma Mum ta rik'eshi Dad ya fita kiran Dr sai ga Dr da Dad sunzo tare inda ya kamo hannun najeeb din da yake zubar da jini aka samai auduga aka matse

Dr yace najeeb bai kamata ka tashi ba you need to rest.....

Najeeb yace no Dr am OK I have to go, bana son zama a hspt Ina bukatar tafiya gida

Dr yace plz najeeb ka koma ka kwant....

Najeeb yace I said no Dr zan tafi America zan kula dakai na just allow me to go....

Dr babu yanda ya iya yace OK tare da bashi magani inda itama ibtisam aka bata

Kai tsaye gida suka nufa inda najeeb yake ganin dishi dishi Dad ya taimaka aka kaishi d'akinshi inda ya kwanta

Ibtisam kam gaba d'aya jikinta taji ya mutu gaba d'aya zubewar cikinta yasa taji komai baya mata dad'i, bata taba sanin cewa Ashe tana son cikin ba saida akace ya fita kuka ta saki mai cin rai......

Tana cikin kukan mum ta shigo ta ganta cikin wannan halin inda Mum tace tayi hakuri ta tashi taje tayi wanka, sannan ki tabbata kin gasa jikinki domin kina k'aramin jego ne..... Jin muryan Granny sukayi tana fad'in tashi muje inyi miki

Granny ta kalli Mum tace kisa a had'o Mata tea tasha

Ibtisam tashi tayi Granny ta Mata wanka, gaba d'aya ibtisam bata jin dad'in komai, amma da tayi wankan sai taji jikinta yayi mata karfi

Najeeb kam gaba d'aya ya kasa bacci gaba d'aya abunda ibtisam ta aikata yasa gaba d'aya yaji ko ganinta baya son yi, wanda ya tabbatar tsanar da take mishi yayi yawa, tunda har zata iya k'okarin cire cikinshi dake jikinta...... Shida kanshi yasan yayi hakuri yayi accepting d'inta but amma ita ta kasa ido ya k'ara lumshewa yana jin zafin abunda ta aikata, ga zafin aikin da aka mishi domin alluran kashe zafin da aka mishi ya daina aiki, gaba d'aya zafi wajan yake masa Sosai.....

Shigowan mum yasa ya kalli bakin kofar domin yaga Waye, ganin Mum yasa ya kura mata ido harta k'araso inda yake, tace sannu ya kamata kayi wanka ko zaka ji karfin jikinka

Ido ya lumshe alaman baya son magana

Ganin haka Mum yasa tayi dan murmushi tare da fad'in idan kayi wanka zaka ji karfin jikinka, sannan kaci abinci kasha magani

A hankali yace Mum plz I need to be alone, just go out

Mum kallonshi tayi tace son zan fita but sai kaci abinci kasha magani

Yace Mum I told you to leave, bazan shaba just leave me alone plz

Mum ganin haka yasa ta tashi jiki a sanyaye ta fita ta barshi.

Gaba d'aya najeeb jin zuciyarshi yake yana tafarfasa lallai komai zaima ibtisam bai kamata tace zatai yunkurin zubar Mai da ciki ba,  duk da yasan ya mata laifi Sosai, but why zatai yunkurin cire mishi jininshi daka jikinshi, ido ya lumshe cikin takaici gaba d'aya zafin da yakeji na aikin da aka mishi bai Kai ko rabin zafin da zuciyar shi take mishi ba, domin wani irin tafarfasa yake ji, lallai inta k'ara yunkurin aikata abunda ta aikata zai Mata abunda zatai mamaki

Dad ne da Abba da Granny sai Mum a falo, inda Mum take fad'a musu abunda najeeb ya aikata Bayan yasha giya inda ya saki ibtisam, sannan ya sadu da ita Bayan ya furta Mata Kalman saki cikin Maye

Granny salati ta saki sannan ta kalli Dad tace Wlh duk kaine ka lalata tarbiyan d'anka kaine kasa yake wannan Abun, ka kaishi k'asar da babu addini, k'asar masu jajayen fata, wanda su babu ruwansu da duk abunda wani ya aikata, wlh komai najeeb yayi kaine da laifi, kuma Wlh sai Allah ya tambayeka ka d'auka abunda Kama najeeb gata ne??  Wlh ba gata ka masa ba, domin ka bata mishi rayuwa ne gaba d'aya, ka cuci d'anka, Kai burinka yayi ilimin boko toh yayi Amma na addini bai dashi bana tunanin najeeb ko FATIHA zai iyayi, kai Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, yanzu miye amfanin irin haka??  Allah yace ka sanni Kafin ka bauta min, na tabbata najeeb babu abunda ya sani game Da addini, inda ya sani bazai sha giya ba, ku dama masu kud'i daka Allah ya baku duniya saiku manta da komai Idan kuka haifi yara burinku ku kaisu boko islamiya ko oho, wlh wannan tsanar y'ay'anku kuke ba so bane kuke nuna musu, yanzu ko miye amfanin hakan oho.....

Najeeb dake d'aki yana jin maganan Granny domin da karfi take maganan dan haka ya tashi ya fito dakyar ya zauna a falon domin yana dan jin k'adan daka magananta, wanda wasu baya ganewa

Ganinshi ya fito yasa duka suka tsaya suna kallonshi

Granny tace saiku fad'a mana miye yanzu tsakaninshi da ibtisam din??  Ya auransu yake??

Abba yace a kira ibtisam din

Mum tashi tayi ta nufi d'akin da ibtisam din take inda ta sameta tana hawaye domin itama tana jiyo su, sai dai ta fad'a ma mum abunda najeeb yayi amma ta kasa fad'a mata ta kamashi da mace Wanda ta rasa dalilin kasa fad'in hakan.

Mum tace ibtisam wai ba zaki bar wannan kukan ba?? Maza ki tashi muje falo ana kira

Ibtisam tashi tayi tasa hijab tare dabin Mum suka fita

Tunda suka fito idon najeeb yake kanta, gaba d'aya fuskanta yayi fayau kaman wacce tayi kwana da kwanaki tana jinya, lokaci d'aya ya kauda idonshi daka kanta

Ibtisam itama tana kallonshi ta gefen ido, domin gaba d'aya jinin data gani yana zuba a jikinshi ba k'aramin d'aga mata hankali yayi ba, domin tayi mugun tsorata sosai Wanda ganin jinin ya saka mata jiri, for the first time taji tausayin NAJEEB a rayuwarta domin ganin blood na zuba a jikinsa, duk da shi yaja ma kansa da yasha alcohol ya fasa bottle din

Nan Abba ya kalli ibtisam tare da kiran sunanta inda ya fara tambayanta da harshen turanci, maiya faru ranan da najeeb ya sakeki sannan saki nawa yayi miki

Najeeb da sauri ya kalli ibtisam din, wacce ta fashe da kukan da bata san zai fito ba.

Abba yace ke bana son shashancin ki fad'a mana abunda ya faru.....

Ganin yanda abba ya d'aure alaman bada wasa yake ba, yasa ibtisam fara fad'a musu yanda abun ya faru duk da tana jin kunya amma haka ta daure ta fad'a

Najeeb wani irin zugi yakeji cikin ranshi

Abba yace maganan saki ya saku, domin kuwa domin kuwa ba'a wasa da saki, koda da wasa mutum ya furta Kalman saki ya saku, balle a cikin Maye, Abu d'aya ne shine za'ace babu saki Idan mutum yana Maye yayi amma fah sai dai in matse mutun akayi aka bashi shine babu saki, amma idan mutum ne yasha da kansa yayi saki to sakin ya saku, toh amma kaman yanda ta fad'a ya furta Kalman sakin ne sau biyu ya fad'i, kenan ya zama saki Biyu,

Sanda ya tashi kuma wani abu ya shiga tsakanin su, Toh daka k'okarin koda bai furta ya dawo da itaba aure ya dawo, tunda har wani abu ya shiga tsakanin su..... Wanda yanzu suna da igiya d'aya data rage musu a tsakaninsu

Abba kallon najeeb yayi tare da kiran sunanshi yace najeeb Ina son ka sani shan giya haramun ne, shan giya yana d'aya daka cikin manyan laifi, sannan duk Wanda yasha giyar duniya koda ya tuba ya daina bazai sha ta Aljanna ba, sannan kaga abunda ka aikata ma kanka kana k'okarin kashe kanka kasha giya ka fasa kwalban ka fad'a kan kwalban gashi saboda razanan da matarka tayi na ganin jinin dake fita a jikinka yasa tayi Bari.......

Najeeb da sauri ya tashi tare da fad'in what?? Ibtisam miscarriage?? How?? Hannunshi ya d'aura a kai alaman mamakin Kalman da aka fada mishi yake

Lokaci d'aya ya cire hannunshi a fuska wanda idonshi ya kad'e yayi ja, kallon ibtisam yayi tare da fad'in are you happy now?? Yes I know you are happy cikin da kike burin ki cire gashi ya fita....... Shuru yayi yana hura iska Mai zafi sannan ya yace ibtisam just for once kin taba tunanin irin yanda zanji Idan cikin nan ya fita?? I know babu furgicin da yasa cikin nan Ya zuba, da gangan kika zubar.....

Abba yace kaman ya najeeb Dr ya fad'i haka??

Najeeb ya kalli Abba tare da bashi Labarin maganin da tasha domin cikin ya fita wanda shine silan da yasa na dawo nasha alcohol domin in huce saboda raina ya baci sosai and only alcohol zansha inji sanyi....

Tas saukan Marin da abba yama ibtisam yasa NAJEEB yin shuru wanda NAJEEB yaji Marin kaman shi akama Dan irin sautin da Marin yayi......

Abba yace irin tarbiyan da muka koya miki kenan?? Ibtisam ashe baki da tausayi baki da imani?? Kisa?? Kisan kai kike kokarin yi?? Yau koda cikin shege kikayi bazan yarda ki zubar ba, domin ni musulmi ne Nayi imani da kaddara, balle cikin da kika samu ta hanyar sunna.....

Cikin kuka tace Abba naso in zubar da cikin daka jiya da abun ya faru Wlh nayi nadama, domin gaba d'aya idona ya rufe bana gane komai, Abba karka manta abunda kayi shine za'ama d'anka, tun daka irin yanda na samu cikin da irin halin najeeb Wanda yake aikata manyan laifi baya tuna Allah sai yasa gaba d'aya nake tsoran had'a zuri'a dashi, gudun kar Nima aima nawa Yaran, I knw I never love him, but whenever I try to accept him as my husband daka na tuna irin abunda yayi min sai in kasa, Abba nida kaina Nasan ban dace da najeeb ba, Abba karka manta ance ku zabama y'ay'anku iyaye na gari, najeeb baya tsoran Allah, gaba d'aya duk wasu manyan laifi da Allah ya hana shine yakeyi Bayan shan giya harda..... Kuka yaci karfinta tare da fad'in ba komai bane zan bud'e in fad'a amma ina son Ayi min adalci, NAJEEB baya so na Nima bana sonshi duka muna wani irin zama ne wanda gaba d'aya ban San amfanin zaman ba......

Abba yace Yimin shuru, badai ciki kike son ya fita ba?? Toh yanzu burinki ya cika saiki ji dad'i, sannan Wlh zama keda NAJEEB yanzu kika fara, domin wannan auren rai ne dashi Bamu da ikon rabashi har sai ya k'are......

Najeeb dake tsaye yace Abba zan nema mana mafita nida ita Wanda nake ganin shine ya dace, kaman yanda ta fad'a bata so na and Nima bana sonta, yeah is true babu amfanin zaman ni da ita..... Shuru yayi tare da kallon ibtisam dake kuka mai cin rai, yace I know nasha fada bazan Saki matar dana aura ba, saboda inada kishi yau for the first time naji bana bukatar zama da

ibtisam.........

Plz am sorry for late post

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Ibtisam kallonshi tayi da sauri wanda akai Sa'a shima ita yake kallo, matsawa yayi kusa da ita tare da fad'in you always ask me to send you free right??

Ibtisam kasa bashi amsa tayi......

Najeeb yace OK I will send you free, coz even I ban San kallon Fuskanki because whenever I see your face zan tuna da abunda kika aikata which....... Shuru yayi yana kallonta yanda take kuka

Ibtisam wani kuka ne ya kubce mata wanda bata san tanayi ba, kuma bata san zai fito ba......

Granny ce tace wai miye haka kukeyi ne? Kai ku fad'amin Mai kuke cewa Kun barni cikin duhu fah

Matsawa tayi kusa da najeeb wanda yake gaban ibtisam yana kallonta, tace Mai yake faruwa ne?? Tare da kallon ibtisam

Dad ne yayi magana tare da fad'in najeeb karka sake ka aikata abunda kake k'okarin aikatawa domin ibtisam nada laifi kaima kana dashi, just forgive and forget, kuyi hakuri ku d'auki kaddara, sannan maganan ibtisam gaskiya ta fad'a babu wacce zatai burin samun miji Dan giya har tai fatan ta had'a zuri'a dashi......

Abba ya katse Dad da fadin karka fad'i haka, komai da Allah ya tsara yana cikin kaddaran mutum, kaman yanda ka fad'a su amshi kaddara, haka shima abunda najeeb yake yana cikin kaddaranshi duk da akwai sakaci a ciki.....

Granny tace Kai Wai ba zaku fad'amin abunda ke faruwa bane??

Mum ce ta Fara Mata bayani harta gama granny ta kamo hannun najeeb Tana kuka Tana fad'in najeebu kayi hakuri dan Allah karka rabu da ibtisam na dad'e Ina fatan kuyi aure, sai gashi Allah ya yarda kunyi, kayi ma Allah kuyi hakuri ku zauna, Nayi farin ciki na Farko ranan da aka d'aura aurenku, yanzu babu abunda nake so in gani kafin in mutu sai yaranku, idan naga wannan kad'ai ya isheni dan Allah ku barni inga cikan burina na ro'keku.....

Najeeb yana jin abunda Granny take fad'a amma bazai iya bata amsa da Hausa ba.... Gaba d'aya yauce rana ta farko da yaji tausayin tsohuwar wanda ta kasance abokiyar fad'anshi..... Idonshi ya sauka akan ibtisam dake kuka itama wanda gaba d'aya maganan Granny yasa jikinta yayi sanyi

Granny ta kamo hannun ibtisam ta had'a dana NAJEEB tace wlh Idan kuka kasance a haka, koda banga abunda kuka haifa ba, zan mutu cikin salama, amma bazan iya juran ganin kun rabu ba dan Allah......

Najeeb ya janye hannunshi daka na ibtisam tare da fad'in I have make a decision bazan zauna da itaba, granny am sorry bazan zauna da matar da bata so na ba, na tabbata Idan ina tare da ita bazan juri Kalman cewa Tana son wani namiji a gaba naba Dan haka am sorry to say na sakeki saki d'aya.......

Ibtisam wani dum dum taji Wanda komai nata taji ya tsaya cak...... Lokaci d'aya kuma ta saki kuka mai sauti tare da fad'in Wlh najeeb baka da imani baka da tausayi, kaman yanda ka fad'a ban taba Sonka ba, amma yau kawai just for granny happiness naji Ina son zama dakai, dan kawai in sata farin ciki but you divorce me.... Hawayen idonta ta share tare da fad'in Allah yasa haka shine alkhairi, tana fad'in haka tayi Fuuuuu ta shige ciki

Najeeb ganin haka yasa ya lumshe ido, abunda baya son ji daka bakinta shine ta fad'a ban taba Sonka ba..... Wannan Kalman yana bata mishi rai, a kullum ya tuna irin yanda take cewa I hate you Abun yana sashi cikin takaici

Mum ce tace wannan sakin daka aikata bai saku ba......

Da sauri ya kalli mum alaman Mai take fad'i.....

Mum tace idan namiji ya saki mace tana jini wannan sakin bai saku ba, karka manta ibtisam tayi Bari kuma Tana jini a halin yanzu.....

Najeeb kallon mum yayi wanda Abba ya cabe da wannan hakane, ibtisam har yanzu tana matsayin matarka

Najeeb barin falon yayi inda jim kad'an sai gashi da k'aramin akwatin shi

Dad yace ina zaka??

Yace am leaving the country now

Dad yace taya zaka tafi Bayan baka da lafiya anyi maka aiki

Yace Dad plz am not a child yana fad'in haka ya fita Fuuuuu yabar gidan

Ibtisam itama tunda ta shiga d'aki ta Fara had'a kayanta domin yau take son barin gidan, Toh zaman Mai zatayi a gidan? Bayan ta gama had'a kayanta ta fito inda ta gansu a falo

Mum tace ke Ina zaki Kema haka??

Granny tace ni kun barni a duhu ko binshi za tayi ne??

Ibtisam tace Mum zan tafi skul yau, dan Allah karku hanani Ina bukatar in tafi wajan da......

Abba yace babu inda zaki

Dad yace a'a ka barta, ibtisam ki koma d'aki ki bari gobe sai driver ya kaiki

Komawa tayi inda su kuma suka zauna suna tattaunawa akan yanda zasu bullo ma al'amarin, inda Dad ya fara magana da fad'in nasan na cuci Najeeb Wlh komai yayi laifi nane, gaba d'aya ban bashi Ilimin sanin uban gijinsa ba, na D'aukeshi na kaishi rayuwar data Tamu ba, lallai Ina jin kunyar kiran kaina mahaifi Domin ban kasance d'aya daka cikin iyaye na gari ba, sai ga hawaye akan fuskan Dad,

Gaba d'aya kowa yayi shuru domin jikinsu yayi sanyi Sosai dajin kalaman Dad.

Dad yaci gaba da fad'in lallai sai yanzu na gane babban gatan da mutun Zaima d'ansa shine ya nema mai ilimin addini, bana zamani ba, domin daka ranan da mutum ya mutu wannan ilimin nashi na boko baida amfani ko kad'an, amma ilimin addini kam shine zai taimaki mutum a lahira, inda har yana dashi kuma yayi aiki dashi, gaba d'aya najeeb baya ganin girman mu which irin abunda yaga anayi a k'asar daya taso kenan, yaro yana abunda yake so, iyayenshi basu isa su hana shiba, rayuwar da kowa yake ganin yana da y'anci, na cuci d'ana da kaina

Yanzu idan NAJEEB  ya mutu baida wani hujja, shikenan na bata mishi rayuwa....

Granny tace Alhmdlh tunda har Allah yasa ka fahimta kuma harka gane hakan, dama abunda naita kokarin nuna maka tun Farko kenan, gashi yanzu ka fahimta wanda a yanzu zan iya cewa lokaci ya k'ure maka, gaba d'aya kun d'auki rayuwar boko Kun sama kanku, bakwa tuna addini, wanda shi wannan bokon iyaka duniya ne, daka nan cikin duniya ya gama amfani, ku a'a bakwa tuna haka kudai burinku kawai kuyi boko shine wayewa, Hmmm Allah sarki rayuwa, Allah yasa mu dace

Duka suka amsa da Ameen

Abba yace yanzu lokaci bai k'ure Ba, ya kamata NAJEEB din a zaunar dashi Ayi mishi magana domin yasan addininshi

Mum tace inaga gaskiya babu wanda zaiyi mishi wannan taimakon sai a ibtisam, domin gaba d'aya na lura da NAJEEB yana Sonta, duba da irin yanda yake mata abu, na tabbata inda ibtisam zata kwantar da hankalinta ta nutsu ta amshi kaddara ta D'aukeshi matsayin miji ta nuna mishi muhimmancin ilimin addini na tabbata zai nema ilimi, domin ko dazu da take fad'in a mata adalci taya zata haiyu da Wanda yake aikata manyan laifi, na lura dashi kaman abun ya bata mishi rai sosai Wanda nake tunanin shine yasa har ya yanke hukuncin rabuwa da ita, wlh Nasan NAJEEB yana Sonta, shi a nashi tunanin inya rabu da ita shine zai bata daman samun abunda take so.....

Abba yayi murmushi tare da fad'in Nima na Lura da hakan ai koda aka fad'a mishi sakin bai saku ba, Kinji ai baice komai ba, sai barin gidan da yayi

Itama ibtisam d'in tana sonshi, duba da irin yanayin data shiga daya furta mata Kalman saki, tunda gashi itama daka karshe kwaso kayanta tayi zata bar gidan, wanda Ita bata san yama tafi

ba, amma inaga tunda hakan ta faru mu barsu su hutu, dukansu suna jin haushin junansu, musamman NAJEEB da yake ganin itace ta zubar mishi da ciki, idan ya huce Nasan komai zai dai daita

Granny tace hakane,, Allah ya zaba mana abunda yake alkhairi

Duka suka amsa da Ameen

Inda Aka Kai abba d'akin ba'ki

Granny kuma tayi wajan ibtisam inda ta sameta tana kuka, tasan bata san najeeb amma gaba d'aya bataji dad'in raguwar aurensu ba, duba da yanda Granny take son su zauna a tare....

Granny tace ibtisam wannan kukan, fah???

Al kamata yayi kiyi murna tunda auren ya mutu, ba kince baki sonshi ba, toh ya rabu dake sai kije ki auri kabiru Mai Mata, wanda nake tunani hala harda ciki ma, ya manta dake, inma bai manta dake ba kyaje ki had'u da kishiya......

Ibtisam gaba d'aya ji tayi ta shiga rud'ani, ita fah duk wannan abunda ake ta manta ma fah ance kabir shima an d'aura Mai aure da wata..... Lokaci d'aya ta lumshe idonta domin yanda taji zuciyarta na Mata zafi, wannan zafin da takeji bana komai bane saina sakin da najeeb yayi mata, gaba d'aya ji tayi duniyar babu dad'i

Ganin granny ta dameta yasa ta tashi tayi toilet Tana kukanta, tare da kosawa gari ya Waye tabar gidan ta taji skul wanda sun kusa Fara exam

Najeeb kam America ya koma, domin yana bukatar tambayan malami game da wannan sakin da yayi ma ibtisam akace bai saku ba, kai harma da Wanda yayi mata sanda yasha giya, domin yana ganin kaman sharri ma tayi dan kawai ta rabu dashi, murmushi yayi sannan yace na barki ibtisam.....

Najeeb koda ya koma gidansa dake America sai yaji gidan yayi mishi empty, gashi tunanin ibtisam da abubuwan daya faru tsakaninsu shine ya fara dawo Mai cikin rai...... Ganin tunanin yayi mishi yawa yasa ya d'auko kwalban alcohol d'inshi ya bud'e harya kafa Kai zaisha yaji maganan ibtisam cikin kunnenshi " amin adalci babu wacce zata so ta had'a zuri'a da Wanda yake shan giya, NAJEEB na tsaneka mashayi, you are drinker I hate to see your face...... Sakin kwalban yayi ta fad'i k'asa ta fashe tare dajin wani irin bugun zuciya, gaba d'aya ranshi babu dad'i ganin rad'adin yayi mishi yawa gashi tunanin ibtisam din ya hanashi sakat dole ya d'auko wata kwalban ya bud'e tare da kafa kansa ya fara kwankwada yasha wajan kwalba uku..... Gaba d'aya ya kasa tashi sai sumbatu yakeyi .......

Washe gari kaman yanda Dad yace hakan ya faru inda yasa driver yakai ibtisam skul Bayan dad yayi mata nasiha akan ta ri'ke mutuncin ta

Gaba d'aya ibtisam kallo d'aya zaka mata ka gane tana cikin wani hali, har rama tayi na wuni daya kaman wacce tayi ciwon kwana da kwanaki

Abba ya K'ara da fad'in sannan maganan aurenki da najeeb ki d'auka bai mutu ba....

Da sauri ta kalli Abba

Abba yaci gaba da fad'in Domin kuwa zamu tambayi malamai akai muji, saiki d'auki kanki matsayin matar aure

Jiki a sanyaye ta tashi ta fita gaba d'aya ta rasa maike Mata dad'i a duniya.....

Haka driver yaja suka wuce bayan Dad ya bata kud'i masu yawa

Bayan tafiyar ibtisam ne Abba yace suma Bari suzo su Kama hanya..... Abba yace lah kaga wani abu Aida ma mu muka sauketa a skul d'in

Dukansu dariya suka sa, domin Sun manta shap hanya ne..

Dad yace ai yanzu tunda hakan ta faru shikenan Allah dai ya kaisu lafiya

Suma su Abba kama hanya sukayi

Ibtisam wajan 3 suka k'arasa inda ta d'auki kayanta tai ciki, tazo zata k'arasa d'akinsu ta had'u da kubra

Kubra tace ibtisam sai yau?? Kai gaskiya kinsha ciwo Wlh har kin rame, sannu Allah ya k'ara sauk'i Bari ana jirana zanje in dawo

Gaba kubra tayi inda ibtisam tayi d'akinsu ta samu kofar a bud'e...  Kai tsaye ta shiga inda taga zarah na girki

Zarah ganin ibtisam yasa ta saki ihu tare da rungumeta tana murna

Ibtisam kam kuka ta saki tare da fad'in Zarah NAJEEB ya sakeni.....

Zarah tace what saki??  Garin yaya??

Nan ta Fara bata Labarin abunda ya faru daka karshe tace zarah NAJEEB yana zargin na zubar

da cikin ne da gangan wanda da farko Nayi yunkurin yin hakan amma na fasa sai gashi daka baya ya zube, which jinin da naga yana zubar Mai yasa gabana ya Fadi duka zatona ya mutu ne.....

Ajiyan zuciya Zarah tayi tare da fad'in haka abubuwa marasa dad'i sukai ta faruwa?? Amma duk ban sani ba

Ibtisam tace taya zaki sani Bayan bani da sim din da zan kiraki dashi muyi magana

Zarah kallom ibtisam tayi sannan tace ibtisam kina son NAJEEB,..

Ibtisam da sauri ta kalleta tare da sakin tsaki tace, ban taba sonshi ba, har gobe kabir nake so, sai dai kuma shima yana da mata sai kuma ta saki kuka....

Nan zarah taita rarrashinta akan tayi hakuri ta daina wannan kukan,

Dakyar ibtisam tayi shuru baccin wahala ne ya d'auketa

*AMERICA*

NAJEEB gaba d'aya yanzu kullum cikin Maye yake ko aiki ya rubuta musu takardan hutu harna wata biyar inda kullum yana gida yana shan alcohol d'inshi, domin baya son ya bata lokacin shi wajan wani tunanin da yake cewa baida amfani wanda gashi ya kasa daina tunanin

Kaman yanda yayi da Malam akan zaiso America zasu had'u hakan ko ta faru

Domin malamin shida kanshi yayi ma najeeb text akan yana America tare da tura ma NAJEEB harda address d'inshi domin tun sanda sukai waya da najeeb maganan najeeb ta tsaya mai a rai....

Allah yasa lokacin NAJEEB bai kwale ba, wanda hakan yasa dole ya garzaya domin ya sadu da malamin, domin yana son shima da kanshi yasan miye addinin Islam, sannan Abun dake ranshi yanzu yana son sanin miye hukuncin sakin da yayi ma ibtisam.......

Bayan najeeb ya shirya Kai tsaye gidan malamin yaje inda malamin ya amshi NAJEEB hannu bibbiyu

Nan ya mi'ka ma najeeb hannu suka gaisa

Inda yama NAJEEB umarni daya zauna

Bayan najeeb ya zauna sannan malamin yace najeeb koh??

Najeeb yace eh, tare da fad'in Malam mutum ne yasha giya Bayan yasha giya saiya furta ma mace Kalman na sakeki na sakeki har sau biyu ya matsayin sakin yake?? Shin yana matsayi saki Biyu ne duk da bai furta ba??

Sannan Idan namiji ya saki mace tana jinin haila ya matsayin sakin yake??

Malamin yayi gyaran murya tare da fad'in :

Wanda ya saki matarsa cikin Maye bata saku ba

Malamai sunyi sabani game da aukuwar sakin Wanda yake cikin Maye

1) mafi yawan malamai sun tafi akan cewa idan mutum ya saki matarsa, tabbas sakin ya auku, saboda shan giya sabon Allah ne, kuma shi ya jawo wa kansa, don haka sakin ya saku baza'ayi masa uzuri ba wannan itace maganan Abu hanifa, da Malik da shafi'i a daya daka cikin zantukansu

2) sakinsa bai auku ba, saboda lokacin da ma'iz yazo ya tabbatarwa Annabi (S A W) yayi zina, saida ya tambaye shi ko kasha giya ne, kamar yadda baihaki ya rawaito a sunanul kubra, hakan sai ya nuna mashayin giya ba'a amsar magananrsa.
Sannan an rawaito daga SAYYADINA USMAN da ibnu Abbas cewa :sakin mashayin giya baya aukuwa, kuma ba'a San wanda ya saba musu ba a cikin sahabbai. Wannan itace maganan imamu Ahmad da zahiriyya da ibnu taimiyya

Sannan akwai mutanan da sharuddan saki basu rataya a wuyansu ba

Halaye biyar da Shari'a tace in mutum ya saki matarshi a wannan halayen bata saku ba.

1) sakin mahaukaci: wannan ma wani abu ne sananne a shari'a cewar hankali na daga cikin sharuddan karban ko wane irin aiki na ibada

2) sakin mutumin dake cikin Maye : wasu Malaman na ganin ta saku saboda shi ya Sanya kansa a halin Maye, amma wasu Malaman na ganin matar bata saku ba saboda akwai hukuncin da Allah zaiyi masa akan shan kayan Maye da yayi Allah ne mafi Sani.

3) sakin mutum da aka tilasta: dole ne miji ya kasance Mai ra'ayi kansa Idan kuma har wasu zasu yi amfani da matsayi na jini ko kusanci ko kuma karfi a tilasta a sakar ma mutum mace to bata saku ba, ciki harda iyaye

Sai dai mafi kyawun a duk lokacin da iyayen mutum suka nuna masa ba su son wani abu, sai yabi hanyar data dace Don fahimtar dasu ta yadda zasu amince da abun, in kuma basu har suka k'i yarda suka cije sai ya duba darajan su na iyaye ya musu biyayya Don neman yardan Allah

4) sakin mara lafiya Wanda yakai gargara : malamai sunyi magana cewar Idan har ya saketa ne da gangan Don ya hanata cin gado to bata saku ba, in kuma ita da kanta ta nema ko kuma tayi laifin da yana iya Kai wa ga sakin shima wasu malaman na ganin ta saku.

5) sakin da akayi cikin zuciya ba tare da furuci ba. Mafiya rinjayan malamai sun tafi akan wannan saki bai inganta ba, saboda fadar Annabi (S A W)  da yace lallai Allah ya yafe wa Al'ummata abin da zukatansu suka ambata muddin basu furta ko suka yi aiki dashi ba.

Malamin yace sannan yazo cikin sahih Muslim daga Manzon Allah ( S A W)  cewa :

A duk lokacin da wani mutum ya saki matarsa yayin da take cikin al'adarta, lallai ya zama wajibi kada ya kula da wannan saki da yayi mata (Ma'ana sakin bai yi ba)  yaci gaba da zama da matarsa har zuwa lokacin da zata yi tsarki, sannan ya saketa idan yaga dama,  sahin Muslim kitabut talak juzu'i na 2

Maganan saki cikin Maye bata saku ba, kallon NAJEEB yayi sannan yace ko kaine ka aikata hakan??..

Najeeb yace nine na aikata hakan bayan nasha giya, na furta Kalman har sau biyu

Malamin yace Toh kaji yanda abun yake Sannan shima saki cikin haila shima bai saku ba......

Najeeb gaba d'aya wani irin Abu yaji cikin ranshi shidai ba ba'kin ciki ba haka ba murna ba

Malamin yace sannan ka tambayeni a waya akan shan giya haramun ne tare da zina??

Najeeb yace eh hakane, ina bukatar sanin hukuncin Mai shan giya a addinance da kuma hukuncin zina......

Malam yace shan giya haramun ne saboda fadar Allah a cikin SURATUL MA'IDAH Aya ta 90

Hukuncin mai shan giya kuwa in an kamasa za'ayi masa bulala 80 a mazhabar Abu hanifa da Malik da wata ruwa daga Ahmad bin hambul
Amma a wurin imam shafi'i da Ahmad a wata ruwayar daga gareshi za'ayi masa bulala 40 ne, duk suna kafa hujja da hadisin Anas dan Malik, wanda imamu Muslim ya rawaito shi a Lamba ta 1706.
In kuma ya mutu bai tuba ba zai shiga wuta,  kamar yadda hadisin Abdullahi  ibn Umar wanda ke cikin bukhari 5147 da Muslim 3736 ya nuna

Sannan sallah kwana arba'in mashayin giya zaiyi ba'a amsa, hadisi ya tabbata cikin sunan na imam nasa'i 5570, Sheihk albani ya inganta shi cikin silsila sawahiha 709 hadisin Abdullahi dan Umar.

Sannan ga cuttuka da giya ke haifarwa

Ulcer gyambon ciki
Yawan mantuwa
Tana taba hanta kuma Idan ya taba hanta yana sama mutum hepatitis
Sannan zuciyar mutum zata dinga bugawa da sauri, har zai iya janyo MA mutum kumburin zuciya, ga hawan jini
Sannan hantar mutum zata dinga nokewa
Gashi yasa mutum yayi wani irin girma Mara amfani

Akwai alot of cuta da giya ke sawa.....

Najeeb shuru yayi amma daka duka alama maganan malamin na shigarshi

Ajiyan zuciya najeeb ya sauke sannan yace yanzu wannan shine hukuncin mai shan giya???

Malam yace eh

Najeeb yace musulunci babu wani abu daya tanadar ma mutum in yana fushi, wanda in yasha zai huce

Malamin yace akwai mana

Najeeb kara zama yayi alaman yana son yasan Mai musulunci ya tanada

Malamin yace Al'qur'ani, a duk lokacin da mutum yake fushi ko kunci to tabbas ya d'auki al'qur'ani ya karanta.....

Nan malamin yai ta mishi bayani akan hukuncin zina da sauransu

Najeeb gaba d'aya jikinshi ya mutu lallai sai yanzu ya gane ashe da ba rayuwa yake ba, yana ta aikata manyan laifi ba tare da saninshi ba, lallai iyayenshi basu mishi gata ba, gashi yanzu yana da ilimin boko ga dukiya ya tara amma babu ilimin addini wanda shine zai kaishi da hanyar tsira wani irin hawaye ya silalo mishi a fuska.......

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Malamin ganin haka yasa gaba d'aya yaji NAJEEB din ya k'ara bashi tausayi Sosai, lallai an bar gini tun ran Zane, da yawa haka yanzu iyaye sukeyi basa bama yaransu ilimin addini saina boko, wanda wannan Abun ya zama ruwan dare, sudai burinsu y'ay'ansu suyi ilimin boko kawai na addini kuma ko oho, Allah yasa mu dace.

Da yawa masu kud'i suna d'auka kaman ba zasu mutu ba, gaba d'aya sunsa duniya a gaba, basa tuna mutuwa, sudai duniya kawai suka sa a gaba.....

Malamin ya kira Sunan NAJEEB da fad'in Allah mai yafiya ne ga bayinsa baya Kama bawa da laifin da bai sani ba, sannan koda mutum ya aikata Sabo, Indai harya tuba toh Allah zai yafe masa, a cikin.....

SURATU AL'IMRANA:

Wanda take karantar da cewa Allah yana karban addu'ar wanda ya kira shi da gaskiyar niyya, kuma yana keta al'adu Da wannan kira. Babu abin da yake da wuya ga Allah idan an kadaita shi da tsarkakewa daga shirka da abin da ya yi Kama da shirka.

Toh ka gani Allah yana yafe ko wani laifi amma banda shirka

Allah babu wani abin bautawa face shi, rayayye mai tsayuwa da Kome, Al'imran Aya ta (2)

Ya sassaukar da littafi a gareka da gaskiya, yana Mai gasgatawa ga abin da ke gaba gare shi, kuma Allah ya saukar da attaura Da linjila. Al'imran Aya ta (3)

A gabani, suna shiryar da mutane, kuma ya saukar da littattafai masu rarrabewa. Lalle ne wad'anda suka kafirta da ayoyin Allah suna da azaba Mai tsanani. Kuma Allah mabuwayi ne, ma'abucin azabar ramuwa. Al'imran Aya ta (4)

Lalle ne Allah babu wani abin da ke boyuwa gareshi a cikin k'asa, kuma babu a cikin sama. Al'imran Aya ta (5)

Malamin ya kalli NAJEEB yace kaga Allah yana Sonka da rahma tunda har ka farga ka gane, domin yau Idan mutum ya mutu bashi da wani hujja ko uzuri da mutun zai kawo wanda ya hanashi sanin uban gijinsa

Amma yanzu da yake Allah na Sonka da rahma gashi ka farga da wuri tun lokaci bai k'ure maka ba

An kawata wa mutane son sha'awoyi d'aga mata da d'iya, da dukiyoyi abubuwan Tarawa daga zinariya da azurfa da Dawaki kiwatattu da dabbobin ci da hatsi. Wannan shine dad'in rayuwar duniya. Kuma Allah a wurinsa kyakyawar makoma take. Al'imran Aya ta (14)

Kace : shin kuma, in gaya muku mafi alheri daga wannan?  Akwai gidajen Aljanna a wurin Ubangiji saboda wadanda suka bishi da takawa, koguna suna gudana  daga k'arkashinsu, suna madauwama a cikinsu, da matan aure tsarkakku, da yarda daga Allah kuma Allah mai gani ne ga bayinsa. Al'imran Aya ta (15)

Allah ya shaida cewa: Lalle ne babu abin bautawa face shi,  kuma mala'iku da ma'abuta ilimi sun shaida,  yana tsaye da adalci babu abin bautawa face shi mabuwayi, mai hikima. Al'imran Aya ta (18)

Malamin ya kalli najeeb yace Allah mai gafara ne, sannan Allah mai adalci ne, yana yafiya Idan aka ro'ka, yana amsa kiran wanda ya kirashi....

Kace: Idan kun kasance kuna son Allah, toh ku bini, Allah ya so ku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Kuma Allah mai gafara ne mai jin k'ai. Al'imran Aya ta (31)

Toh kaji abunda wannan ayar take fad'a?  Allah mai gafara ne, Najeeb Allah yana son Idan bawansa zai tuba yayi tuba ta tsakani da Allah wanda ya tuba kenan, bawai mutum yace Allah

na tuba ba, sannan ya koma abunda yake aikatawa na sak'o ba, Allah baya son irin wannan tuban....

Najeeb yayi ajiyan zuciya tare da fad'in Malam gaba d'aya Ina son insan addini na, sannan ina son ka koyar dani kaman sabon wanda ya musulunta wanda bai San komai ba, ina son ka fad'amin duka hakkokin dake kaina, sannan mai addini yayi umarni da muyi da kuma wanda yayi hani dashi, wlh Malam yau kawai nima da kaina ...... Maganan ibtisam ta fad'o mishi a cikin kunne Ina jin kunyar kiranka da sunan musulmai..... Wani hawaye Mai zafi yaji ya fito Mai, lallai dole tace haka, shima da kanshi abunda yaji yanzu kenan, gaba d'aya yana jin kunyar kiran kanshi da sunan musulmai....

Malam dinne ya katse mishi tunani tare da fad'in Alhmdlh tunda har zaka Fara koya, lallai mutane irinka suna da Sa'a a rayuwa, kwata kwata wata d'aya zanyi a America in koma saudiya, amma yanzu just kawai for you zanyi wata uku, domin nida kaina naji Ina burin ka koyi abubuwa da yawa, kuma insha Allah inka dage zaka San abubuwa da yawa, yanzu abu na Farko kasan miye addini?? Ya ake bauta ma Allah, abunda zamu Fara kenan.......

Tun daka ranan najeeb ya Fara d'aukan darasi wajan malamin, kuma malamin ya lura najeeb yana son karatun gashi yana saurin d'aukan abunda aka koya mishi, hatta sallah najeeb ya gane da ba dai dai yakeyi ba, domin kuwa a da kawai yana yine sunan muna musulmi.

Najeeb kullum yayi sallah yana ro'kan Allah akan ya bud'a Mai kwakwalwa, tare da neman gafaran Allah akan abunda ya aikata cikin rashin sani, sai dai abu d'aya dake ranshi yana fama da yawan sha'awa ga tunanin ibtisam ko a wani hali take yanzu oho, domin tunda yazo bai kuma zancen taba, ko yayi waya da iyayenshi baya magananta Suma basa masa zancan ta

Najeeb ya fad'ama Malam irin yawan sha'awan da yakeji, inda malamin yace ya dinga yin azumi

Hakan koh yakeyi yana azumi, lallai najeeb ya yadda addinin musulunci bai boye komai ba, a kullum yaje wajan malam sai yaji wani sabon Abu Wanda bai taba jiba, wasa wasu har yayi wata d'aya yana d'aukan darasi, najeeb yasan abubuwa da yawa, yasan yanda ake bada Zakka, yanda ake kula da hakkin iyali, yanda zai bauta ma Allah, abubuwan da Allah ya hana da Wanda Allah Ya halitta, a halin yanzu malamin yana koya mai ba'ki domin yace Idan ya iya zai iya karanta komai......

ABU ZARIA FEMALE HOSTEL

ibtisam gaba d'aya ta canza ta rame gashi sun Fara exam, abubuwa sun Mata yawa a Kai na Farko ga cewa har yanzu akwai aure tsakaninta da najeeb na biyu gashi ko kira babu balle

yasan wani hali take, wani irin hawaye ne ya zubo mata a ido tare da fad'in inda kabir ta aura daba haka ba , da tasan yanzu yana can yana nuna Mata so, tare da caring, kai auren wanda baka so babu dad'i ko kad'an

Tashi tayi ta goge hawayen dake idonta inda ta fita waje ta zauna a wajan wata bishiya tana danna wayarta wanda kabir ya bata, kiran iPhone, kaman daka sama taji an rufe Mata ido, da sauri ta Fara k'okarin cire hannun a fuskanta, k'okarin cire hannun tayi tana fad'in Zarah na gane ki AI.

Dariya Zarah tayi tare da fad'in taya akai kika gane?

Ibtisam murmushi tayi tace kamshin turarenki mana

Zarah tayi dariya tare da fad'in kai yau paper din yau yaso ya caza min kwakwalwa Wlh, abun babu dad'i

Ibtisam tace Kai ni gaba d'aya ma Sai dai ince Allah yasa dai inga dakyau, domin wlh Zarah kwata kwata ban San mai nake rubutawa ba, ko karatu bana iyayi daka na Fara sai inji baya shiga, wlh abubuwa sun min yawa

Zarah tace ibtisam Nima na lura da hakan, tunani ne ya miki yawa zaki ce, ba abubuwa ba

Ibtisam tace Hmmm

Zarah taci gaba da fad'in ibtisam ya kamata ki yarda ki kuma amince kiyi hakuri kina son mijinki ki, ki yadda ku zauna komai ya wu......

Ibtisam wani mugun kallo ta watsa ma Zarah, tare da fad'in dan Allah ya isa haka malama, ni na ce miki Ina sonshi?? Ko ni nace miki ina bukatar zama dashi?? Zarah yanda d'an uwanki baya bukatar zama dani Toh nima haka bana bukatar zama dashi, ki duba saki d'aya ya rage mana amma yace ya sakeni, inda badan ina haila ba, toh da sakin ya saku, wlh Zarah na tabbata tunda harya iya k'arasa igiyar dake tsakanin mu a lokacin da badan haila ba da yanzu babu auren, tun daga lokacin na tabbatar baya son zama dani, na kuma tabbatar da tsanar da yakemin da gaske ne...... Sai kuma ta fashe da kuka

ita dai Zarah ido ta bita dashi

Ibtisam cikin kuka taci gaba da fad'in najeeb ya cuceni ya amsa budurcina ba tare da saninshi ba, burin ko wace mace takai budurci d'akin mijinta yanda zata samu girma da mutunci a wajan miji, haka naita lallaba kaina tare da taimakon Allah, na ri'ke kaina Amma najeeb yayi sex dani ya rabani da wannan budurcin ba tare da saninshi ba, a lokacin inma ni ba virgin bace bai sani ba, tunda bai San inda kanshi yake ba, yamin ciki yace ba nasa bane, harta kamashi nayi yana...... Sai kuka mai cin rai

Zarah shafa mata baya take alaman tayi hakuri tayi shuru tabar kuka

Ibtisam tace wlh Zarah tun ranan da Nayi yunkurin zubar da cikin nan, amma bai zube ba, daka ranan Nayi nadama, kuma sai Allah ya jarabceni da son cikin, domin tunawa da Nayi inda ya fita da nasha magani Nayi kissan Kai wannan shine dalilin da yasa naji jikina ya mutu, sai gashi washe garin ranan ganin halin da najeeb ya shiga Wanda yasa Nayi mugun tsorata na rasa cikin Wlh duk yanda najeeb yakai da bacin rai Ina tunanin Bai kaini ba, nasan dole yayi zargin nina zubar domin a jiya nayi k'okarin in zubar abun baiyi ba, sai gashi washe gari ya zube.....

Dan shuru tayi tana zubar da hawaye Mai zafi, sannan taci gaba da fad'in, inda kowa zai fad'i sanadin zubar da cikin zai gane cewa najeeb ne sila, tunda inda baisha alcohol ba, yaje ya saka kwalba shigan mishi ciki ba aida banji tsoro ba har cikin ya zube......

Zuwan kubra ne yasa ibtisam yin shuru da maganan da takeyi wanda yasa tayi saurin goge hawayen da takeyi.

Kubra zama tayi kusa dasu tana fad'in na shiga uku yau, kai ku tayani murna Allah ya soni da kunji labarin na mutu

Zarah tace maiya faru dake??

Tace Hmmm Kedai Bari......  Yau na had'u da dan iskan daya so d'aukan rayuwa ta, Kai Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, sai ta saki kuka tana fad'in yau na tsallake Rijiya da baya, ban taba jin ance yau anyi Tsafi da karuwa ba sai dai inji ance anyi Tsafi da kamilan mace, Ashe yanzu duniya ta canza da kowa ma yi akeyi

Sex yace zaiyi dani, na amince mukai na Farko ya shiga toilet saina dauki wayarsa domin tayi min kyau saiga sa'ko ana fad'in idan kayi sex din Farko da ita a......  Daka nan sa'kon ya datse, nan na bud'e sa'kon naci gaba da karantawa..... A na biyun saika saka Mata tsutsa domin dodon mu ya nuna yarinyar tana da baiwa sosai, yanzu haka inkun gama na biyun tsutsan ya fita nan take ka korata tun kafin ta mutu domin awa biyu zatayi indai tsutsar ya shigeta........ Saita fashe da kuka tana fad'in Wlh ban gama karantawa ba na saki wayar tare da d'aukan jakata na gudu, ina hanya sai kirana yake mutumin daka karshe kashe wayan Nayi.....

Wlh ban taba jin tsoran Allah ba irin yanda naji tsoran in had'u dashi yau inya d'auki rayuwa ta, wlh gaba d'aya tsoran Allah ya kamani, in Naje Mai zance mishi??

Na farko nice na kai kaina da kaina, naje anyi zina dani, na mutu ba tare dana Tuba ba, wayyo Allah na na shiga uku.......  Kuka take sosai tana fad'in Allah na tuba, wlh yau Nayi nadaman abunda nake aikatawa lallai duniya Abun tsoro ne, gaba d'aya har yanzu wlh a tsorace nake, gashi na Farko da yayi babu condom ni yanzu tsorana kar ace ya sakamin tsutsar tun a na

farkon ba tare dana Sani ba, ko kuma ya samin wata cutar tunda Dan mafia ne.....

Ibtisam gaba d'aya jikinta har rawa yake saboda tsoro tare da tausayin kubra din

Zarah kam tace kubra tunda yanzu kin gane gaskiya, sai kiyi ta neman gafaran Allah tare dayin istigfari Allah zai yafe miki, domin Allah mai gafara ne ga bayinsa, Indai har mutum ya nemi gafara wajan Allah toh Allah zai yafe masa

Kubra tace zarah ina jin tsoran kar in mutu, wlh ji nake kaman ya samun tsutsan tun sex din Farko da mukayi, wlh Ina jin tsoran in mutu na shiga uku kuka take Sosai mai ban tausayi kallo d'aya zaka mata ka gane tana cikin firgici tare da tsoro

Ibtisam tace ki daina wannan kukan kubra, mutuwa hutu ce, karki manta duk Mai rai Mamaci ne, sannan Koba yanzu ba dole akwai ranan da zamu mutu, ga Allah muke kuma gareshi zamu koma, babu wani abun tsoro a cikin mutuwa, domin mutum zai koma wajan mahaliccin shi.....

Kubra cikin kuka tace nasan haka, amma ni ban aikata abunda zanso in had'u da ubangina ba.....

Ibtisam tace kar kice haka Allah cikin SURATUL AN'AM.....

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya halitta sammai da k'asa kuma ya Sanya duffai da haske, sa'an nan  kuma wad'anda suka kafirta da ubangijinsu suke karkacewa. SURATUL AN'AM Aya ta (1)

Shi ne wanda ya halitta ku daga laka, sa'an nan kuma ya yanka ajali, Alhali wani ajali ambatacce yana wurinsa, sa'an nan kuma ku kuna yin shakka. SURATUL AN'AM Aya ta (2)

Kuma shine Allah a cikin sammai, kuma a cikin k'asa, yana sanin asirinku da bayyanenku, kuma yana sanin abin da kuke yi na tsirfa. SURATUL AN'AM Aya ta (3)

Kubra duk abunda kikeyi Allah yana kallonki, na tabbata Allah yana sonki da rahma shine ya had'aki da wannan mutumin domin ki tuba, wlh kubra Allah yana son bayinsa, ki duba irin girman zunubin da muke aikatawa amma idan muka kirasa saiya amsa, idan muka ro'kesa gafara saiya yafe mana.....

Kubra rungume ibtisam tayi tana kuka, tare da fad'in hakane ibtisam Wlh na yarda Allah yana sona shi yasa ya ganar dani da sauri, wlh ko yanzu Allah ya d'auki rayuwa na tuba da duk abunda na aikata, kuma Wlh tuban gaskiya Nayi, in kuma inada rayuwa gaba, zan kasance mai bauta ma ubangijina tare dayin duk abunda yayi umarni inyi

Ibtisam tace Alhmdlh tare da fad'in

Wanda aka  juyar dashi daga gare shi, a wannan Ranar, toh Lalle ne (Allah ) Ya yi masa rahama. Kuma wannan ne tsira bayyananniya. 16 SURATUL AN'AM

Idan Allah ya shafe ka da wata cuta, to babu Mai kuranyewa gare ta, face shi, kuma Idan ya shafe ka da wani Alheri, toh shine, a kan Kome, mai ikon yi . 17 SURATUL AN'AM

Kuma shi ne tankwasa a kan bayinsa, kuma shine mai hikima, masani. 18 SURATUL AN'AM

Toh Kinga ya Allah shine mai shiriya da bayinsa, Kinga da Farko kin fad'a halaka, amma yanzu Allah ya ganar dake

Zarah tace hakane, kubra ki k'ara godema Allah, idan kika duba duniya ba komai bane, babu jin dad'i a duniya, cikakkiyar ni'ima tana Aljanna

Kubra tace hakane, amma sai Ina jin tsoran kaman Allah bazai yafe min ba, ki duba nice bin maza lesbians duka Inayi......

Ibtisam tace karki k'ara fad'in haka ki duba girman laifin da shaidan yayi ma ubangiji, idan kika duba SURATUL A'araf....

Lalle ne hakika mun halitta ku, sa'an nan kuma mun suranta kuyi sujada ga Adam.  Sai suka yi sujada face Iblis bai kasance daga masu yin sujadar ba. Aya ta 11 suratul A'araf

Ki duba irin laifin da Iblis yayi wanda Allah ya bashi umarni ya'ki bi, domin yana ganin shine mafifici domin an halicceshi da wuta, shi kuma Adam an halicceshi da laka

Kinga dai irin girman kan shaidan wanda yayi ma Allah amma daya nemi alfarma sai Allah yayi mishi inda yace ma Allah....

Yace kayi mini jinkiri zuwa ga Ranar da ake tayar da su. Suratul A'araf Aya ta 14

Allah yace lalle ne,  kana daga wadanda aka yi wa jinkiri . Suratul a'araf Aya ta 15

Bayan Allah yayi masa jinkiri sai shedan yace ....

Yace to Ina Mai rantsuwa da halakarwar da kayi mini Lalle ne ina zaune musu tafarkinka madaidaici. Suratul A'araf Aya 16

Sa'an nan kuma, hakika Ina je musu daga gaba garesu, kuma daga baya gare su, kuma daga barin jihohin damansu da barin jihohin hagunsu: kuma ba za ka sami mafi yawansu masu godiya ba. Suratul A'araf aya 17

Kinji irin abunda Iblis yayi alwashin batar da al'uma inda Allah yake ce Mai...

Yace : ka fita daga gareta kana abin zargi korarre. Lalle ne wanda ya bika daga gare su, hakika za ni cika jahannama daga Gare ku, gaba d'aya. Suratul A'araf Aya ta 18

Kuka ibtisam ta saki tare da fad'in kinci irin laifin da Iblis ya aikata wanda inda zaiyi sujada ga Annabi Adam lallai Allah zai yafe masa

Toh haka Muma Idan mukai laifi kuma muka ro'ki gafara lallai Allah zai yafe mana......

Kuka yaci karfinta sannan taci gaba da fad'in wlh duk Wanda yabi turban shaidan lallai alkawarin Allah na jiransa, Indai harya mutu bai tuba ba, kubra da yawa yanzu idan mace bata irin rayuwar Banza kallonta ake bata Waye ba, wacce take iskanci ita ake ma kallon wacce ta Waye, Innalillahi'wa inna ilaihirajiun,

Wlh ya kamata muji tsoran Allah, mu tashi daga turban shaidan, babu Waye wa irin mace ta suturta jikinta sannan ta kame kanta, wannan itace Waye wa, bawai fitar da tsiraici ba, da rayuwar Banza ba, da yawa mutane sun amsa kiran shaidan wanda yayi nasara a kansu, sai yasa a kullum ake son bawa Ya nemi tsari daga tsaida na'a nanne

Kubra tace lallai yau na gane rayuwa na kuma k'ara yarda, duk abokin da bazai fad'a maka abunda Allah yace ba, tabbas ba Aboki bane, duk abokin da zai dinga kaika hanyar halaka ka guji wannan abokin, ibtisam wlh Nayi nadaman sanin mutane da yawa a rayuwa ta, wanda sune suka k'ara Sani cikin wannan banzar hanyar, wlh babu rayuwa Mai dad'i kaman bin abunda Allah yace, sannan Kak'i abunda yayi hani dashi .... Sannan yau kawai na gane babu mutunci ga mace face gidan aurenta, domin da yawa abunda yake cutan mu sai muce sai mun gama karatu za muyi aure, muna mantawa aure baya hana komai, yanzu na tabbata inda inada aure da yawa bazanyi wani abu ba, koda kuwa Ina son inyi, saboda koda banji tsoran Allah ba zan dinga jin tsoran kar wannan mijin nawa ya ganni ko a Kai mishi labari, amma da yake banda aure yin Abu nake iya son rai na, ban damu da kowa ba, tunda iyayena ba a nan suke ba.....

Ibtisam tace hakane, amma rashin aure bashi bane kesa mata yin iskanci a jami'a ba, abun tsoran Allah ne kawai, ki duba zarah ai gata bata da aure, zan iya cewa bata kula samari ma, Kinga ta kame kanta, akwai ma ire irenta Wanda suka kame kansu basa irin wannan rayuwar, saboda sun ri'ke addini kuma suna tsoran Allah, dan Sun San komai suka aikata in wani Bai gansu ba, toh Allah ya gansu, kuma shine mai sakayya, mai hukunta bawa dai dai da abunda ya aikata

Kubra tace hakane, mudai munbi rudin duniya, amma yanzu Alhmdlh Allah ya ganar dani, kuma indai har inada rai ban mutu ba, zan zama cikakkiyar musulma Mai bauta ma Allah, tare da kame kaina sannan inna samu miji inyi aure duk da nasan kona samu mijin in yaji ba budurwa bace ni, zansha wulakanci amma zanyi hakuri in jure, dama duk Wanda ya zabi hanyar sabon

Allah zaiga ba dai dai ba a rayuwa

Ibtisam tace ku tashi mu shiga ciki

Tashi sukayi suka shiga ciki, inda ibtisam tace kubra ta kunna wayarta

Kubra tace wlh Ina jin tsoro Karya kira

Ibtisam tace karki damu ki kunna

Kunna wayar tayi Aiko tana kunnawa saiga kiran mutumin nan ya shigo tace kin gani koh??

Amsan wayar ibtisam tayi tare da dannawa tasa a speaker

Mutumin yace hello kubra

Ibtisam tayi mata alama da tayi magana

Kubra dakyar tace inaji.....

Yace har yanzu baki mutu ba.....

Ibtisam ta fusge wayar tare da fad'in bata mutu ba, kaine zaka mutu insha Allah.....

Kit wayar ta mutu alaman ya kashe wayar

Kubra kam babu abunda take sai kuka tare da fad'in Kun gani koh, kunji abunda yace koh??
Na shiga uku

Ibtisam tace miye haka kubra??  Bayan d'azu kika ce koda kin.....

Tun Kafin ibtisam ta k'arasa kubra tace hakane, nan ta Fara addu'a cikin ranta, da sauri ta bud'e data tare da shiga play store tayi downloading app na complete qur'an audio, nan ta saka ta Fara ji, ikon Allah uhm lallai babu wani sarki face Allah, shine sarki kuma Mai jin kai.

Allahu Akbar Allah mai rahma mai gafara ga bayinsa wanda suka tuba, mutum yayi ma Allah babban laifi sannan Idan ya nemi gafara Allah ya yafe masa....

Mai yasa mu muke ri'ke da y'an uwanmu musulmai??  Ya kamata Muma mu dinga yafiya, idan aka mana abu, idan ka yafe kaima sai Allah ya yafe maka

Kubra jin karatun al'qur'ani yasa gaba d'aya taji nutsuwa a tare da ita, duk wani firgici da takeji sai taji duk ta daina, ga wani tsoran Allah da taji yana k'ara shiganta, lallai maganin ko wace

cuta da nasiba tana cikin al'qur'ani Mai girma

Kubra haka ta zauna a dakin su ibtisam har dare yayi inda tace itafa a nan zata dinga kwana, domin a d'akinsu babu na Allah ko wacce tayi nisa, tare da fad'in Tana zargin d'ayan ma ta shiga cult

Koda su Aisha suka shigo d'akin suka ji kubra ana jin karatun al'qur'ani, abun ya basu mamaki, hauwa kasa hakuri tayi tace yau duk yanda akayi Kinji wa'azi a wani wajan wanda ya ratsaki kikai tuban mazuru....

Dariya Aisha ta saki tare da kallon kubra tace Nima fah Abun yaban mamaki, bandai fad'a bane kawai, wai kubra yau kodai kin had'u da wani sabon guy USTAZ ne yayi miki wa'azi

Kubra tace uhm, ban had'u da USTAZ ba sai dai na had'u da Wanda yayi niyan zama ajalina nan ta basu labari

Dariya suka saki tara da fad'in Wlh wannan k'arya ne

Kubra jin haka tayi banza dasu tare dayi musu fatan shiriya domin ita yanzu Allah ya ganar da ita gaskiya kuma ta gane

AISHA ta kalli Zarah tace nidai dan uwanki nake so, inda zai aureni dana daina harkan banzan nan.....

Ibtisam jin wani abu tayi ya tsaya mata a wuya da taji abunda Aisha ke fad'i........

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA

NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

AISHA taci gaba da fad'in Wlh zarah inda yayanki zai yarda ya aureni..... Hmmm da naji dad'in rayuwa, ni aida na more da nafi ko wace mace Sa'a.....

Hauwa ta Katseta da fad'in nidai Ina son ganin wannan guy din da kike ta wasa wa haka Wlh

Aisha tace uhm, Aini tsoran ki ganshi ma nake wlh, baki ga yanda ya had'u ba

Hauwa tace yakai zarah kyau??

Tsaki Aisha taja, tace ina itafa Zarah ba'ka ce, wannan sak Balarabe, baki ji zarah tace mamansu ya d'auko ba, Kai Wlh ya had'u namiji iya namiji, Kinga Wlh zaiyi kwazo.....

Dariya suka saki tare da shewa

Ibtisam gaba d'aya ji tayi ranta na baci, jin bazata iya saurar ansu ba yasa ta tashi tayi waje abunta, koda ta fita tsaki taja tare da fad'in aikin Banza dana hofi, waima NAJEEB suke wani kuzantawa, tsaki taja tare da fad'in inda Sun San halinshi da basu bata lokacin suba, Wlh, gaba d'aya ranta taji babu dad'i.

Gaba tayi tana tafiya, ranta gaba d'aya a jagule yake

mota ce ta tsaya a gabanta, wanda hasken motar ya kashe mata ido, tsaki taja tare da fad'in duba yanda suke wani haska mutum saboda iskanci

Har zata gota wajan motar taji muryan Dr jibril yana fad'in am so sorry plz, na kashe miki ido, sai Ina haka??

Ibtisam tsayawa tayi cak tare da fad'in ina wuni sir

Yace lafiya, tare da kallonta lokaci d'aya kuma ya fito daka cikin motar ya nufi inda take

Murmushi ya sakar mata tare da fad'in Amina dare yayi ina zaki??

Tace sir na fito insha iska ne

Yace Ok, ya exam din??

Tace Alhmdlh

Yace Bari in gudu, so Kema ki koma ciki, domin bai kamata kina yawo ke d'aya yanzu ba, domin lokaci ne da yara marasa ji ke zanyar fita

Ibtisam tace toh tare da fad'in saida safe

Yace OK motarshi ya nufa tare da barin skul din

Itama hanyar komawa tayi, domin gaskiya ya fad'a mata, domin taga irin motocin dake shigowa suna d'iban y'an Mata, ga kuma y'an Mata sai fita ake, Allah dai ya kyauta ya kuma shirya....

Ta kusa zuwa kofar d'akinsu ta hango zarah Tana tawowa, tsayawa tayi har Zarah ta k'araso inda take

Ibtisam tace sai Ina??

Zarah tace ke nazo nema, ina kika je??? Kodai duk kishin najeeb dinne yasa kika fita

Tsaki taja tare da fad'in Allah ya kiyaye akan mai zanyi kishin shi. Wlh kina bani haushi Idan kina fad'in haka, saifa kana son mutum kake kishin shi, in baka son mutum kishin Mai zakayi nashi??

Zarah tace toh mai yasa kika fita sanda ake maganan najeeb??

Ibtisam shuru tayi kaman tana tunanin abunda zata ce, can tace saboda haka nayi ra'ayi, keda kanki kin San bana son yayanki Mai zanyi dashi? Kinga dan Allah ki barni haka inji da abunda ke damuna na exam d'ina, gashi gobe zan Gama paper amma gaba d'aya na kasa zama inyi karatu nidai wannan semester din gaba d'aya sai a hankali Wlh

Zarah tace ai dole, tunda kin d'auki Abu kinsa ma ranki, ibtisam karki ce zanyi miki wannan maganan dan najeeb yayana ne, karki manta Kema y'ar uwata ce, sannan kuma abokiyar shawarata, Nasan a baya bakya son NAJEEB, amma a yanzu na tabbata kina sonshi, domin kuwa a da yanda kike yawan nuna tsananshi k'arara a ranki yanzu ba haka bane, gaba d'aya tsanar da kike Mai ya ragu, kibar yaudaran kanki, ki amshi mijinki hannu bibbiyu......

ibtisam wani harara ta sakar ma Zarah tare da fad'in baki da hankali sannan tayi gaba cikin fushi tana fad'in akan me Zata ce tana son NAJEEB, ai koda zanso mutum bazan so wanda ya tsaneni ba, mutumin da baya so na shine zanso?? Allah ya kyauta, mai zanyi dashi, mutumin

da yake zina, tare dashan giya wanda baya tsoran Allah, aini har abada bazan taba sonshi ba, yaje can ya zauna da matanshi Wanda ya saba dasu, domin zama da irinshi wata rana saiya kwaso ma mutum cuta ya manna Mai, tunda shi neman Mata yasa gaba, d'aki ta shiga, tana shiga daga su Aisha Anata surutu da HAUWA, ko kallonsu batayi ba, domin gaba d'aya ji tayi haushi suke bata, nufa gadonta tayi wanda kubra ke kwance tana jin karatu bacci ya d'auketa, kashe karatun tayi domin su Aisha Nata surutu ga karatu, itama kwanciya tayi a kusa da kubra, amma gaba d'aya ta kasa bacci, har yau abunda najeeb yayi ya tsaya mata a rai yanda ta kamashi da Najwa suna sex, wani hawaye Mai zafi taji yana zubar mata, lallai najeeb ba mijin zama bane, har yau abun ya tsaya mata a rai ta kasa Manta abun kuma wani abun mamaki ta kasa fad'ama kowa, daga tazo fad'a saita fasa, ta rasa dalili, ita dai ranta yana bata ta rufa Mai asiri.....

Hawaye take da yake ba kuka bane, kuma akwai huta ga k'aran fanka yasa su Aisha basu San mai takeyi ba, balle su Fara mata tambaya ko lafiya

Ido ta lumshe tana ganin yanda najeeb din ke fucking din Najwa, da sauri ta bud'e ido tare da tashi ta zauna tana sauke wani nishi, sama sama, lokaci d'aya kuma ta fita taje ta dauraye fuskanta, inda ta hango zarah Tana waya

Bayan ta dauraye fuskan Nata, ciki ta koma inda tahau gado ta kwanta, still tunanin nedai ya kuma dawo mata, duk yanda takai danta cire Abun a rai ta kasa gaba d'aya tunanin abun ne a ranta

Haka taita juyi akan gadon har zarah ta shigo d'akin Itama ta kwanta, ibtisam ta kasa bacci har su Aisha masu fira suma sukai bacci

Washe gari ibtisam idonta duk ya kumbura ga ciwon kai, domin batai bacci ba, ga exam 8 haka ta shirya ta nufi exam, Bayan sun fito daga exam dinne ta dawo dak'i inda ta samu kubra na zaune ta manne waje d'aya alaman zazzabi ke damunta

Ibtisam tace kubra bakya jin dad'i ne??

Kubra tace eh wlh fever ke damuna Sosai, plz ki bani paracetamol insha, ko zanji dama dama

Ibtisam tace Kai Wlh banda paracetamol, amma inaga ki tashi muje hspt sai a dubaki, a baki magani, Kinga is very risk kisha magani baki San maike damunki ba

Kubra tace hakane, bari muje, tashi kubra tayi ta d'auki babban hijab tasa suka fita ita da ibtisam, inda sukai cikin Shika domin taga Dr

Bayan taga Dr inda aka bata gwaji inda aka ga Malaria ne, nan aka rubuta Mata magani, suka biyo ta wajan emergency, inda suna tsaye domin wata mota ta wuce, aka faka wata mota kusa dasu, nan aka bud'e wani matashi ne wanda kallo d'aya zaka mishi kace lafiyanshi kalau, domin

ko motsi bayayi amma sai wanda suka kawo shi sukace bazai iya tafiya ba, nan aka d'auko Keken guragu domin a sashi, nurse din na tabashi tace ai ya rasu......

Kubra wani irin ihu tasa yanda kuka san ta san yaron, kuka take tana fad'in ibtisam kalla kiga, wlh kaman kice ya tashi, kalla kiga ikon Allah Innalillahi'wa inna ilaihirajiun, wayyo kai Allah yaji k'anka

Nan y'an uwan yaron suka bita da ido, domin ganin yanda ta nuna damuwa akan dan uwan nasu

Nan ibtisam ta jata sukai gaba

Kubra na hawaye tana fad'in ibtisam wannan kukan Inayi ne tare da tausaya ma kaina, wlh ibtisam tunani Nayi inda nice na mutu, mai zance ma Allah?? Gaba d'aya na bata rayuwa ta, na bijire ma Abun da ubangiji yace Ayi, nabi hudubar shaidan, amma yanzu na gode Allah daya ganar dani tun lokaci bai k'ure Ba, wlh gaba d'aya komai na duniya ya fitar min a kai, ina matukar jin tsoran in aikata Sabo yanzu, lallai ibtisam idan kana son ka k'ara jin tsoran Allah imani ya Kama ka kazo asibti ziyara, na tabbata inda mun shiga accident and emergency da munga abubuwa wanda tayu wani in muka gani bazamu iya bacci ba, saboda tausayi, ibtisam kalla wannan saurayin, jikinshi fresh kaman bai mutu ba, kaman kice Mai ya tashi, ya kuma tashi din, lallai duniya ba komai bace

Ibtisam tace hakane nima mutuwar shi ta tsaya min a rai tasa gaba d'aya jikina yayi sanyi..... Allah yaji k'anshi tare da sauran musulmai

Kubra ta amsa da Ameen, tare da fad'in Wlh ibtisam ke Kinji dad'i kina da aure, rayuwarki Abun sha'awa, baki da wani fargaba, amma mu gashi babu aure ga sabon Allah, gashi karatun bama bashi muhimmanci tunda yawon mu kawai muke, in mun dawo mubi lecturer su kwanta damu, dan karsu fadar damu, kai Wlh babu komai cikin raina sai tarin dana sani, gobe zan koma Gida tunda na Gama paper, ina son koda na koma Kafin hutu ya Kare zamu dinga waya ina tambayarki abunda ya shige min duhu

Ibtisam tace karki damu kubra, insha Allah, duk sanda kike da tambaya ki kirani kawai

Nan sukai gaba, inda suka koma cikin skul

Koda suka shiga d'akinsu a kwance suka tarar da zarah

Ganin Sun shigo yasa Zarah fad'in Ina kukayi

Ibtisam tace hspt na raka kubra ganin Dr, ya paper din??

Zarah tace hmm, Alhmdlh, tare da kallon kubra tace bakya jin dad'i ne? Ko duk maganan

mutumin nan ne?? Kubra tace a'a kawai zazzabi naji Inayi

Zarah tace Allah ya sawake

Washe gari duka suka watse sukai gida, Zarah taso ibtisam ta bita suyi abuja amma ta'ki, dole ta hakura ta tafi abuja ibtisam tayi Kano

Ibtisam ta isa Gida wajan 1 Tana shiga ta iske Ummi bata nan sai granny dake sallah, Dan haka itama alwala taje tayi inda ta Fara sallah

Bayan ta idar, ta kalli Granny dake zaune tace ina ummi??

Granny tace ta tafi anguwa, ya naga kin dawo, ko baki da lafiya ne? Naga duk kin rame

Ibtisam tace Hmmm granny ba dole ba, exam babu dad'i Wlh, munyi hutu ne sai yasa na dawo

Granny tace auwo tare da gatsan goranta tana ci tana gurus gurus

Ibtisam tace wai ba zaki daina cin wannan goran ba?? An fad'a miki yana da Illa, Amma kin k'i, wlh Granny ki shafa mana lafiya ki daina, kar kije kici abunda zaisa Musha wuya, gwara ki mutu cikin salama ba tare da wahalan jinya ba......

Granny tace dallah Rufamin baki, Al sai a kasheni, naga bakan mutum nake ba, in naci goro ya kashe ni, jiki na ko naki, haba yara sai iyayi komai ace yana da Illa shi kenan mutum kar yaji dad'in rayuwa, haba ni ban taba jin inda akace goro nada Illa ba

Ibtisam tace ai sai kiyi taci tunda an fad'a miki kin dage, nidai in ciwo ya kama ki bazanyi jinya ba, tunda na fad'a

Granny ta tsuke baki tare da fad'in shirmen banza da hofi, dama wake bukatar ki? Al na tabbata babu abun arzikin da zaki iya, Aini da kiyi jinyata gwara in zauna ni d'aya yafi min, wannan ba'kar zuciya taki, gashi mijin naki kin kasa hakuri dashi.....

Granny jin ibtisam tayi shuru yasa ta kalleta, ganinta tayi tana hawaye....

Granny tace miye haka kuma?? Haba takwarata maiya faru? cikin sigar rarrashi take tambayarta

Ibtisam kallon Granny tayi tare da fad'in yanzu Granny komai najeeb yayi ba'a ga laifinshi ba sai nawa???

Granny tace ba haka nake nufi ba, abunda nake nufi kin kasa hakuri dashi.....

Ibtisam tace taya zanyi hakuri dashi?? Granny karki manta ni mace ce, an d'aura min najeeb ba tare da sanina ba, infact ma ban taba tunanin zan aureshi ba, gaba d'aya nasa rai za muyi aure da kabir sai naji an d'aura da wani, yau najeeb Koba dan uwana bane shi, dole yanda naji babu dad'i hakan zanyi, anyi min wannan a matsayina na mace, wanda ya zama dole in hakura in zauna dashi, Wanda nasan igiyar auren shine keda ikon tsinkata, sannan shi namiji ne, Ance in za suyi adalci su Fara daga Biyu.....

Kinga Mata biyu akace ba d'aya ba, kinga yana da ikon k'ara auren wacce yake so, amma nifa?? Bani dashi, dole shi dinnan dai zan zauna mawa, ba wani ba, granny inda kin San zafin rabuwa da wanda kake so da ance Nayi hakuri, da yawa mutane basa gane wani abu, yau Indai Abu ba'a kansu yake ba, koya fad'a musu ba, toh basa gane irin zafin abun da kuma rad'adinsa

Nasan ni mace ce, kuma Aljanna ta tana k'asan kafar mijina, Nasan dole nayi masa biyayya, dole nayi masa abunda yayi umarni da inyi masa Indai bai saba ma sha'ria ba......

Duk Nasan wannan, toh amma shi najeeb din yana bin abunda ubangiji yace??

Baya bi, mutumin daya kauce ma mahaliccin shi taya wani zai bishi.....

Kuka ta saki mai cin rai sannan tace Granny, Koba alakan aure najeeb jinina ne, duk da tun Farko bama jituwa haka koda mukai aure babu wata magana Mai dad'i data taba shiga tsakanin mu, yau Koba najeeb dake jinina ba, ko wani naga yana shan giya Wlh zan tsaneshi, amma da yake najeeb akwai ala'kan jini sannan aure ya had'amu dole haka na hakura, kuma na tabbata inda najeeb ba jinina bane kuda kanku zaku ce saiya rabu dani, tun a lokacin da yayi min sharri yace wannan cikin ba nasa bane

Ya kamata inda kuna sona a lokacin da kun raba wannan auren, amma daga karshe sai kuka barni a wajansa, duk da ya nuna baya bukatar in zauna a tafi dani amma sai lokacin kika ce dole in zauna, haka kuka tafi kuka barni dashi

Granny Kun San irin abunda naji?? Kun san irin kuncin da naji?? Duk baku Sani ba, ku burinku in zauna dole a gidan miji, tunda ni mace ce banda wani zabi face inyi hakuri da duk irin abunda miji zaimin, ku matsalanku kar ace y'arku ta zama bazawara koh?? Koba shi bane matsalan??

Granny da yawa a k'asar Hausa Anfi samun irin wannan matsalan, kiga namiji shine dukan mace, cin zarafin ta, ya hanata haiyuwa, saboda baya bukata, ya tauye Mata hakkinta, etc

Kinga duk irin wannan matsalolin ba zasu gyaru ba, har sai iyaye sun daina jin tsoran kar y'ay'ansu su dawo gida su Zame musu nauyi ko kuma kar ace suna da bazawara

Granny shifa aure sunna ne, ba farillah bane, sannan shi aure daka ranan da mace tayi komai kikayi lada ake baki, bauta ne

Ni a nawa ganin Nasan duk abunda akace bauta ne sai an jure, amma da mace ta zauna miji ya dinga kuntata Mata, ita kuma tana masa abunda zaiji baya so, gwara a raba auren, domin anyi aure Dan samun lada sannan yakai mutum da Aljanna, amma babu farin ciki kuna kai kanku hanyar halaka, ku jefa kanku wuta, Indai irin wannan ne miye amfanin auren?? Kinga babu shi

Namiji zai bugi mace, ya mata mummunan duka, inta dawo gida sai a bata hakuri ace ta koma aure d'an hakuri ne shi dama bauta sai an jure, aita bata hakuri ana fad'in kiyi ta hakuri wata rana sai labari.....

Toh Kunga tun daga nan kun ba mijin daman ci gaba da dukanta kenan, domin yaga yayi na Farko ba'a d'auki mataki ba, an k'ara tura mishi ita, kinga zaiga baki da wani gata, wani namijin ma sai yaga kaman Turaki akeyi wajansa, kinga ba'a Fata a haka sai kiji ana fad'in ya kasheta wata rana, ko ita ta kashe shi, domin ita zuciya bata da k'ashi. Bawai Ina nufin Idan namiji ya bugi mace a raba auren bane a'a, but ya kamata a nemo shi aji dalili da zai bugeta, in Abun ta Kama a nemo har waliyansa ayi magana akan Karya k'ara dukanta, in Abun bazaiyi ba ko babu Mai fad'a mishi yaji zaku iya zuwa kotu, alkali ya bashi takarda yayi signing akan inya K'ara dukanki akwai hukunci akansa.

Indai aka d'auki wannan matakin bazai k'ara ba, shine ake kira da kwatan y'anci

Idan ana haka za'a rage irin abubuwan dake faruwa a gidajan aure musamman......

Granny ta dakatar da ita da fad'in ya isa haka ibtisam, na fahimta, amma ina son ki sani, shi aure dace ne, kuma ko wace mace tana da nata jarabawan, Mai hakuri yana tare da Allah, eh abunda kika fad'a gaskiya ne, yana dakyau a kwatan ma mutum yancinshi , amma ina son ki san wani abu guda d'aya akan najeeb, sannan ina son ki sama ranki wani abu, ki d'auka duk abunda yayi miki yayi miki ne cikin rashin sani, ba tare da yasan yayi ba...... Ibtisam na k'okarin magana Granny ta Katseta da fad'in kiyi shuru in Gama magana sai kiyi

Granny taci gaba da fad'in yanzu kinga NAJEEB yana Abu ne ba tare da sanin ilimin addini ba, kinga baiyi karatun addini ba, duk wasu abu da zaki ga yanayi Ina son ki d'auka cewa bai sani bane, abunda muke k'okarin yanzu mu d'aura shi a hanya kenan, muna son yasan addini ta yanda zai bauta ma mahaliccin sa, duk wannan Abun laifin mahaifinshi ne daya fifita boko akan karatun addini, wanda shi yake d'auka yama d'ansa gata ne, bai san ba gata ya masa ba, domin inda yana sonsa yana son nuna mishi gata shine ya koya Mai ilimin addini, wanda shine zai kaishi ga tsira ranan lahira,.

Granny kamo hannun ibtisam tayi tana fad'in dan Allah takwara ta, Ina son ki zauna da najeeb, ki ceto Dan uwanki daga fad'awa halaka, ina son ki zauna dashi matsayin mata Mai biyayya, domin ke y'ar uwarsa ce, Kece zaki fi kowa sanin darajansa, Koba dangantakar aure akwai na jini, ina son ki duba girman Allah kiyi hakuri ki koma wajan mijinki..........

Ibtisam kuka ya kubce mata sosai gaba d'aya ta kasa magana, ta rasa mai yasa Granny take

ganin kaman itace take gudun zama dashi, shine fah yace ya saketa, Bayan haka kuma ance Mai sakin baiyi ba, amma ya tafi ba tare da yace komai ba, sannan tunda ya tafi bai kuma waiwayo waba, amma granny tazo tana d'aura mata laifi........

Read and leave it, dnt share to anyone*IDAN KIKA KARANTA BAKI BIYA BA INA BINKI BASHI, KUMA NAUYI NE A KANKI*

*WACCE TAKE SON BIYA ZATA TURA 200 TA ACCOUNT NUMBËR DINNAN*

3138831065 Firstbank Maryam Alhassan

*SAI A TURO SHAIDAN BIYA TANAN 08060860886 IDAN KUMA KATI NE MTN SHIMA TA NUMBER DIN ZAKI TURA 200 NAIRA ONLY*

*KARKI MANTA KINYI ALKAWARI, BAZAKI FITAR MIN DA NOVEL BA, IDAN KIKA FITAR DASHI KEDA ALLAH, KUMA KINA D'AYA DAKA CIKIN MUNAFUKAI, DOMIN ALAMAN MUNAFUKI GUDA UKU NE, 1 IDAN ZAIYI MAGANA YAYI K'ARYA 2 IDAN AKA AMINCE MASA YAYI HA'INCI 3 IN YAYI ALKAWARI YA SABA, KIN DAI JI, KINCE KIN MIN ALKAWARI, IDAN KIKA SABA KIN ZAMA MUNAFUKA, KUMA WUTAR MUNAFUKI DABAN TAKE, IDAN KIKA FITAR KINMA KANKI*

Kaman granny tasan abunda ibtisam ke tunani, tace ibtisam zaki ga kaman bana goyan bayanki, ba haka bane, yanzu duniya ta canza, komai ya canza, idan mace batai hakuri gidan mijinta ba inta fita bata san wanda zata aura ba, kinga gwara tayi hakuri ta zauna da Wanda tasan halinsa, saita dinga kiyaye wa, amma yanzu in mace ta nemi saki , inhar mijinta ya saketa bata san wa zata fad'a mawa ba, sai yasa ake cewa hakuri shine gaba da komai, kuma Mai hakuri yana tare da Allah, wlh ibtisam ban taba ganin laifinki ba gaba d'aya na najeeb ne, domin ke aka cuta amma gashi ina rokanki akan kiyi hakuri wata rana insha Allah za kiyi dariya

Ibtisam nidai burina in ganku tare har abada, shine Fata na, indai kukai haka zan mutu cikin salama......

Da sauri ibtisam ta rungume Granny tana kuka tare da fad'in insha Allah bazaki mutu ba Granny

Granny tayi murmushi tare da fad'in ai mutuwa ta zama dole ibtisam, lokaci kawai ake jira, amma dole ce ko Ana so ko ba'a so

Ibtisam tace toh nidai Granny abar maganan mutuwar nan dan Wlh ba son jinta nake ba, gaba d'aya

Granny tace Indai kam baki Sonta saiki koma ma mijinki, yanda zaki sani farin ciki

Ibtisam tace Granny ni Kinga Wlh yunwa ma nake ji, Sosai mai kuka dafa ne Inci

Granny tace ja'ira wato canza firan zakiyi koh?? Yayi miki kyau ai

Ibtisam tashi tayi ta nufi kitchen inda ta dibo abinci domin taci, tana cikin ci sai ga Ummi ta shigo cikin d'akin tana fad'in ah Ashe y'an karanta an dawo

Ibtisam cikin fara'a da murna take fad'in eh Ummi tun dazu na dawo bakya nan

Ummi tace Mun fita da Maman fati ne, ya karatun an Gama jarabawan kenan?

Ibtisam tace eh mun gama zamu sha hutu Mai tsawo harna wata d'aya da sati Biyu

Ummi tace Kai Aiko zaku dad'e a gida Sosai Allah ya taimaka bari inje in watsa ruwa duk na kwaso rana, Ummi ciki tayi tabar ibtisam da Granny

*AMERICA*

najeeb ne zaune yana karanta al'qur'ani domin gaba d'aya yanzu ya iya had'a ba'ki, abun har mamaki yaba malamin yanda yayi saurin iyawa, gashi najeeb baya dad'ewa ya gane Abu, wanda yawanci tun a k'aramin shekaru mutum yake saurin haddace Abu haka, amma sai gashi Abun mamaki shi najeeb da girmansa yana haddace Abu da wuri

Malamin ne yazo inda najeeb yake yana fad'in gaskiya najeeb ka gode Allah, wlh komai naka Abun sha'awa babu wuya ka haddace Abu, nan da nan wlh kana da kwakwalwa sosai

Najeeb saida yakai karshen Aya sannan ya kalli malamin Bayan ya ajiye al'qur'ani yace malam ba komai bane yasa kaga Ina saurin haddacewa ba sai Dan Ina son in koya wanda Allah yaga zuciya ta, duk abunda nake da Wlh Ina aikatawa ne ba tare da sani na ba, sannan yanzu dana gane nake son in koya in iya dole in dage, aikina gaba d'aya na dau hutu dan in nemi ilimin

addini, inta Kama ma Wlh ajiye aikin zanyi, duk da nayi yunkurin yin hakan amma suka d'age akan bazan ajiye ba, inje inyi hutu, shine nace na d'auki hutun 5mnt

Malamin yace hakan ma yayi tunda gashi yanzu ko wata biyu bamu yiba amma harka iya abubuwa da dama, ko a haka ka tsaya aika gode Allah, domin wani wanda ya taso tun yana yaro yayi karatun ban tunanin zaiyi aiki dashi akan Kai yanda kake aiki dashi, yanzu nima tafiya ta Kama ni dole zan tafi saudiya, domin mahaifina baida lafiya, Kaga bazan zauna ba har inyi wata ukun da Nayi alkawari ko a haka na Barka Alhmdlh Nasan ka koya abubuwa da yawa

Amma idan naje naga yanayin jikin nasa inda hali zan dawo.....

Najeeb yace a'a karka damu, nida kaina zan biyo ka saudiya, zanje Nigeria insha Allah daga nan Zanzo harda iyayena domin su ganka, ku gaisa

Malamin yace haka yayi, tare dayi MA NAJEEB addu'an samun nasara a rayuwa

Najeeb Bayan ya koma gidansa gaba d'aya baya son zama shi d'aya sai yaji gidan yayi masa girma, kwanciya yayi akan kujeran falon inda ya lumshe ido, lallai sai yanzu yasan yana rayuwa, a da yana rayuwa ne amma kaman matacce, domin bai San yanda zai bauta ma Allah ba, gaba d'aya wannan canjin daya samu ya sameshi ne ta sanadin rayuwarshi da ibtisam ta shigo

Ya fara tunanin yasan mai yasa shan giya ya zama haramun da zina, lokacin da tace mishi duk manyan laifin da Allah ya hana kana aikatawa, tun daga ranan ya fara tunanin sanin Mai yasa ya zama laifi har yakai shi ga kiran malam, wanda gashi yanzu gaba d'aya rayuwarshi ta canza, sai dai abu d'aya da yake fatan shima ya canza

Lokaci d'aya ya tashi ya nufi bedroom d'inshi inda ya fad'a toilet yayi wanka ya fito daga shi sai boxer da singlet Kai tsaye kitchen ya nufa inda ya Tarar damai mishi aiki yace ta Kawo mai coffee, yana fad'in haka ya juya falon ya zauna yana danna wayarshi dake hannunsa

Bayan Mai aikin ta kawo mai coffee ta ajiye Mai akan center table har zata wuce najeeb yace ta tsaya tare da fad'in gobe zani Nigeria so zaki iya d'aukan hutu, but amma ki dinga zuwa kina duba gidan coz ban son in dawo inga datti ko k'ura

Ta amsa da OK sir

Najeeb d'aukan coffee din yayi inda ya fara sha.....

Washe gari kaman yanda yace hakan ko ta faru domin kuwa jirgin k'arfe 10 yabi inda ya tafi Nigeria Kai tsaye a abuja ya sauka inda aka turo mai driver yazo ya d'auko shi,.

Bayan sun k'arasa gida, Zarah da saurinta ta nufeshi tana fad'in Wlcm bros

Murmushi ya sakar mata tare da kallonta yace ya gida da skul?  Yana ganki a gida??

Tace lafiya bros munyi hutu ne

Yace OK

Nan suka shiga ciki abunda najeeb bai taba yiba yau yayi gaida iyayenshi cikin girmamawa, gaba d'aya daga Dad har Mum sunyi mamaki tare da kallon juna

Najeeb ya lura da hakan sai yayi murmushi tare da fad'in kai am so tired I need to rest hope d'aki na a gyare yake??

Mum tayi murmushi tare da fad'in eh my only son, a gyare yake, AI ban barin dakinka da datti, domin Nasan yaron nawa baya son kazanta, amma before ka huta Aida kaci abinci koh

Yace Mum bari in huta na gaji Sosai wlh, nayi missing food d'inki amma tunda kika ga na kasa ci, toh na gaji ne

Tace OK a huta dakyau

Yayi murmushi tare da shiga d'akin nashi wanda yana shiga ya fad'a gado ya kwanta sai bacci

Mum da Dad sukam zama sukayi inda Dad yake fad'in kinga yanda yake gaidamu cikin girmamawa, gaba d'aya harta magananshi ya canza kaman bashi ba

Mum tace Wlh kuwa abun ya bani mamaki, bari dai ya tashi muji ya akayi

Ibtisam ce zaune tana ta wanke underwear d'inta, a wajan fanfo din dake waje, a tsakar gidan

Granny ta fito tana fad'in in banda kazanta mutum saiya tara su wando da skirt da yawa Kafin ya wanke, ai wannan kazanta ne

Ibtisam tace kazanta?? Lallai Granny Wlh kina shiga sabga ta da yawa, d'ago wani pant d'inta tayi tare da nuna mata da tace ina kika ga alaman kazanta a nan??  Kuma pant d'in ga sunan gudu biyar ne duka amma kina wani kiramun kazanta, salan wani yaji kisa a d'auka haka nake

Granny tace toh aji mana, AI gaskiya na fad'a Inba Kazami ba, taya mutum zai dinga tara pant da yawa haka babu wanki, ko ni da nake tsohuwa bana irin haka saike yarinya karama saboda lalaci.

Ibtisam tashi tayi tana d'iban kayan domin ta gama zata toilet ta shanya tace Kedai kika sani, nidai banda lokacin wannan surutun dake inada abunyi da yawa

Granny tace ai kyace haka mana t.....  Wani irin K'ara ta saki tare da yin k'asa, da sauri ibtisam ta saki roban dake hannunta ta nufi Granny tana fad'in Granny lafiya kuwa? Maiya sameki tana tambayar Granny tana kuka

Ganin granny bata ko motsi yasa ta nufi d'akin ummi dake bacci da gudu tana fad'in ummi Ummi kizo mukai Granny asibti na shiga uku Granny ta fad'i k'asa

Ummi dake bacci sai taji kaman tana mafarki da sauri ta tashi amma sai taji ba mafarki bane domin dai dai lokacin ibtisam ta shigo d'akin Tana fad'in ummi Granny ta fad'i muna cikin magana Dan Allah mu kaita asibti ki kira abba

Da sauri Ummi ta tashi tare dasa hijab tana fad'in maiya faru da ita?? Kai tsaye waje suka nufa inda suka tarar har yanzu tana nan kwance a k'asa tana nishi sama sama

Nan Ummi tace maza su kamata su kaita asibiti, hakan ko sukayi ibtisam ta fita ta kira Mai adai daita sahu inda suka Kama Granny ita da Ummi sukai motar da ita, direct asibiti suka nufa da ita inda aka amsheta akai emergency da ita domin a duba lafiyarta

Ibtisam kuka take Sosai, domin a duniya Tana son Granny, ko kad'an bata son taga wani abu ya sameta

Ummi sai a sannan ta kira abba Inda ta fad'a mishi halin da ake ciki, ko minti 30 baiyi ba ya garzayo asibitin Kai tsaye inda ya Tarar dasu suna zaune ibtisam nata faman kuka

Abba yace maiya sameta??  Nan ibtisam ta Fara fad'a mishi Abba muna fira na tashi inje inyi shanya tasa ihu tare da faduwa

Abba yace Toh ya isa mana kibar wannan kukan Mai Dr yace ??

Ummi tace baice komai ba, har yanzu Dr bai fito ba

Nan Abba ya zauna suna jiran fitowan Dr din

Wayar abba ce tayi K'ara d'auka yayi yaga Dad ne Bayan sun gaisa Dad yake cema Abba d'anka ya dawo yau

Abba yace a Barka da fatan ya dawo lafiya

Dad yace lafiya

Abba yace gamu a asibiti Mama bata da lafiya

Nan Dad yace Subhanallah maiya sameta??

Abba yace gamu nan dai har yanzu Dr bai fito ba

Nan Dad yace bari yanzu mu kamo hanya

Abba yace kai yamma yayi fah

Dad yace ya zamuyi dole mu tawo

Nan Bayan sun kashe wayan Dad ya kalli Mum yace mama bata da lafiya yanzu zan kama hanyar Kano

Mum tace maike damunta?

Dad yace wlh ban sani ba, Tadai fad'i ne kuma ance Dr bai fito ba

Mum tace amma daka bari gobe saimu tafi gaba d'aya koh??

Yace a'a yau zani ku saiku tawo gobe

Nan Zarah tace zata bishi

Yace Toh kiyi sauri muje kin San ban son jira

Zarah tashi tayi da gudu taje ta zuba kayanta a akwati tare da abun bukata sannan ta fito suka Kama hanya ita da Dad, mum dai tace ita da najeeb gobe zasu tawo

Bayan fitan su Dad saiga najeeb nan ya fito ya tashi Daga bacci.

Mum tace harka tashi

Yace eh mum Ina Dad ya fita ne??

Tace ya tafi Kano yanzu

Yace yanzu da yamma haka? Lafiya kuwa??

Mum tace granny ce aka kwantar a asibiti, shine ya tafi shida Zarah Nima gobe zamu tafi

Yace Subhanallah maike damunta?? Kai ni bamma taba ji ance tana ciwo ba sai yau

Mum tace Wlh bata ciki ciwo ba, gashi wanda bai ciwo inya tashi yi bai iyaba

Najeeb yace Allah ya Sawake, nima da Ina nan Aida nabi Dad munje tare

Mum tace gobe saimu tafi da safe ai, kaci abinci ko saina zuba maka ne??

Dariya yayi tare da fad'in tunda y'ar autarki bata nan yau nine autan sai a zuba min din kawai

Mum tayi dariya tare da zuba mai, nan suka zauna suna ta fira Inda NAJEEB yace Mum yanzu nasan ina rayuwa wanda da gaba d'aya ba rayuwa nake ba

Mum tace kaman ya??..

Yace Nasan addini na, Mum da gaba d'aya Ina amsa sunan ni musulmi ne amma ban San miye addini ba, amma a yanzu Alhmdlh Nasan abubuwa da dama kuma ina kan koya

Mum cikin mamaki tace najeeb a Ina ka koya??..

Murmushi yayi tare da bata labarin abubuwan daya faru Bayan tafiyar shi

Mum wani hawaye ne ya zubo mata tare da tashi ta rungumeshi ta baya tana kuka tare da fad'in Alhmdlh Alhmdlh Alhmdlh yau nafi kowa murna yau Ina cike da farin ciki d'ana ya fara neman ilimin addini, najeeb Wlh baka ga yanda naji dad'i ba, abunda yake ranmu kenan akan muyi maka magana sai gashi kaida kanka ka Fara koya Wlh ji nake yau kamun anyi min kyauta Mafi girma a duniya

Najeeb yayi murmushi tare da fad'in Mum nima yanzu baki ji yanda nake jin dad'i ba, nasan miye rayuwa nasan yanda zan tafiyar da rayuwa domin samun tsira wanda da duk ban sani ba yanzu kam Alhmdlh

Mum tace najeeb Allah yayi maka albarka

Tashi yayi tare da kamo hannun Mum Ya ri'ke tare da fad'in mum plz ina son duk wani abu dana miki na rashin tarbiya ki yafe min, Dan Allah domin na gane da ba'a akan dai dai nake ba

Mum ta rungumo shi tare da fad'in na yafe maka duniya da lahira, Wlh najeeb komai kayi min ban taba ri'keka ba cos ni uwa ce sannan nasan duk wannan abunda kakeyi ina maka uzuri duba da irin kasar daka taso a cikinta

Wani irin hawaye ne ya zubo a fuskanshi wanda yayi sauri ya goge, lallai uwa uwace, shida kanshi yana jin kunyar abubuwan daya musu baya amma gashi yanzu tace bata rik'eshi ba,

Allah sarki rayuwa duk Wanda bai mutunta iyayenshi ba yayi Asara, kun dai ga irin abubuwan da najeeb yayi amma Mum tace bata ri'ke shi ba, waye Zaima wannan inba Uwar data haifeka ba

